# Tarihin Annabi
## Kammalalle

*na*

Alhaji Abubakar Imam, C.O.N., O.B.E.

Juzu'i na Daya, da na Biyu, da na Uku

# TARIHIN ANNABI

## KAMMALALLE

(Juzu'i na 'Daya, da na Biyu, da na Uku)

Na

**Alhaji Abubakar Imam, C.O.N., O.B.E.**

NNPC

NORTHERN NIGERIAN PUBLISHING COMPANY
ZARIA

Copyright © NNPC 1970

*First Published* 1957
*Reprinted* 1961, 1969, 1972, 1974, 1975, 1976

*Published by*
The Northern Nigerian Publishing Company Ltd.
P.O. Box 412
Zaria

*Printed by*
Gaskiya Corporation, Zaria

# ANNABI MUHAMMADU

## Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi

A cikin tarihin annabawa da dama, in ka karanta, za ka riƙa gamuwa da mu'ujiza iri kaza, da mu'ujiza iri kaza, da mu'ujiza iri kaza, waɗanda suka nuna a zamansu na duniya.

Amma in ka karanci tarihin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sai ka ga shi tun daga haihuwarsa har ɓakuwarsa, har yanzu ga abin da ya bari, mu'ujiza ce Allah ya saukar, don ta zama aya, wadda za ta ƙara tabbatar wa ɗan Adam, cewa Allah shi kaɗai ya ke, ba shi da abokin tarayya.

A juzu'i na biyu, na wannan tarihi, mun bar ku ga labarin yadda Annabi ya yi hijira, bisa ga umurnin Maɗaukakin Sarki Allah, ya taso daga Makƙa ya komo Madina.

Wannan tasowa ta Annabi, daga Makka zuwa Madina, ita a ke kira hijira. Daga wannan shekara ne a ke fara ƙidayar shekarun musulunci, ba daga haihuwar Annabi ba, kama ryadda Kirista ke yi. Bana wannan hijira ta Annabi tana da shekara 1374.

Kun karanta a juzu'i na biyu, yadda kafiran Makka na lokacin, su Abu Jahali, su ke ta fitinar Musulmi. Da yadda su ke da burin su zo su halaka su. Sabo da haka ne fa, a cikin watan Rajab, hijira na da shekara biyu, ya zaɓi mutum 12, ya sa su ƙarƙashin wani, wai shi Abdullah Ibn Jahshi, ya ce su je wani wuri da a ke kira Nahla, su riƙa dako domin kada abokan gaba su far wa Madina ba labari. Abin ƙaddara, suna isa Nahla, sai ga ayarin waɗansu fatake na Makka sun sauka bakin wata rijiya. Da su Abdullah suka bukaci ruwa, sai ayarin nan suka hana su. Daga nan sai faɗa ya tashi a tsakaninsu. Aka kashe mutum guda cikin ayarin na Makka, aka kama biyu. Suka komo Madina da su, wai ganima.

Wannan al'amari da su Abdullah suka aikata ya ɓata ran Annabi ainun ainun. Domin shi bai aike su yaƙi da kowa ba. Ya zargi Abdullah ƙwarai da aikata wannan aiki. Ya ƙi karɓar

ganimar, ya saki wadanda aka kamo. Ya sake su kuwa cikin daraja, da girmamawa. Kunji abin da ya auku a Madina.

To, me ya faru a Makka da jin wannan labari? Wannan ai ba sai mun gaya muku ba. Yaya lafiyar kura bare ta yi hauka? Da ma mutanen Makka suna can suna wasa takubba, suna damara, suna tara dangi, jira kawai su ke yi su sami dan dalilin da zai sa su auka wa Madina. To, ga dalilin ya samu !

Jarumawan Makka suka shiga fartar ƙasa, suna cewa, "Sai mun niƙe Madina, duk da abin da ke cikinta !" Wadansu mutanen Makka kuwa, da suka sami labarin abin da Annabi ya aikata ga Abdullah sai suka ga wannan al'amari dai ƙaddara ce, bai kamata sabo da ita a je yaƙi Madina ba. Suka ce sun tabbata idan mutanen Makka suka aika ga Annabi bidar diyyar wannan rai da aka kashe, zai bayar. Kada a je yaƙi. Da ji manyan maƙiyan Annabi sai suka riƙa cewa, wai wannan zance ne na matsorata su ba za su ji shi ba ! Shi ke nan, sai kafirawa suka yi dabur. Da ma ana jira ne. Suka yunƙuro daga Makka, da runduna ta barade mutum dubu, kowa na girgiza kansakali, yana yi wa kansa kirari, ni dan Wane jikan Wane ! Suka tinkaro Madina. Wannan shi a ke kira Yaƙin Badar. Ga su nan, sun nufo Madina da niyyar su zo wai su niƙe Annabi, su niƙe mabiyansa, su niƙe Madina ! Hasali dai wai su niƙe addinin musulunci dukansa, su huta !

## Sahabbai Sun Karda

Ɗa Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ji labari ga maƙiya nan tafe da niyyar halaka su, sai ya tara jama'arsa Muhajirina, da Ansarina, watau wadanda suka biyo shi daga Makka, da mutanen Madina wadanda suka karɓi musulunci. Duk sahabban nan na Annabi suka karɓa masa da kalmar yarda. Tsaya ma mu fassara muku kalamin da wani sahabi, Sa'adu binu Mu'azu, ya ba Annabi amsa sa shi. Ga abin da ya ce, "Haƙiƙa ya Rasulullahi, mun yi imani da kai. Mun gaskata ka ! Mun shaida abin nan da ka zo da shi gaskiya ne ! Mun ba ka alkawurammu ga wannan. Muna damfare da kai, masu saurare da aikatawa ga dukan abin da ka ce ! Ci gaba, ya Annabin Allah, ga abin da ka yi nufi, muna tare da kai Na rantse da Sarkin nan da ya aiko da da gaskiya, da za ka ce ka ja mu, mu fada bahar, da sai ka ga mun fada tare da kai,

ba mutum ɗaya a cikimmu wanda zai tsaya a baya ! Ba mu ƙi ba ka ja mu gobe mu gamu da abokan gabammu........ Ya Annabi Allah, ja mu mu je bisa ga albarkar Ubangiji".

Wannan amsa fa ta ƙara ba Annabi ƙarfi. Ya ba da oda, aka yi ɗamara, aka fita, aka nufi wani kwari da a ke kira Kwarin Badar, don a taryi abokan gaba. Rundunar Annabi duka duka ta mutane ne 313 kaɗai, da dawaki biyu da raƙuma saba'in. Galibinsu kuwa, ba gwanaye ba ne a fagen yaƙi, sai dai a fagen imani ga Maɗaukakin Sarki Allah.

## Annabi Ya Fita Biɗar Labari

Da suka sa uka,sai Annabi ya ɗauko Sayyidina Abubakar, suka rabu da sansani, suka milla suna sansanen labarin abokan gaba. A can suka gamu da wani tsoho. Suka tambaye shi yalla ko yana da labarin rundunar Muhammadu, kuma yalla ko yana da labarin rundunar mutanen Makka ? Tsohon nan ya ce, "Ina da shi, amma ba ni gaya muku, sai ku ku kun gaya mini daga inda ku ke". Sai Annabi ya ce, "A'a, kai dai fara gaya mana, sa'an nan mu mu gaya maka". Tsohon nan ya karɓa ya ce, ya sami labari, rundunar Makka sun taso rana kaza. Idan labarin da aka-gaya masa gaskiya ne, yau suna wur kaza ke nan. Ya cigaba da cewa, Muhammadu kuma da rundunarsa ya sami labari sun taso rana kaza. Idan labarin da aka gaya masa gaskiya ne, yau suna wuri kaza. Ya kuwa faɗ daidai inda su ke dukansu.

Sa'an nan ya dubi su Annabi, ya ce, "To, yanzu ku kuma sa ku gaya mini daga inda ke ku". Suka ce masa, "Mu mun fito daga Ma'ine !" Ba su tsaya wata magana ba kuma sai suka yi baya sukakoma ga jama'arsu. Suka bar tsoho yana cewa,"Sun fito daga Ma'i, wace Ma'i su ke nufi, ko Ma'in Iraƙ ?" Ku lura fa tsohon nan bai san da Annabi ya ke magana ba. Allah ya rufe mana wannan basira.

Kashegari kuma Annabi ya sake fita dai sansanar labarin rundunar Makka. A can ya sadu da waɗansu mutane biyu, ya tambaye su labari, suka ce masa rundunar Makka kam tana wuri kaza. Annabi ya ce, "Kuna iya gaya mana yawan mutanen da ke cikin rundunarsu ?" Suka ce, "A'a, ba mu san yawansu ba". Annabi ya sake tambayarsu, "Raƙuma nawa su ke sokewa ko wace-rana domin abinci ?" Mutanen nan suka ce, "Wata

rana tara. wata rana goma". Sai Annabi ya ce, "Yawansu, watau tsakanin mutum ɗari tara ke nan, da dubu". Annabi ya sake tambayarsu, "Wu wane ne cikin mashahuran Makka waɗanda ke tare da wannan runduna?" Suka ce, "Akwai da Utbatu ɗan Rabi'atu, da Shaibatu ɗan Rabi'atu, da Abu Jahali ɗan Hisham, da Suhailu ɗan Amru....."

Da jin haka sai Annabi ya nufi jama'arsa ya ce musu, "Ga Makka nan dukanta ta tinkaro ku". Daga nan Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya koma gefe guda, ya shiga roƙon Ubangijinsa yana cewa, "Ya Ubangijimmu ga rundunar Kuraishawa ta gabato, cike da alfaharinta, suna buri-wai su hana a yi biyayya ga umurninka, suna ƙaryata manzonka. Ya Ubangiji ina roƙonka nasaran nan da ka yi mini alkawarinta...."

## An Shaya Daga!

Gari na wayewa, aka yi arba da rundunar kafiran Makka, aka shaya daga. Tun kafin a fara, Annabi ya ba jama'arsa albishir cewa aya ta sauka, am ba shi labari su ke da nasara! Suka ɗauki hamdala da kabbara. Annabi ya sake ce wa jama'arsa amma fa su sani, Allah bai ba su iznin su kashe mutum guda ba daga cikin abokan gaba, sai in su sun fara kisansu. Shi ke nan, barade aka yi kabbara, aka fara gwabzo. Can sai wani jarumin barde, na kafiran Makka, wanda a ke ce masa Utbatu, ya fito ya yi wa kansa kirari. Sahabbai uku, daga cikin sahabban Annabi, suka zaburo, su ne Aufu, da Mu'awwizu, da Abdullahi ɗan Rawahata. Sai manyan baraden Makka suka tambaye su, "Ku ne su wa?" Suka karɓa musu, suka ce, "Barade ne daga cikin baraden Annabi waɗanda ya iske a Madina!" Sai kafiran Makka suka ce, "Ku tafi, ku ba mu wuri! Ba ku isa mu shaya daga da ku ba. Mu ba sabo da irinku muka zo ba. Ba mu bukatarku!"

Daga nan sai wani barden na kafiran Makka, ya hura hanci, ya yi kirari ya ce, "Ya Muhammadu, turo mana tsararrakimmu, daga mutanemmu da suka gudo daga Makka!" Daga nan sai Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya dubi baradensa ya ce, "Tashi Ubaidatu! Tashi Hamza! Tashi Aliyu!" Annabi bai gama rufa baki ba, sai baraden nan uku suna tsakar fage, ko wannensu yana girgiza kansakalinsa, yana kabbara.

# ANNABI MUHAMMADU

## Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi

BISMILLAHIR Rahmanin Rahim. Alhamdu lillahi Rabbil alamin. Ya Ubangijimmu, ka dada tsira ga shugabammu Muhammadu, mabudin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici !

Tun dawowata daga taron da aka kira mu a Ingila, a 1943, cikin yakin Hitler, mu Editor da Editor na Afirka ta Yamma, na rubuta dan littafi, "Tafiya Mabudin Ilmi." A ciki na bayyana cewa, cikin wasiyyar da na rubuta na bari, har na ce in na mutu, wana Alhaji Muhammadu Bello, walin Katsina na yanzu ya iyad da wani littafi da na ke da burin yi.

To, da Sarki Allah ya kudura ni ne zan iyad da littafina da hannuna sai ya nufe ni da dawowa, ba a kashe ni a can ba. Sai dai fa ko da shi ke na dawo, sai na zauna shekaru ban ci gaba da rubuta littafin can ba. Shiru, shiru, ran nan da tsakad dare, sai na ji ana buga mini kofa. Na ce, "Wane ne ?" Sai mai buga kofar ya ce, "Ni ne Bala naka. Ga wani mutum a zaure wai shi sarkin Gobir yana sallama. Na ce masa ka shiga, ya ce in shigo in tayad da kai."

Na taso na fito na ga ashe babban abokina ne M. Haruna, sarkin Gobir na Kalgo, jikan Sarkin Gwandu Haliru. Muka rungume juna don murna. Na ce masa, "Daga ina, ba ko labari ?" Ya ce, "Daga Takalafiya. Mun sauka Sabon Gari. Gobe za mu wuce Birnin Kabi. Amma na ce kome dare sai na gan ka, don in yi maka tuni."

Na ce, "Tunin me ?" Ya ce, "A cikin littafin da ka rubuta, "Tafiya Mabudin Ilmi," ka tuna ka ce ka fara wani littafi. To, ina ya ke ? Jama'a fa duk suna nan suna jira. Yau shekara nawa ba ka motsa ba, in ka mutu fa ?"

Na yi shiru, can na ce, "Ai kuwa da ni ban yi shirin ci gaba da shi ba tukuna. Ina nan ina kara damara da ilmi, domin kuwa dawa ne mai rukuki na ke so in yi wa jama'a, 'yanuwa, wadanda ba su sami yin ilmi mai zurfi ba, hanya a ciki."

Sarkin Gobir ya ce, "Wane rukuki ka ke niyyar ratsawa ?" Na ce masa, "Musulunci—Alkur'ani—Hadisi—Sunna !" Sarkin Gobir ya girgiza kai ya ce, "Hakika M. Imam ka dauki babban

buri. Sai ka yi shirin karɓar suka daga mahassada. Sai dai kuma Sarkin nan ' ya nufe ka da yi, shi zai zama fiyayyen garkuwa a gare ka.

Wannan jawabi nasa ya yi kamar zai sa ni in yi sanyi. Sai na tuna da wa'azin da wannan nawa, Alhaji Muhammadu Bello ya kan yi mini, in wani al'amari ya tashi rikita ni. Ya kan ce, da larabci. "Abubakar Imam, lam turlin nasa kullahum, aslih ma bainaka wa bainallahi wada'ahum." Ma'anar-sa, "Abubakar Imam, ba ka iya wa mutane su duka. Kai dai gyara abin da ke tsakaninka da Allah, su kuwa mutane ƙyale su."

Shi ke nan, gari na wayewa sai na ɗauki alƙalami, na yi istigfari ga Allah, na yi hamdala, na biɗi taimako na fara. Na so tun a wannan juzu'i na farko, in sa wa littafin sunansa—'Addinin Musulunci.' Amma na ga wannan suna zai zama tsalle. Domin kuwa, kafin mutum ya rubuta littafi a kan addinin musulunci, wajibi ne ya fara da ba da ko da ƙaɗan, daga tarihin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Wannan suna Muhammadu, a duk duniyan nan ba sunan da ke shan kira kamarsa. Da wannan suna baki zambar dubbai, bisa zambar dubbai, su ke furuci ko wace rana. Da wannan suna zuciyoyin mutane zambar dubbai, bisa zambar dubbai, su ke raurawa ko wace rana. Haka kuwa za su ci gaba da huruci da raurawa har ya zuwa ranar tashin kiyama !.

## Maɗaukakin Sarki Allah

TO, ga shi mun ce kowa zai wallafi littafi a kan addinin musulunci wajibi ne farkon littafin nan ya zama taƙaitaccen tarihi ne na Annabi Muhammadu, Wanda aka aiko ya kawo wa duniya, wannan babban saƙo. tsira da amincin Allah su tabbata ga wannan Manzo.

Amma kuma yaya za a ba da tarihin Annabi, ba a fara da ba'anin Sarkin da ya halicce shi ba, har ya aiko shi duniya. Sabo da haka ashe kafin mu fara maganar Annabi, ya wajaba mu fara da maganar sarkin da ya halicce shi tukun. Duk dai mun sani, ba sai wani ya gaya mana ba, cewa abincin da muka ciwo yanzu akwai wanda ya dafa shi, tufafin da mu ke sanyawa yanzu akwai wanda ya saƙa su, littafin da mu ke karantawa yanzu akwai

wanda ya yi shi. To, haka duk sa'ad da muka dubi wani abu wanda aka sana'anta, mu kan tuna da wanda ya sana'anta shi. Idan sana'ar ta yi kyau, ko ta yi bam mamaki, mu kan yabi wannan da ya sana'anta ta.

In haka ne kuwa, ashe idan kuma muka ɗaga kai muka dubi samaniya, muka ga shimfiɗar giragizai, fa tsayuwar rana, da yadda wata ke ratsa duhun giragizai, da yadda taurari ke kewayar samaniya, babu kuskuren hanya, muka sake sunkuyad da kai ƙasa, muka ga shimfiɗar ƙasa, da duwatsu, muka ga yadda ciyayi da itatuwa ke tsirowa, har su yi 'ya'ya, waɗansu masu zaƙi, waɗansu masu garɗi, waaɗnsu masu ɗaci, waɗansu masu tsami, muka dubi dabbobi na gida da na daji, na ruwa da na tudu, masu tafiya bisa ƙafafu da masu jan ciki, muka dubi masu iyo a ruwa, da masu tashi a sama, sai mu haƙiƙance lalle waɗannan su ma suna da wanda ya yi su.

Idan har waɗanda suka sana'anta abincin da muka ci, da tufafin da mu ke sanye, da littafin nan da mu ke karantawa, sun cancanci gutsuren yabo daga gare mu, ashe kuwa wajibi ne du. kan yabommu mu zuba shi ga Fiyayyen Masana'anta, wanda ya halicci sama da abin da ke cikinta, ya kuma halicci ƙasa da abin da ke cikinta. To, wannan Fiyayyen Masana'anta, Mabuwayin Koyi, shi ne Maɗaukakin Sarki Allah ! Allah shi ne mai iko ga ko wane ala'amari !

Kowa ya sani, ba sai wani ga gaya wa wani ba, cewa ko wane pan Adam almajiri ne na wani. Ba shi yiwuwa ya zama ka iya karatun nan da ka ke yi yanzu ba don ka sami malami ba da ya koya maka. Ba shi yiwuwa ya zama ke mace kin iya dafuwan nan da kika yi, ba don kin sami wata ba da ta koya miki. Hasali ma ko wane mutum, a farkon tashinsa, ba shi yiwuwa ya san abin da ke cutar sa, ko wandake amfaninsa, sai ya sami mai shiryad da shi. Shi mai shiryarwan nan shi ne zai riƙa nuna masa bambanci tsakanin abin da zai cuce shi da wanda zai amfane shi.

### Manzannin Allah

SABO da wannan aiki na shiryad da jama'a, Sarki Allah ya zaɓi waɗansu mutane, ya cika su, su kansu tukuna da shiriya iyakar cikawa, ya cika su da sani iyakar cikawa, sa'an nan ya sanad da su abubuwa masu amfanin bayinsa 'yan Adam, da

abububuwa masu cutarsu. Daga nan ya aiko da su duniya, gare mu, mu bayinsa, domin su zo su shiryad da mu, kamar yadda Allah ya shiryad da su, su sanad da mu, kamar yadda Allah ya sanada su. To, su wadannan mutane, su mu ke kira Manzannin Allah, amincin Allah ya tabbata a gare su su duka.

Manzannin Allah suna da yawa. Amma dai na farkonsu shi ne kakammu Annabi Adamu, amincin Allah ta yabbata gare shi Na karshensu shi kuwa ne Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Cikin Manzannin Allah, guda ishirin da biyar ne kadai aka fadi sunansu cikin Alƙur'ani. Sabo da haka wajibi ne a sansu, ga kawo sunayensu a wannan waka:

Ina danuwa, ga Annabawa daki daki,
Da Allah ya zana, ko kana so ka hardace.

A Alƙur'ani za ka gan su idan ka bi,
Guda ishirin ne, sa biyar don ka ƙarasa.

Da Adamu, Idirisu, Shu'aibu, da Yasa'u,
Da Iliyasu, sa Ishaƙu, Ayuba, Salihu.

Su hudu da Ibrahim, da Ludu da Yunusu,
Ka sa Zakriya, Musa, da Zulƙifili, Yusufu.

Da Yahaya, da Isma'ila sa Nuhu, Haruna,
Sulaimanu, sa Dawuda, ga kuma Yaƙubu,

Dada sai su Isa, sai Muhammadu shugaba,
Da yaz zo a ƙashe don bayanin da zai gamu.

To, wannan saƙo da Sarki Allah ya aiko manzanninsa da shi, don su zo su sanad da bayinsa, 'yan Adam, shi a ke kira addini. Amma saƙon da Sarki Allah ya aiko Manzonsa na ƙarshe da shi, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, shi a ke kira addinin musulunci. Yanzu in wani ya tambaye ka, mene ne addinin musulunci, me za ka ce? Sai ka ce masa, saƙon da Sarki Allah ya aiko Annabi Muhammadu da shi zuwa ga dukan al'umma na duniya, shi ne musulunci.

To, kafin mu fara ba da tarihin wannan Manzo na ƙarshe, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare

shi, ya wajaba mu fara ba da tarihi kaɗan daga cikin Manzan-nin da aka riga aiko da su. Bari mu fara ta kan shugabammu, Annabi Nuhu, amincin Allah ta tabbata a gare shi.

## Annabi Nuhu

SA'AD da Maɗaukakin Sarki Allah ya aiko Annabi Nuhu duniya ba ga dukan kabilu na duniya ya aiko shi ba. Ya aiko shi ne ga mutanen da ya fito a cikinsu. Allah ya hore shi ya zo ya kira su ga bin Allah. Ya gaya musu abubuwa marasa kyau, ya hore su da bari, ya gaya musu masu kyau, ya hore su da aika-tawa. Aka haife shi kamar yadda a ke haihuwar ko wane ɗa, ya girma, kana aka nufe shi da kawo saƙo. Ya zo, ya yi kira ga jama'arsa, su bi Allah, su aikata abin da ya umurce su da aika-tawa, su guji abin da ya hore su da gujewa. Amma ina, sai ka-ɗan daga cikin mutanen nasa suka bi maganarsa. Ya yi ta ƙoƙa-rin bayyana musu masifar da za ta faɗa musu in sun saɓi saƙon Allah, da nasihar da za ta same su in sun bi. Amma ina ? Da yawa ba su karɓa kiran ba.

Da Annabi Nuhu ya yi, ya yi, ya ga dai abin ya faskara, har Ubangiji Allah ya bayyana masa babu sauran wanda zai ba da gaskiya gare shi daga cikin mutanensa. Sai ya roƙi Ubangiji Allah da ya hori jama'an nan tasa da azaba. Ubangiji ya karɓi roƙonsa, ya sanad da shi cewa zai cika ƙasa dar uwa yadda duk jama'ar za ta nutse ciki. Ubangiji ya umurce shi, shi annabin, da ya sassaƙa jirgi, wanda zai shiga shi da waɗanda suka ba da gaskiya da shi. Annabi Nuhu ya shiga sassaƙar jirgi. Mutanen da ba su ba da gaskiya da shi ba, da suka ji dalilin sassaƙa jirgin, sai suka riƙa zuwa suna yi masa dariya. Suna cewa, "Annabci ya ƙiya ne kuma aka koma sassaƙa ?"

Allahu Akbar ! Yana gama sassaƙa jirgi, wa'adin Allah ya cika, sai kawai aka ga sama da ƙasa duk sun kece da kawo ruwa. Tun jama'a na gudu daga wannan tudu su hau wannan har abin ya buwayi tudu. Ruwa ya shafe ƙasa, bai rage kan wani abu ba a waje. A sa'an nan sai Annabi Nuhu kawai, amincin Allah ya tabbata a gare shi, shi kaɗai ke yawo cikin jirginsa, shi da waɗanda suka ba da gaskiya a gare shi, da dabbobi, da dai duk waɗanda Ubangiji ya nufe shi da ɗauka. Amma kafirai duk sun halaka ! Da suka ƙare, Allah ya umurci sama da ƙasa

da dainawa. Wannan shi ne abin da ƙaramin ilmimmu ya ba mu ikon gutsurowa daga tarihin wannan shugaba namu, Annabi Nuhu. Asalin wannan labarin duk yana nan rubuce cikin AlƘur'anin Allah mai girma. Tun daga nan ina so ku fara sa ido ku gani. Ko wane Annabi aka aiko in kun duba labarin yadda aka haife shi, ko yadda ya girma, ko yadda ya yi fama da jama'arsa, sai ku gane ashe ko wane Annabi rayuwarsa tare ta ke da abubuwa masu ban mamaki.

Ban da labarin nan na Annabi Nuhu, amincin Allah ya tabbata a gare shi, labarin shugabammu Annabi Musa, kallamu ayar Allah shi ma abin mamaki na cikinsa.

## Annabi Musa

ANNABI MUSA, amincin Allah ya tabbata a gare shi, yana cikin kabilar Bani Isra'ila ne. A Masar aka haife shi, a zamanin wani Fir'auna da a ke kira Alwalidu ibn Musab-ibnal-Rayyar. Haka aka ruwaito shi cikin littafin da a ke kira Hazinu. Sunan mahaifin Annabi Musa Imrana. A lokacin, su Bani Isara'ila suna ƙarƙashin daular wannan Fir'auna ne, sarkin Masar-Shi kuwa wannan Fir'auna, ba abin da ya ƙi, kamar wannan kabila ta Yahudawa Bani Isra'ila. Ga su a ƙarƙashinsa, amma kamar suna ƙarƙashin wuta. Azaba kusan ba irin wadda ba shi gwada musu. Hasali ma, abin har ya kai ya ba da Oda; in Yahudawa sun haifi ɗa namiji, to, sai ya ce a yanke shi. Wai don wani boka ya gaya masa cewa za a haifi wani jinjiri a cikinsu wanda zai ɓata masa mulkinsa. Amma idan sun haifi mace wannan ita ba a yanka ta.

Ana nan haka, sai wata mace, a cikin Yahudawa, watau matar Imrana ta haifi ɗa, aka sa masa suna Musa. Shi ne kuma Annabi Musa da za mu ba ku labarinsa a yanzu. Da uwarsa ta haife shi, sai tsoro ya cika ta, ga shi ya fito namiji, ba mace ba, watau Fir'auna zai sa ke nan a zo a kama shi a yanka, kamar yadda a ke yanka sauran 'ya'yansu maza. Tana cikin wannan zulumi, mai baƙanta rai, sai Maɗaukakin Sarki Allah ya aiko mata da ilhami aka ce mata ta sami akwati, ta saka jinjirin a ciki ta rufe, ta ɗauka ta je ta jefa shi cikin Kogin Masar.

Shi ke nan sai ta zabura, ta bi umurnin Mahaliccinta. Da ta jefa shi a kogi ta dawo gida, sai ruwa ya yi ta tafiya da shi. Uban.

giji ya yi mata alkawarin zai mayar mata da shi, ya kuma sanya shi cikin Manzanni. Bisa ga nufin Maɗaukakin Sarki Allah, har ruwan ya kai akwatin kusa da Birnin Fir'auna, sai akwati ya sarƙafe a gefen kogi. Shi ke nan, waɗansu jama'ar Fir'auna sun zo ɗibar ruwa sai ga akwati, suka ɗauka suka kai wa matar Fir'auna. Da aka fasa akwatin sai ga jariri ciki, da ransa kuwa, ba matacce ba. Daga nan sai matar Fir'auna ta dube shi, ta yi mamaki, ta ce, "Kada a kashe shi, kila in ya girma ya zama mai amfani a gare mu, ko kuwa ma mu riƙe shi kamar mu muka haife shi." Shi ke nan, Annabi Musa ya yi ta girma a cikin Birnin Fir'auna. Mun gaya muku kuwa tun baya, irin zaman da jama'ar su Annabi Musa, watau Bani Isra'ila su ke yi a ƙarƙashin daular Fir'auna. Hasali dai ma Yahudawa a lokacin su ne kamar bayi na mutanen Masar.

Ana nan a haka, da Annabi Musa fa ya kawo ƙarfi, sai ya fara tunanin yadda zai taimaki Yahudawa, har ya cire musu wannan ƙangi na bauta, da ƙasƙanci, da azaba, waɗanda su ke samu daga Fir'auna.

Wannan tausayi na Annabi Musa, zuwa ga jama'arsu ta Bani Isra'ila, ya yi ƙarfi a zuciyarsa, har ya kasa ɓoyuwa. Ta haka, har labari ya isa ga Fir'auna na irin tunanin da Annabi Musa ke yi, da irin burin da aka farga yana cikin zuciyarsa. Da Fir'auna ya ji sai ya harzuƙa ya shiga shirya yadda zai hori Annabi Musa, horo mai tsanani. Da Annabi Musa ya sami labari, sai ya sulale, ya bar garin yana cewa, "Ubangiji, ka kuɓutad da ni daga mutane azzalumai."

Annabi Musa, ya yi ta tafiya, ya yi ta tafiya har Allah ya kai shi wani birni da a ke kira Birnin Madyana. Wannan birni yana nan kusa da Birnin Tabuka. Watau ga shi nan tsakanin Madina da ƙasar Sham. Da ya shiga garin sai ya tarar da mutane jingim an taru bakin wata rijiya, ana turereniyar ɗiban ruwanta. Annabi Musa ya duba daga gefe guda, sai ya ga waɗansu 'yam mata su biyu, sun zo don ruwan, amma ba su da ƙarfin kokawa da masu ƙarfi. Sabo da haka suka raɓe, suna jiran sauran wani. Ganin haka, sai tausayinsu ya kama Annabi Musa. Ya matsa, ya keta jama'a, ya samo musu, ya shayad da dabbobinsu, suka tafi.

Shi kuwa ya koma gindin wata itaciya ya zauna yana cewa, "Ya Ubangiji, ni mabukaci ne ga abin da ka saukar mini daga alherinka." To, da 'yam matan nan suka koma gida sai ubansu

ya tambaye su, "Yau lafiya kuka komo da wuri haka ?" Sai suka ba shi labarin taimakon da wani mutum baƙo ya yi musu.

Sai tsohon ya aiki ɗaya daga cikinsu, ya ce ta je ta kira masa baƙon nan don ya saka masa. Da shi Annabi Musa ya zo masa, ya tambaye shi daga inda ya ke. Da ya ba shi labari, sai ɗan tsohon nan ya ce, "Kada ka ji tsoro, ka kuɓuta daga mutane azzalumai !"

A nan, tsohon nan ya ce masa, "Ina so in auram maka ɗaya daga cikin 'ya'yan nan nawa biyu. Sadakinta kuwa, ka zauna tare da ni, kana yi mini hidima, shekara takwas. In ko ka cika, suka kai goma, wannan ganinka ne. Ni ba na nufin tsananta a gare ka. Za ka same ni cikin bayin Allah, masu salaha, in sha Allahu !"

Annabi Musa ya karɓi wannan aure, bisa wannan sadaki, ya ce, "Allah shi ne shaida ga abin da mu ke faɗa."

Aka yi aure ba wata jayayya. Ya jama'a, wannan irin aure bai ba ku mamaki ba ? Babu mamaki, nufi ne na Maɗaukakin Sarki Allah. Yanzu ne za ku saurari abin mamaki. Kuna zato, wane ne wannan mutum, wanda ya aura wa Annabi Musa ɗiyarsa a haka ? Im ba ku san shi ba, shi ne shugabammu Annabi Shu'aibu. Ka ji nufin Allah, Annabi ya auri ɗiyar Annabi ! Shi ke nan, Annabi Musa ya zauna tare da surukinsa, yana yi masa hidima har alkawari ya cika.

## Fir'auna Ya Halaka !

DA WANNAN lokaci ya cika, ya yi ban kwana da surukinsa, ya tashi zuwa Masar. A kan hanya sai Maɗaukakin Sarki Allah ya aiko da wahayi, zuwa ga Annabi Musa, ya umurce shi da ya je ga Fir'auna, ya kira shi da ya bi Allah, ya yi imani da shi, ya kuwa daina gwada wa Bani Isra'ila azaba hakanan. Annabi Musa ya tashi, ya tafi gare shi ya aikata kamar yadda Sarki Allah ya umurce shi. Amma ina ? Fir'auna bai karɓa kira ba !

Shi ke nan kuma sai Ubangiji Allah ya umurci Annabi Musa da ya kwashe dukan Bani Isra'ila, ya gudu da su, ya mai da su ƙasar Sham. Sai ya tashi da dare, ya kwashe su, ya yi niyyar ya sulale da su a asirce. Amma sulalewa ba ta yiwu ba, sai aka kai wa Fir'auna labari.

Da ji sai Fir'auna ya harzuƙa. Ya hawo da jama'arsa suka bi. Suka kuwa iske su can sun ƙai bakin Bahar Maliya. A nan Allah ya umurci Annabi Musa da ya bugi ruwan kogin da sandansa. Ya ɗaga sanda ya buga, sai ya ga ruwa ya rabe biyu. Shi ke nan, ya taka, shi da jama'arsa, suka haye. Fir'auna kuwa da rundunarsa, da ganin ga hanya ta samu, sai su ma suka ƙunduma. Suna kawowa tsakiya, kogi ya sake gamewa, bisa ga nufin Allah.

Na taƙaita muku labarin Annabi Musa, a nan, ba domin labarin yana taƙaitacce ba, sai dai domin ilmin mai rubuta wannan littafin da ku ke karantawa shi ne taƙaitacce.

Malam ku duba, wa zai yi musun akwai mu'ujrza abar mamaki game da rayuwar wannan Annabi na Allah, shugabammu Musa, amincin Allah ya tabbata a gare shi ?

## Annabi Isa

HASALI dai, da ya ke tarihin Annabi Muhammadu ne mu ke niyyar bayarwa, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ba na dukan Annabawa ba, sai mu dakata a nan. Sai dai ko a haka, ba shi yiwuwa, mu gina wannan harsashi, ba tare da ba da tarihin babban jigo ba, guda, Annabi Isa—Isa Ruhullahi !

A cikin dukan Manzannin Allah, Manzonsa Isa, amincin Allah ta tabbata a gare shi, shi ne Manzo wanda ya fi kusa da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Shi Annabi Isa, Allah ya nufi uwarsa, Maryama, yardar Allah ta tabbata a gare ta, ta haife shi ba tare da wani namiji ya kusance ta ba. Maɗaukakin Sarki Allah ya hukunta haka, don ya nuna wa 'yan Adam cewa, yadda ya ke iya sanya mace ta haihu bayan namiji ya kusance ta, haka ma yana iya sanyawa mace ta haihu ba tare da namiji ya kusance ta ba. Yana kuma iya sanya namiji ya haihu ba tare da kusantar mace ba, in ya so. Haihuwar Annabi Isa ba da uba ba aya ce cikin ayoyin Ubangiji. Kamar yadda ta bayyana ga labarin Annabawa na baya.

To, da uwarsa Maryamu ta ɗauko shi, danginta suka ƙyalla ido suka gan ta da ɗa, sai suka ce cikin mamaki, "Daga ina kika samo jariri alhali kuwa ga ki ba ki da miji." Sai ta ce musu, "Ku tambaye shi." Sai suka ce, "Yaya za mu tambaye shi, ga shi ɗan jariri ƙarami, a bisa zanen goyo ?"

Daga nan, sai shi jaririn ya buɗa baki, ya karɓa musu, ya ce, "Ni bawan Allah ne. Allah ya zaike mini da littafi, ya kuwa sanya ni in zama Annabi." Duk mutane suka ruɗe, tsoro ya kama su game da jawabin jaririn nan, na shugabammu Annabi Isa, amincin Allah ta tabbata a gare shi.

Ana nan haka, da Annabi Isa ya girma, sai Ubangiji ya aiko masa da annabci. Ya aiko da shi ga Bani Isra'ila. Ya zama yana wa'azi bisa ga abin da Sarki Allah ya umurce shi da shi, na cikin Linjila.

Jama'a suka ƙaryata shi, kamar yadda aka yi ta ƙaryata Annabawan da suka zo kafinsha. Sai su dubi wani abu mai wuya su ce ya yi musu su gani, in gaskiya ne, Allah ne ya aiko shi. Nan da nan sai Allah ya ba shi iko ya yi abin. In sun ga wannan, sai su ce kai sihiri ne, ba wata mu'ujiza ba ce ta annabci Ba wanda ya aiko shi! Hasali dai har makaho, Allah ya ba Annabi Isa iko ya maida masa da ganinsa. Ya ba shi iko ya warkad da mai ciwon da ya buwayi magani. Kai, har matacce ma an kawo wa Annabi Isa, Allah ya ba shi iko ya mayar masa da ransa. Amma duk da haka jama'arsa da yawa ba su yarda da shi ba a lokacin.

Da himmarsa ta iyad da saƙon Allah ta tsananta, sai Yahudawa suka ƙulla makirci, wai su ƙashe shi. Aka kamo shi har aka zo da shi wani wurin da aka shirya wai za a rataye shi. A nan Maɗaukakin Sarki Allah ya nuna shi ne Fiyayyen Mai Hikima, ya aikata abin da ya aikata. Ya ɗauke shi zuwa sama. Annabi Isa amincin Allah ya tabbata a gare shi, ya kuɓuta daga wannan halaka.

A nan zan taƙaice labarin girman Annabi Isa, da yawan hikimomin Ubangiji na game da shi. Annabi Isa ya wuce ya bar mana wa'azin littafinsa mai tsarki, Linjila, wanda ya tara Zabura ta Annabi Dawuda, da Attaura ta Annabi Musa, da busharar bayyanar Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

To, bayan Annabi Isa da shekara kamar dari shida ne, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya bayyana. Labarinsa shi ne za mu kutsa yanzu.

## Kabilun Larabawa

DAshi ke tarihin Larabawa yana da tsawo, kuma da rikitarwa, ga mai ƙaramin ilmi irimmu, shi ya sa zan gajarce shi. Su dai Larabawa dukansu sun rabu ne kashi biyu. Larabawan birane, da Larabawan ƙauye. Larabawan birane su zaune su ke kamarmu sai noma da ciniki. Amma Larabawan ƙauye, waɗanda a ke kira Badwi, su kamar Baroro ne, Filanin daji. Haka za ka ga suna ta bin daji suna kiwon dabbobinsu. Ba su gina gidaje sai dai su kafa tantuna, yadda dai Filanin daji ke bukkoki da kara ko da tsumangi.

Larabawan daji, Badwi, ba su biɗar su sha wata daula, su dai ba su sa kome gaba sai jaruntaka, sai kuwa biyayya ga kabilarsu da son ƙasarsu. Ba su aurarwa a waje, ba su aurowa, Filanin daji dai sosai !

## Harami

KASAR Larabawa a da rarrabe ta ke lardi uku. Su ne Hijaz watau ƙasar Makka, da Yaman da lardin Najad, watau inda fadar sarkin Makka na yanzu ta ke, Abdul Aziz. Ibn Sa'ud. Cikin lardi lardi ɗin nan ne, ke da lardin Harami. Harami nan ne lardin da aka haramta yaƙi a ciki, tun tun tuni, tun iyakar sanin 'yan Adam, na zamanin bayyanar musulunci, haka abin ya ke. Kome ya sa jama'a suka riƙi wannan wuri a haka Allahu shi ɗai ya sani. Sai dai abin da ke tafe nan gaba ya isa ya jefa mu cikin kogin tunani. Ga shi :

A cikin lardin nan na Harami, nan ne Maɗaukakin Sarki Allah ya nufi ajiye 'Dakinsa mai tsarki Ka'aba. 'Dakin Ka'aba yana cikin Birnin Makka ne. Ga ya nan mil hamsin daga Bahar Maliya. A wajen Musulmi, Birnin Makka kamar tauraro ya ke a cikin birane na duniya. Dalili kuwa, a Makka cibiyar Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ta ke. A Makka aka haife shi. Kuma a Birnin Makka nan Ka'aba ta ke. 'Dakin Allah mai tsarki.

Sabo da darajar wannan birni na Makka, Larabawa suka raɗa masa suna, Ummul Kura. Watau Uwar Birane. Abin mamaki shi ne wannan, Birnin nan na Makka tun tun tun tuni, tun kafin bayyanar musulunci, mutanen ƙasar su ke riƙe da shi da daraja. Maɗaukakin Sarki Allah kuma ya nufi wannan birni na Makka, da tsarki haka, tun asalin asali, don ya zama mahai-

far Mai Isarki Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

A wajen al'amarin duniya kuma, Birnin Makka, tun da ma can mashahuri ne. Domin kuwa babban zango ne ainun ainun, na ayarin da ke tafiya, tsakanin ƙasar Yaman zuwa ƙasar Sham. Wannan bayanin da mu ke yi, ayoyi ne, irin waɗanda suka nuna wa 'yan Adam na can can zamanin da, cewa lalle a gaba akwai wani babban al'amari a game da wannan birni na Makka. Ashe kuwa ba ƙarya ba ne.

## Annabi Ibrahim

NAbar labarin Annabi Ibrahim a baya, don in ji daɗin zura shi da labarin Annabi Muhammadu. Daga labarin Annabi Ibrahim, za mu ƙara gane irin ayoyin da Sarki Allah ya nufa, suka yi ta aukuwa a karkarar Makka. Sai ka ji abu ya auku kamar babu dalili, ashe dalili yana zuwa. Bayyanar musulunci ta hannun Babban Manzo, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Da shi ke zan ambato tarihin zaman Annabi Isma'ila a Makka, tilas ne im faro da labarin ubansa, Annabi Ibrahim amincin Allah ya tabbata gare su. Ko da shi ke an yarda da cewa Annabi Isma'ila shi ne farkon wanda ya zaɓi Makka ta zama masa garin zama, duk da haka an san ko kafin wannan lokaci, wannan wuri sananne ne ga 'yan Adam. Sai dai ainihin labarin wurin ne, kafin bayyanar Annabi Isma'ila, shi ya buwayi malaman tarihi ganowa.

Wannan wadi na Makka an san shi tun tun tun tuni, domin ayari na fatake su kan kafa tauntunansu a wurin. Ya zama zango na zuwa ga ƙasar Falasɗinu, ko daga jihar ƙasar Falasɗinu zuwa ƙasar Yaman.

Yanzu ne fa za mu kutsa kai cikin wani ƙunƙurmin dawa na tarihi. Shi Annabi Ibrahim, mahaifin Annabi Isma'ila, yana cikin zuriyar Annabi Nuhu ne. An haife shi, zamanin Namaruzu. Mulkin Namaruzu a lokacin ya mamaye ƙasar Iraƙ. Ubansa wani masassaƙi ne. Ana kiransa Azara. Aikinsa sassaƙa gumaka na itace, yana sayarwa ga jama'arsu, su kuwa suna bauta musu.

Ana nan ana nan, sai Maɗaukakin Sarki Allah, ɗa ya nufi ya bayyana aya cikin ayoyinsa, sai ya nufi masassaƙin nan da haihuwar ɗa, aka sanya masa suna Ibrahim. Ashe Annabin Allah ne! Da ya yi wayo sai Allah ya lurad da shi, ya ga irin aikin da ubansa ke yi. Ya ga ubansa, tare da shi su ke zuwa daji, su saro itace, su zo gida a sassaƙa mutummutimi, a sayar. Sai ya ga wai kuma mutane da suka saya sun mai da kawunansu bayi ga sassaƙe-sassaƙen nan na ubansa. Har ya ga yadda su ke ƙasƙantad da kai gare su, da yadda su ke sujada a gare su. Alhali kuwa rassan itatuwa ne, waɗanda suka saro, shi da ubansa, suka sassaƙa. Saboda haka idan uban Annabi Ibrahim ya ba shi tallan gumaka, ga irin tallan da ya ke yi musu "Wa zai sayi abin da zai cuce shi, ba zai amfane shi ba!"

Ana nan dai, ran nan, sai Annabi Ibrahim ya tambayi ubansa abin da ya sa zai sassaƙa itace da hannunsa, kuma ya koma ya riƙa yi masa sujada yana bauta masa. Annabi Ibrahim ya ci gaba da tambayar mutane, yaya za ku ga an karyo itace, an sassaƙa, sa'an nan ku saya kuma ku yi ta bauta wa itatuwa?

Sa'ad da sarki Namaruzu ya sami labarin irin maganganun da Annabi Ibrahim ke yi, da irin tuntuntuninsa sai ya aika a kira shi. Da ya zo gabansa ya tambaye shi. "Wane ne sarkin nan naka da ka ke kiran jama'a zuwa ga bauta masa?"

Annabi Ibrahim ya karɓa ya ce, "Ubangijin nan nawa shi ne mai rayarwa kuma shi ne mai matarwa!" Sai Namaruzu ya ce, "Ni ne mai rayarwa, kuma ni ne mai matarwa!" Sai ya aika aka kamo mutum biyu daga kurkuku, ya sa aka yanka guda, guda kuwa ya sake shi. Ya dubi Annabi Ibrahim ya ce, "Ka gani ko, na kashe wannan, na raya wannan. Ni ne mai rayawa, ni ne ma kashewa!"

Daga nan Annabi Ibrahim ya ci gaba da cewa, "Ubangijina yana jawo rana daga gabas ya kai ta yamma. To, kai kawo ta daga yamma ta yi gabas." A nan Sarki Namaruzu ya iyi turus.

Da mahaifin Annabi Ibrahim, amincin Allah ya tabbata gare shi, ya riƙa jin irin kalamin da ke fitowa bakin ɗansa yana sukar bauta wa gumaka, sai ransa bai so ba. Yana tsoro kada ɗansa ya kashe masa kasuwa. Amma yaron shi sai ya ci gaba da waye wa jama'a kai, da buɗe musu ido, yana nuna musu wautarsu a fili. Sannu sannu, sai waɗansu suka fara gane cewa lalle dai aikin wauta su ke yi.

## Annabi Ibrahim Ya Karya Gumaka

ANA nan, ran nan sai Annabi Ibrahim ya tafi wurin da gumakan gari ke tare ya kakkarya su duka. Amma ya bar babban gunkin kawai, shi bai karya shi ba. Da safe mutane suka ga gumakansu an kakkarya, sai suka ce, "Ba wanda ya yi wannan aiki sai ɗan yaron nan Ibrahim!" Sai suka je suka kamo shi. Suka zo da shi gaban taro, don a tambaye shi. Suka ce masa, "Yalla kai ne ka aikata wannan al'amari ga guma. kammu, ya Ibrahimu?" Daga nan Annabi Ibrahim ya karɓa, ya ce, "Bal, ku bar wannan zance, babbansu, wannan, shi ya aikata haka. Ku tambaye su ku ji in suna iya magana."

Annabi Ibrahim bai yi haka ba, sai bayan da hikimar Allah ka sa ya yi tunanin tsananin ɓata ga bauta wa gumaka. Ya sakankance kam bauta wa gumaka ɓata ne. Annabi Ibrahim shi ya san Ubangijinsa shi ne Allah. Amma da ya yi nufin ya kawo hujja sabuwa ga waɗansu jama'arsa masu bauta wa tauraro, da masu bauta wa wata, da masu bauta wa rana, sai ya ƙallafa wa kansa jahilci—yau ya shiga cikin wannan ƙungiya, gobe ya fita ya shiga waccan, tare da soke dalilansu, har daga ƙarshe ya zo ga maƙasudinsa da ya ke son su gane kuma su aikata. Wannan ya faru bayan ya bar ƙasarsa, ya komo Sham.

A sa'ad da Annabi Ibrahim ke wannan dabara ta kama jama'arsa da hujja, ran nan da ɗare ya yi sai ya ɗaga ido sama ya ga tauraro. Sai ya ce, "To, ni wannan shi ne Ubangijina!" Watau ya nuna wa masu bauta wa tauraro kamar yana tare da su. Amma daga baya sai ya ɓace, sai ya ce, "Af, ni kam ba na son wanda ke ɓacewa." Ka ga ya nuna musu ya bar su ke nan.

Daga baya sai ya ga wata ya ɓullo. Sai ya ce, "Mh, wannan kam shi ne Ubangijina!" Shi kuma wata can an jima ya ɓace. Sai Annabi Ibrahim ya ce, "Idan Ubangijina bai shiryad da ni ba, zan zama ke nan a cikin mutane ɓatattu." Duk wannan ya faɗa ne don ya ganad da jama'arsa a kaikaice kamar da kowa ya ke yi, ba da su ba.

Da gari ya waye ya ga rana ta fito, sai ya ce, "Wannan daɗa kam shi ne ubangijina. Wannan ma ai ya fi waɗancan duka girma!" Da magariba kuma sai ita ranar ta faɗi. Annabi Ibrahim ya ce, "Ya ku mutane, ni kam ba na cikin abin da ku ke shirkarsa. Ni na fuskanta kaina ga wanda ya halicci sammai da ƙassai. Ni kam ba na cikin masu shirka."

Hasali dai Annabi Ibrahim bai ci nasara ba ga shiryad da dukan mutanensa. Sakayyar ma da ya samu daga gare su, ita ce da suka gaji da kiransa, sai suka hura wuta, suka kamo shi, suka jefa shi. Ubangiji ya hori zafin wutan nan ya koma sanyi. yadda ba zai cuci Annabi Ibrahim ba. Ta haka, Maɗaukakin Sarki Allah ya kuɓutad da shi. Amma wannan maganar ta ƙonewa ta auku a Iraƙ game da Namaruzu, amma ƙissar taurari kuwa ta faru a can Falasɗinu ne.

## Annabi Ibrahim A Masar

DA Annabi Ibrahim ya ga ya kuɓuta, sai ya bar garinsu, ya koma Falasɗinu bisa ga umurnin Allah. Ya tafi tare da matarsa Saratu. Daga nan Falasɗinu, ya ci gaba har Masar. To, ita matan nan tasa, Saratu, kyakkyawa ce ainun. Sarkin Masar na lokacin shi kuwa in ya ga kyakkyawa ba a raba su.

Da Annabi Ibrahim ya je ga sarki, sarki ya tambaye shi labarin matan nan da su ke tare, Saratu. Sai ya ce wa sarki 'yaruwarsa ce. Ya faɗi haka, gudun kada sarki ya ji matarsa ce, ya ce zai kashe shi ya ƙwace, ya aura. Allahu Akbar, Ibrahimu Halīlullahi ! Da dare ka san abin da ya faru ? Ai ko da sarkin nan ya yi barci, sai ya yi mafarki, aka ce masa matan nan da ya ke so ya ƙwace daga hannun baƙon nan Ibrahim, tana da miji. Sabo da haka sai ya mayad da ita ga Annabi Ibrahim. Ya kuma ba ta kyauta. Cikin kyautar har da bauya, ana kiranta Hajaratu.

## Annabi Isma'ila

TO, da shi ke Saratu ta yi shekaru da dama tare da Annabi Ibrahim ba ta haihu ba, sai ita Saratu ta yardam masa ya sanya Hajaratu ɗaka. Abin nufin Allah kuwa, ba a daɗe ba, sai ita Hajara saɗakarsa ta sami ciki, ta haihu, ɗa namiji, aka sanya wa yaro Isma'ila. Ana nan ana nan, ina ya Allah, babu ya Allah sai ran nan aka ji kamar wani abu ya tura Saratu. Sai kawai aka ji ta ka da baki, a cikin nufin Sarki Allah, ta ce wa Annabi Ibrahim mijinsu, ya ɗauki Hajara da ɗanta Isma'ila, ya kai su can wata ƙasa ya bar su ! A lokacin kuwa, Annabi Isma'ila yana jinjiri kurum.

Annabi Ibrahim ya yi bakin ciki da jin wannan kalami ya fito daga bakin matarsa. Daga nan sai Ubangiji Allah ya yi masa umurnin da kada wannan magana ta sa shi bakin ciki.

Aka umurce shi da duk abin da Saratu ta ce masa ya saurara ya kuma aikata.

Shi ke nan Annabi Ibrahim ya karbi umurnin Ubangijinsa, ya dauki Hajara da dansu Annabi Isma'ila suka yi ta tafiya cikin daji, kwana da kwanaki har Allah, a cikin ikonsa, ya kai su wata karkara ta Sahara, wadda a ke kira Bakka. A nan Birnin Makka ya ke yanzu. Wannan suna Makka, da suna Bakka duka daya ne. Sabawar karya harshe shi kawai ya bambanta su.

A can, cikin kunkurmin dawan karkaran nan ta Bakka, Annabi Ibrahim ya yi wa Hajara bukka, ya sanya ta ciki, tare da goyonta Annabi Isma'ila. A cikin umurnin Allah ya bar su su kadai a wurin ya juyo fuskar gida. Wurin da Annabi Ibrahim ya yi musu wannan bukka, yana nan yanzu kusa da Ka'aba. Wurin shi a ke kira Hijiri Isma'ila.

To, da Annabi Ibrahim ya ba da baya zai wuce, Hajara ta tambaye shi, har sau uku, dalilin da ya sa ya kawo su nan ya yar cikin karkarar Bakka, ba isasshen abinci, ba wurin kwana, ba mai gadi. Amma Annabi Ibrahim ya yi shiru, bai ce mata kala ba.

Daga nan ta sake tambayarsa, "Shin wannan umurnin Sarki Allah ne ka bi ko kuwa?" Annabi Ibrahim ya bude baki ya ce, "Na'am!" Sa'an nan Hajara ta ce, "In haka ne kuwa, ashe Allah ba zai bar mu mu halaka ba."

Annabi Ibrahim ya wuce, yana mai tausayi a gare su. Da ya bace, yadda Hajara ba za ta gan shi ba, sai ya mai da fuska wajen Ka'aba, ya daga hannu sama, ya yi roko ga Ubangiji, ya ce, "Ya Ubangiji, ga tsatsona na kawo, na ajiye a karkarar da ba ta ko nomuwa, kusa da 'Dakinka Mai Tsarki. Ya Ubangijimmu, ka nufe su da ibada gare ka. Ka jawo zukatan al'umma zuwa gare su. Ya Ubangiji kawo musu 'ya'yan itace don su yi godiya a gare ka."

Shi ke nan Annabi Ibrahim ya wuce. 'Dan abincin da ya bar wa su Hajara kuma duk ya kare. Suka komo ba abinci ba ruwan sha. Daga nan Annabi Isma'ila, dan jinjiri, ya kama kuka, yana haure haure.

## Safa Da Marwa

TAUSAYI ya kama uwar, Hajara ta ɗimauta ta rasa abin da za ta yi, sai ta fara kai tana komowa tsakanin waɗansu 'yan duwatsu guda biyu da ke kusa. Su ne Dutsen Safa da Dutsen Marwa. In ta ruga ta hau kan Safa, ta hanga ko ta ga alamar ruwa, ba ta gani ba, sai ta gangaro, ta ruga ta hau bisa kan Marwa, ta hanga.

Da yaro dai ya tsananta da kuka sai ta koma ga Sarki Allah da addu'a. Allahu Akbar, a cikin karɓa wannan roƙo, sai Maɗaukakin Sarki Allah ya nufi idon ruwa da ɓuɓɓugowa daga ƙarƙashin ƙafafun Isma'ila. Shi ruwan ya riƙa yin ƙara zam, zam, zam. Waɗansu kuwa sun ce ita Hajara, ita ta riƙa cewa idon ruwan nan, zam zam zam, wai da harshen mutanen Farisa, dakata, dakata, ke nan. Daga nan dai aka sami Rijiyar Zam-zam mai albarka, wadda ke a Makka har yanzu. Asalinta ke nan. Ita ce alhazai ke kawo mana ruwanta a nan ƙasar. Allahu Akbar!

## Layya Da Annabi Isma'ila

TO, sa'ad da fa kuma ya tasa, ran nan sai Ubangiji Allah ya umurci Annabi Ibrahim da ya yanka Isma'ila. Saboda tsananin biyayya, ga umurnin Maɗaukakin Sarki Allah, Annabi Ibrahim bai tsaya ba. A'a, sai kawai ya ɗauki umurni daga Maɗaukakin Sarki Allah. Sai ya tashi da safe ya ja ɗansa, suka fita suka nufi bayan gari.

Suna cikin tafiya, don jarrabawa, sai Ubangiji Allah ya nufi Shaiɗan da zuwa ga Hajara, cikin siffar 'yan Adam, ya ce mata, "Ke Hajara, shin kin san inda Ibrahim zai tafi da ɗanki?" Ta ce, "I, sun fita bayan gari ne su samo itace." Shaiɗan ya ce, "Wallahi ba itace suka je samowa ba, ya tafi da shi ne ya yanka shi." Hajara ta ce, "To, ba banza ba, ya fi kowa tausayinsa." Shaiɗan ya ce, "Ba ki sani ba, ne ai cewa ya yi wai Allah ne ya umurce shi da ya yi haka." Sai Hajara ta ce, "Idan Allah ne ya umurce shi da aikata haka, ashe kuwa wajibi ne ya bi umurnin Ubangijinsa." Sai Shaiɗan ya yi waje, yana mai baƙin ciki.

Da tashi, bai zame ba, sai ga Isma'ila, yana biye da ubansa. Ya je ya raɗa masa abin da ya gaya wa uwarsa. Abin nufin Allah kuma, sai Isma'ila ya ba Shaiɗan amsa daidai yadda uwar sa Hajara ta ba shi. Daga nan ya yi gaba, shi Shaiɗan, sai

wurin Annabi Ibrahim, yana ce masa mafarkin nan fa da ya yi, ba naƙaltawar Allah ba ne, Shaiɗan ne ya naƙalta masa abin da ya gani don ya kashe ɗansa, daga baya ya yi da-na-sani. Annabi Ibrahim ya yi masa tsawa ya la'ance shi. Ya ɗauki dutse ya jefe shi. Wannan shi ne dalilin da jifar Shaiɗan ya zama sunna ga alhazai a Mina, kamar yadda Sa'ayi tsakanin Safa da Marwa ya zama.

Shaiɗan ya yi baya, yana mai baƙin ciki. Ya ga bai ci riba ba ga uwa, balle ga ɗa, balle ga uba. Sa'an nan Annabi Ibrahim ya labarta wa ɗansa al'amarin duka. Ya ce masa, "Ya ɗana, na gani a cikin barci ina layya da kai. To, dubi, ina ra'ayinka ?" Sai Annabi Isma'ila, amincin Allah ya tabbata a gare shi, ya amsa, ya ce, "Ya ubana, aikata abin da aka umurce ka. Za ka same ni cikin masu haƙuri in Allah ya so. Ba ni saɓa maka."

A cikin wata ƙissa, an ce, sa'ad da Annabi Isma'ila zai kwanta, ubansa ya yi layya da shi, sai ya ce masa, 'Ya baba, in za ka yanka ni, ɗaɗɗaure mini hannuwa don kada ɗigon jinina ya taɓa ka, ladana ya ragu. Kuma in za ka kwantad da ni, za ka yanka, to, ka mai da kaina ƙasa, kada ka bar fuskata sama tana dubanka don kada tausayina ya kama ka, har wani abu ya shiga tsakanin umurnin Ubangijinka da biyayyarka ga umurninsa. Kuma bayan ka yanka ni, in ka ga kamar in ka mayad da rigata ga uwata, zai sa ta fid da rai gare ni, to, ka mayar mata."

Annabi Ibrahim ya karɓa, ya ce, "Madalla da wannan taimako naka, ya dan gana, ga umurnin Ubangiji ka ke." Shi ke nan Annabi Isma'ila ya kwanta, Annabi Ibrahim ya kwantad da shi, ya ɗauko wuƙa zai yanka, sai ya ji daga bisa tsauni an yi kira a gare shi aka ce masa, "Ya Ibrahima, ka gaskata mafarki. Za mu fanshi Isma'ila da rago babba." Sai ga rago, Annabi Ibrahim ya yanka shi maimakon ɗansa. Ka ji iyakar ƙarshen wannan ƙissa ta wannan ɗa mai tsananin biyayya ga uba.

Ana nan, ana nan, sai kuma Maɗaukakin Sarki Allah ya nufi uwargidar Hajara ita kuma ta haihu a can gida, aka raɗa wa yaro suna Ishaƙa. Wannan kuma shi ne Annabi Ishaƙa da ku ke jin labarinsa, kun ga watau ashe ƙane ya ke ga Annabi Isma'ila.

## Ɗakin Ka'aba

TO, wannan zuriya ta Annabi Isma'ila, wadda kuka karanta tarihinta yanzu, daga cikinta ne Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, zai fito.

Bari mu biyo silalin tarihimmu sannu mu gani.

To, a Birnin Makka nan ne Ka'aba ta ke, Ɗakin Allah Mai Tsarki. A jikin Ka'aba ne ke da wani dutse mai tsarki mashahuri, wanda a ke kira Hajral Aswad. Tun da aka halicci duniya, wannan ɗaki na Ka'aba, shi ne ɗaki na farko, wanda Maɗauka. kin Sarki Allah ya nufi a bauta masa a ciki. Malaman tarihi na duniya duka, sun yi lissafi, sun yi lissafi, amma ba su iya gane shekarar da aka sa harsashi na farko na ginin wannan ɗaki na Ka'aba ba. Shi dai kawai an sani cewa tun tun tun tuni akwai Ɗakin Ka'aba a-duniya.

Tun tun kafin a ha fi Annabi Ibrahim, amincin Allah ya tabbata a gare shi, ginin Ka'aba na asalin asali ya rushe a lokacin Ruwan Ɗufana, wanda kuka karanta labarinsa a baya, cikin labarin Annabi Nuhu, amincin Allah ya tabbata a gare shi. Sai wurin da ya ke kawai 'yan Adam suka riƙe. Da Annabi Ibrahim fa ya bayyana, ya haifi Annabi Isma'ila, wanda Allah ya nufa da ya fara kawo shi a wannan karkara. Da Allah ya aikata abin da ya aikata, sai yaro ya rayu lafiya. Mun gaya muku da ma ko yaushe Annabi Ibrahim ya kan zo ya kewaya su. To, da fa yaro ya girma, sai Ubangiji Allah ya hori Annabi Ibrahim, tare da shi Annabi Isma'ila da umurnin su sake ta da ɗakin nan na Ka'aba, a wurin nan nasa da ya ke na asalin asali. Maɗaukakin Sarki Allah, shi ya aiko Mala'ika Jibirilu, ya nuna musu wannan wuri na asali. Kuma ya nuna musu inda Hajiral Aswad ya ke. An ce sa'ad da Annabi Ibrahim, da Annabi Isma-ila, su ke gina Ɗakin Ka'aba, sai Annabi Ibrahim, amincin Allah ya tabbata a gare shi, ya umurci ɗan da ya kawo masa wannan dutsen baƙi. Ya kawo.. Annabi Ibrahim ya kafa shi a bangon ɗakin. To, wannan dutse shi ne Hajral Awad, Baƙin Dutse na jikin Ɗakin Ka'aba, wanda alhazai ke sumbanta a yanzu, a cikin ayyukan hajji. Wannan Baƙin Dutse ana sumbantarsa ne kawai don an ga Annabi ya sumbance shi. Domin gudun ma kada mutane su maida sumbartarsa wani abu dabam,

shi ya sa da Halifa Sayyadina Umar ya zo zai sumɓance shi sai ya ce, "Ni na san kai dutse ne. Ba ka cuta, ba ka amfani. Ba don na ga Annabi ya sumɓance ka ba, ba abin da zai sa ni sumɓantarka." Sa'ad da Annabi Ibrahim ke gini, da gini ya yi nisa, ya hau kan wani dutse. To, shi kuma wannan dutse, yana nan a Makka yanzu. Shi a ke kira Maƙama Ibrahim.

To, da suka gama ginin, sai Maɗaukakin Sarki Allah ya umurci Annabi Ibrahim da ya yi kira ga al'umma, su ziyarci wannan ɗaki na Ka'aba. Sabo da haka wanda duk Allah ya nufa da zuwa hajji, watau ya karɓa kira ke nan na Annabi Ibrahim, amincin Allah ya tabbata a gare shi. Amma fa kada mu zaci kamar cewa wannan gini na Ɗakin Ka'aba, da alhazai suka sani a yanzu, shi ne ginin da Annabi Ibrahim da Annabi Isma'ila suka yi. A'a, a'a, zamani tafe ya ke tare da sake ginin Ɗakin Ka'aba, domin a da, ruwa ya kan kwashe shi.. Ko a zamanin bayyanar musulunci, an sake gina shi, ba ma sau ɗaya ba. Sai dai fa ko ruwa ya yi malali, kagon kawai ya ke rushewa. Wurin kam na asalin asali wanda Sarki Allah ya kiyaye, har ya nuna wa Annabi Ibrahim, amincin Allah ta tabbata a gare shi, ya shaya, shi ne har yanzu.

Tun sa'an nan kuwa wurin ya ke abin girmamawa, har yanzu. Kafin ma bayyanar musulunci har ibada mutanen Makka su ke yi a wurin. Amma sai dai ba ibadar Allah ba, ibadar gumaka. Tun sa'an nan, zamanin jahiliyya, mutane ke taruwa wurin don ibada irin tasu. Ko a lokacin, ba Makka kaɗai ba, ko da karkarar kwaye da it ana riƙe da ita ne da daraja. Ba a yaƙi da duk wanda ya sanya ƙafa ciki, ko da farauta ba a yi a wurin.

## Kiswa

A YANZU Ɗakin Ka'aba, gini ne-mai kyaun gaske. Kusurwoyi huɗu. A ko wane lokaci, Ɗakin Ka'aba riga gare shi. Ita kan sanya ya ƙara ƙawatuwa, kuma ya ƙara kwarjini. Mun sami labari, daga malaman tarihi, cewa wani sarki na ƙasar Yaman, shi ne ya fara yi wa Ɗakin Ka'aba riga, Kiswa.

A zamanin yanzu kuwa, ƙasar Masar, ita ke riƙe da wannan daraja, ta yi masa riga. Ko wace shekara sabuwa a ke ɗinkowa, ta ƙyalle baƙi, a ƙawata ta da ayoyin Alƙur'ani, rubutun ya riƙa ƙalli.

To. tun zamanin da, duk cikin kabilun Larabawa, wadda ta yi ƙarfi, har ta zama ita ke riƙe da wannan ɗaki na Ka'aba, to, bukatarta ta biya. Saboda haka, darajar riƙon 'Dakin Ka'aba sai ya zama babbar sarauta, kabila mai ƙarfi ita ke ɗauka. Ta haka, har aka sami lokacin da riƙonta ya fita daga hannun masu ita, zuriyar Annabi Isma'ila, ɗan Annabi Ibrahim.

Babban al'amari na biyu, abin ruwaitowa, wanda ya gudana tsakanin Annabi Ibrahim da ɗan nan nasa Annabi Isma'ila, shi ne kuwa wannan. Ko da muka nuna yadda Annabi Ibrahim ya kawo matarsa da ɗansa a wannan karkara ta Makka, bai daina kewayo su ba loto loto. Ta haka, a cikin nufin Allah yaro ya rayu, har ya tasa.

## Kusayyi

SHI Annabi Ibrahim da mu ke ba da labarinsa, shi ne muka ce ya haifi Annabi Isma'ila. Kada mu manta. To, a cikin zuriyar Annabi Isma'ila aka sami wani tauraro, wai shi Kusayyi. Shi kuwa hula biyar ke tsakaninsa da Annabi Muhammadu. Wannan tarihi ya nuna mana cewa Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana cikin zuriyar tsatson Annabi Ibrahim ne, uban Annabi Isma'ila, wanda a cikin zuriyarsa ne aka sami Kusayyi.

Shi wannan tauraro, Kusayyi, sunansa ya yi tambari sosai a cikin tsatson Annabi Isma'ila. Mulkinsa shi ne ya zama kamar bismilla ga tarihin Kuraishawa. Shi ne ya kawo sabon shiri na mulkin Makka da na tsaron 'Dakin Ka'aba. Shi ne ya shirya yadda za a ba alhazai abinci, da ruwa in sun zo hajji, irin nasu na lokacin. Shi ne ya shirya al'amarin riƙon mabuɗin Ka'aba. Shi ne ya shirya rundunar soja da yadda za a yi hukuncin jinaye. Shi ne ya kuma gina majalisa babba, wadda aka riƙa kira Darun Nadwa. Nan a ke shari'a, kuma a nan manyan gari ke taruwa su yi shawara. Yanzu wurin yana nan cikin Masallacin Makka. Shi a ke kira a yanzu, Masallacin Hanafi. Hasali dai ko da Kusayyi ya mutu, shirinsa na mulki bai mutu ba!

Wannan duk ya auku a lokacin jahiliyya ne. Watau kafin bayyanar Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

## Hashim

BAYAN Kusayyi sai jikansa Hashim, watau ɗan Abdul Manafi. Shi kuwa da ya hau gado, a hannunsa fa ne Kuraishawa suka miƙa tilliken mulki. Ga shi da ma Allah ya yi shi mutum ne mai himma ga alheri. Da waɗannan halaye nasa ya bi da ƙasar Makka kaf. Riƙon mabuɗin Ka'aba ya zauna hannunsu, su Kuraishawa, ya zama sarautarsu ta gado.

## Abdul Muɗɗalabi

MALAMAN tarihi sun lissafta, sun ce bayan haihuwar Annabi Isa, amincin Allah ta tabbata a gare shi, da shekara kamar arbaminya ne, aka haifi Kusayyi. Shi kuma shi ne ya haifi Abdul Manafi. Abdu Manafi ya haifi Hashim. Saboda wannan Hashim wanda mu ke maganarsa a yanzu, a ke kiran dangin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata gare shi, Bani Hashim To. shi Hashim kuma shi ya haifi Abdul Muɗɗalabi. Shi kuma Abdul Muɗɗalabi ya haifi Abdullahi, watau mahaifin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

To, tun kafin wannan lokacin kuwa, Rijiyar Zamzam ta ɓata. Ga shi duk an san akwai ta. Amma ƙasa ta toshe bakin. Saboda shekarun sun yi yawa, har ba a iya sanin ainihin inda ta ke.

Da hawan Abdul Muɗɗalabi gado, sai ya yi niyya, cewa shi kuwa da yardar Allah, sai ya gane bakin rijiyan nan ta Zamzam. Ya shiga biɗa. Ya yi, ya yi, amma bai gamu da nasara ba. Sa'an nan, da ya ga dai ba dama, sai ya mai da al'amarin duk ga mai shi, Maɗaukakin Sarki Allah. Ya yi roƙo a gare shi don ya nuna masa wannan wuri. Ubangiji kuwa ya karɓi roƙonsa, ya nufe shi da gane bakin wannan rijiya. Aka shiga aiki, aka sake tone ta, ruwa ya wadaci karkara. Jama'a suka yi ta gamuwa, domin albarkar sunanta. Wannan al'amari fa, shi ne ya kawo wa Abdul Muɗɗalabi martaba mai yawa ga Kuraishawa.

## Abdullahi, Tsohon Annabi Muhammadu

A ZAMANIN da Sarki Abdul Muɗɗalabi ke wannan fama da abokan gaba, ɗansa ɗaya ne tak. Saboda haka ya yi rantsuwar cewa da Sarki Allah zai ba shi 'ya'ya goma, maza, duk kuwa su rayu, har su balaga a zamaninsa, to, shi kuwa da ya yi layya da guda. Allah da shi ke mai jin roƙo ne, sai ya karɓi

roƙonsa, ya nuƙe shi da samun 'ya'ya goma duk maza. Da suka girma yadda ya yi alkawari, sai shi Abdul Muɗɗalabi ya ɗauke su duka zuwa ga 'Ɗakin Ka'aba ya ce wa limamin ɗakin ya buga musu ƙuri'a ya gani, ko a kan wa ta faɗa cikin 'ya'yan nan nasa, to, shi Allah ke so a yanka.

Aka buga, sai ƙuri'a ta faɗa a kan Abdullahi, mowan Abdul Muɗɗalabi. Shi kuwa wannan ɗa Abdullahi shi ne Allah ya nufa zai zama uban Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Abdul Muɗɗalabi ya cika da baƙin cikin abin da wannan ƙuri'a ta nuna. Amma saboda tsananin cika alkawarin Larabawa, sai ya ja yaro, ya nufi Mumbarin 'Ɗakin Ka'aba don ya cika alkawarinsa. 'Yarsa guda, shi Abdul Muɗɗalabi, sai ta zabura, ta rungume shi, tana ta kuka. Daga nan sai dattijan Larabawa suka ba da shawara, suka ce to, a tafi wajen wata mace a Yathrib, don ta warware wannan rikici. To, ita ce ta ba su shawarar su yi ƙuri'a tsakaninsa da raƙummai gwargwadon yawan diyya a ƙasarsu, tsakanin Abdullahi da raƙuma goma. In ƙuri'a ta faɗa kan Abdullahi. to, sai a ƙara raƙumi goma a kai, a sake wata ƙuri'a, idan kuwa ta faɗa kan raƙuma goma, to, Allah ya yarda ke nan, raƙuman nan su zama fansa ga ran Abdullahi.

Aka ce, "E, hakanan ne, hakanan ne." Aka sake bugawa. Abin mamaki, sai kuma ƙuri'a ta sake faɗawa a kan Abdullahi Abu fa ya ruɗe! Jama'a suka ce, watau Allah bai yarda ba ke nan, raƙuma goma su zama fansar ransa. A da kuwa raƙuma goma su ne fansar rai ga kabilar Kuraishawa. To, tun da a wannan karo, Allah bai yarda ba, ba sai a ƙara masa ba. Abdul Muɗɗalabi ya ce ya ƙara raƙuma goma bisa goma ta farko, a buga. Aka buga ƙuri'a ta faɗa kan Abdullahi.

A'a, a'uzubillahi! Abdul Muɗɗalabi ya ƙara goma, suka zama raƙuma talatin. Aka buga, Maɗaukakin Sarki Allah ya ƙi sallamawa. Kaɗa dai mu tsai da ku, Sarki Abdul Muɗɗalabi ya yi ta ƙara raƙuma goma goma, amma ko yaushe aka buga, sai ƙuri'a ta nuna cewa Allah bai yarda ba, shi dai ran Abdullahi ya ke so. Hasali dai sau tara ana bugawa, ƙuri'a na faɗawa a kan Abdullahi! Sai a bugawa ta goma, sa'an nan Sarki Allah ya yarda, ƙuri'a ta faɗa kan raƙuma. Watau Abdul Muɗɗalabi ya ba da raƙuma ɗari suka zama fansar ran [illegible]

...n nan kuma diyyar rai, a cikin kabilar Kuraishawa ta tashi daga rakuma ...ma, ta koma rakuma dari. Watau a ilhami rakuma dari su Allah ya yarda su zama diyyar ran Bakuraishe. Sai addinin musulunci ya tabbatar da shi ya zama diyyar mutum.

Shi ke nan, yaron nan Abdullahi ya girma, ya ko zama shahararre a cikin Kuraishawa, domin tsananin ibadarsa da halayensa kyawawa.

## Zamanin Jahiliyya

ZAMANIN jahiliyya shi ne zamani na kafin bayyanar musulunci. Labarin wannan zamani kamar shimfida ne ga tarihin musulunci. A lokacin addinin Annabi Ibrahim da na Annabi Isma'ila, na babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah, kuma Allah ba ya da abokin tarayya duk an gOce masa. Tsawon zamani ya sanya jama'a sun karkace hanya, sun mai da gumaka su ne abin bautawa, sabanin Madaukakin Sarki Allah! Ka'aba, 'Dakin Allah mai tsarki, wanda da aka ajiye domin bauta wa Madaukakin Sarki Allah, yanzu ya koma gunki, dakin tsafi. Masu tarihi sun ce a lokacin nan a cikin 'Dakin Ka'aba din kansa, akwai gumaka 360. Watau ko wace rana akwai gunkinta, har shekara ta kewayo. Kuma ko wace kabila da nata gunkin, abin bauta wa. Abin mamaki, sai tsatso da Annabi zai fito, su ne kawai dayansu bai taba bauta wa gunki ba. Wani babban mutum, mai tsaron 'Dakin Ka'aba wanda a lokacin a ke kira Amru Ibn Luhayyi, shi ne ya fara sawo gunki daga kasar Sham, Syria, ya kawo Makka. Ya ajiye a kofar Ka'aba, ya sanya mutane suka fara sujada a gare shi, suna bauta masa. Daga nan kabilu da yawa kuma sai suka je suka sassawo nasu. Hasali dai daga nan bauta wa gumaka ya tsira a kasar Makka, ya yi karfi har ya dushe imani ga Madaukakin Sarki Allah, imani wanda Annabi Ibrahim, da dansa Annabi Isma'ila da dukan Annabawa da suka wuce, suka isar.

Sai dai fa a lura, ko a lokacin Larabawan nan da mu ke zance sun san Allah. Amma a jahilcinsu, wai Allah ya faye nisa, har rokon dan Adam ba ya iya isa gare shi, sai ya kama kafar wani. Shi ya sa suka ajiye gumaka don su kama kafarsu, su fuskantad da su ga Madaukakin Sarki Allah.

Abin mamaki kuma, akwai wadansu Larabawa shiryayyu. Ashe su ne za su zama mafitar Annabin shiriya. Kun ga tun asali, da sauran jama'a suka karkace, su wadannan zuciyarsu ba ta bi karkata ba. Ko da yaushe, su bida su ke yi Allah ya nuna musu gaskiya, kamar yadda Annabi Ibrahim, da Annabi Isma'ila suka nuna, su kuwa su bi. Har wa yau kuma ban da wadannan, akwai Kirista, akwai Yahudawa. Fadar Kiristanci ta ƙasar Makka a lokacin, ana kiranta Najiran. Fadar Yahudawanci kuwa a ƙasar Makka a lokacin Birnin Yasriba, watau Madina.

### Al'adu

A LOKACIN nan na jahiliyya, Larabawan ƙasar Makka suna ganin mata kamar wata masifa ce Allah ya aiko a duniya. Wanda ya ji gudar haihuwa a gidansa, in ya tamaya aka ce masa 'ya mace aka samu sai ya ji kamar wata masifa ke nan Allah ya saukar masa. Hasali dai har a kan binne 'ya mace da rai wai a huta da masifarta. Su dai mata a lokacin ga su nan dai ne. Sai mutum ya auri iyakar yadda ya ke so, kuma ya saki wadanda ba ya so, sa'ad da ba ya sonsu. Duk da haka kuwa su matan Larabawa na lokacin cike su ke da mutunci da biyayya. Sabo da haka ko za a bizne 'ya mace, don tsananin biyayya ba ta ɓata rai, balle ta yi raki.

Su kuwa mazan Larabawa, na wannan lokaci, giya ita ce kamar ti a gare su, caca kuwa, da fashi da ƙwace, su ne wasanninsu. To, wadanda suka mai da giya kamar ti ina ka ga aikin hankali ga mashayi ? Sabo da haka ba su mai da kisan kai wani abu ba. 'Yar magana kadan in ta tashi, sai ka ga fada. Daga fada sai yaƙi ya tashi. Shi ke nan an sami dalilin kisan juna. Hasali dai sabo da rudewar wannan lokaci ne har Larabawa ke kiran zamanin da suna Zamanin Jahiliyya.

### Kyawawan Halaye Na Larabawan Zamanin Jahiliyya

KOda muka yi wannan bayani, na munanan halayen jahiliyya, ya kamata kowa ya sani cewa ko can a, a lokacin jahiliyyar, Larabawa ba ɓoye su ke ba cikin kabilu na duniya. Ko can da Larabawa sanannu ne, tum ba a wajen halaye biyu ba, biyayya ga na gaba da gaskiya ga abin da zai fito baki. Idan har Balarabe, ya daukar maka alkawari, ko ya dauki amanarka, ka tabbata da ya karya alkawarin nan, ko ya ci amanan nan taka, gara ya je kabari.

A wajen liyafa kuma. Balarabe a lokacin, sai ka zaci kamar sabo da ya yi liyafa ga baƙi kawai ya ke zaune a duniya. Da bako da ɗanuwa ga Balarabe na lokacin kusan duk matsayinsu ɗaya. In ka baƙunci Balarabe, shi kuwa ya si da ransa domin-ka, wannan bai sayi wuri ba! In da Balarabe na lokacin zai sami lomar tuwo ɗaya tak, ya ɗaga ta zai kai baki, sa'an nan a ce masa ga baƙo, to, ka tabbata, yana iya maido ta ya raba biyu, baƙonsa ya sami rabi.

Abin ma maraki, duk wannan hali abin yabo, Larabawa suna girma ne su gansu da shi. Ba karantawa su ke yi daga waɗansu littattafai ba, ba kuwa koya musu ba a ke yi a wata makaranta. Hasali ma a lokacin ai rubutu sunansa kawai ya shahara, amma ba shi kansa ba.

A wajen ilmi, shaihunan malamai a cikin Larabawa, na lokacin jahiliyya, -su ne mawaƙa. Yadda Shaihu Wane da Shaihu Wane, su ke ababan girmamawa a ƙasashe, haka mawa-ƙi Wane, su ke ababan girmamawa a ƙasar Larabawa a zamanin jahiliyya. A kasuwar Ukaza, kusa da Makka, har a kan yi taron gwanayen mawaƙa. Su zo daga ƙasa ƙasa a yi gasar waƙa. Wanda waƙarsa ta ci sai a rubuta ta da tawwadar zinari a rataya Ɗakin Ka'aba. A wajen iya hardace abu kuwa, Larabawa na zamanin jahiliyya sai dai a bi bayansu, amma ba a wuce gabansu ba.

## Niyyar Rushe Ɗakin Ka'aba

ABAYA, mun yiwo tsalle a kan Abdul Muɗɗalabi. Shi ne kamar sarkin Makka a wannan lokaci. Mun tsaya a kan labarin haihuwar Abdullahi, da ƙuri'ar da aka yi a kan ransa.

To, ga abin da kowa ya fahinta dai a yanzu lalle ne Sarki Abdul Muɗɗalabi ya isa zakara a ƙasar Makka, a wannan zama-ni nasa.

Ga shi dai da farko ya fito daga cikin farar kabilan nan da Larabawa ke girmamawa tun can da, kabilar Kuraishawa. Ga shi kuma ta irin halinsa da kuka karanta, lalle ya isa a bambanta shi da sauran sarakuna.

A wannan zamani na Abdul Muɗɗalabi, ƙasar Yaman tana ƙarƙashin wani sarki ne da a ke kira Abraha. Shi kuwa a loka-cin kamar basarake ne na wani mashahurin sarki na Habasha (Abyssinia). Shi wannan sarki na Habasha Kirista ne. Ya

kasaita har ba abin da ya ke so kamar ya hana kowa cara a gabansa. Ya gina wata babbar majami'a mai ƙayen kyau, a babban birninsa San'a. Ya gina ta da burin wai ya ɗauke hankalin Larabawa daga hajjatar 'Dakin Ka'aba.

Ganin haka ya sai Larabawa suka husata, har wata rana wadansu Larabawa suka je, don son ƙasarsu suka ɓata masa majami'a tasa da ƙazanta. Wannan abu shi ya husata shi, ya yi niyya shi ma sai ya rama. Ya yi niyya shi zuwa zai yi ya rushe 'Dakin Ka'aba baki ɗaya, wai duk a huta. Dubi, saboda tsananin son ƙasa, yadda waɗannan Larabawa suka tafi takanas garin mutane suka aikata wannan.

Shi ke nan, sai ya tashi, ya tinkaro da ɗimbin yaƙinsa, har ɗa giwaye ciki! Ya zo ya kafa sansani kusa da Makka. A nan ya ci karo da garken raƙuman Abdul Muɗɗalabi, ya kwashe su.

Da farko, kamar Larabawa za su fita a gamu, don su tsare 'Dakin Ka'aba. Amma daga baya sai suka tsorata, suka fasa, sun ga am fi su ƙarfi! Suka dai zaɓi sarkinsu, Abdul Muɗɗalabi suka ce ya je ya bidi sulhu ga sarkin yaƙin nan Abraha. Mun gaya muku da ma kabilar duk da ta yi ƙarfin ta riƙe 'Dakin Ka'aba, ita ce sarki. A yanzu kuwa ga riƙonsa ya koma hannun kabilar Kuraishawa, Bani Hashim. Saboda haka Abdul Muɗɗalabi, shugabansu, shi ne kamar sarkin Makka a lokacin.

To, da Abraha ya gan shi tafe, da niyyar salama, sai ya tarye shi don ya ji abin da ke tafe da shi. Shi ke nan, ba abin da ya fito bakin Abdul Muɗɗalabi sai ya ce, "Ina so ka mayar mini da raƙumana metan da kuka kama.

Wannan jawabi na Sarki Abdul Muɗɗalabi ya ba Sarki Abraha mamaki, ya ce, "Yaya da zuwanka ba ka yi mini wata magana ba, sai ta raƙumanka da na kama. Ba ka ce mini kome ba game da 'Dakin Ka'aba, ɗakin iyayenka da kakanninka na ibada, wanda na zo zan rushe?"

Abdul Muɗɗalabi ya karɓa ya ce, "Gaskiya ne, amma ni, ni ne ubangijin raƙummana. 'Dakin Ka'aba kuwa shi yana da nasa Ubangiji dabam. Shi kuwa ne zai tsare shi."

Abraha ya hura hanci, ya ce, "Ubangijin 'Dakin Ka'aba ba za iya tsare shi daga gare ni." Abdul Muɗɗalabi ya karɓa ya ce, "Wannan kuma kai da shi. Ni dai ba ni raƙumana."

Abraha ya ba shi rakumansa, Abdul Mudđalabi ya juyo gida. Bai zame ba sai Đakin Ka'aba. Ya je ya roki Ubangiji a kan ya tsare đakin Mai Tsarki da kansa. Watau shi al'amarin ya fi karfinsa.

Allahu Akbar, Mađaukakin Sarki Allah kuwa ya karɓi addu'a, ya tsare 'Dakinsa na Ka'aba da kansa domin kansa. Allah ya tsare đakin, tsarewa irin wadda har duniya ta tashi ba za a manta da ita ba. Domin kuwa ga yadda abin ya auku. Da rundunan nan ta Sarki Abraha ta tinkaro Makka, da niyyar ta rushe 'Dakin Ka'aba, sai Mađaukakin Sarkin Allah ya aiko da tasa rundunar. Kana zato waçe irin runduna ya aiko da ita? Runduna ce ta 'yan tsuntsaye, ita Sarki Allah ya aiko, da umurnin ta zo ta halaka rundunar Sarki Abraha mai giwaye. Haka kuwa aka yi. Ko wane đan tsuntsu ya taso fir da 'yar tsakuwa a bakinsa, suka yi ta jifan rundunan nan ta Sarki Abraha da 'yan duwatsun nan. Ta haka, da karfin ikon Mađaukakin Sarki Allah, tsuntsayen nan suka halaka rundunan nan! Allah gwani!

### Shekarar Giwaye

LABARIN wannan yaki, shi ne Sarki Allah ya gaya wa Annabi Muhammadu shi da kansa, sa'ad da ya ɓayyana. Ya gaya masa shi cikin Alkur'aninsa mai girma. Surar 'Alam Tara Kaifa, ita ta zo da wannan labari.

To, wannan shekara fa har Larabawa na lissafi da ita, suna kiranta shekarar giwaye. A cikinta ne kuwa aka haifi Aflalul Mursalina, Shugabammu Muhammadu, Mabuđin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici!

To, sa'ad da fa Larabawa suka ga abin da Mađaukakin Sarki Allah ya aikata da rundunan nan ta Sarkin Abraha, duk sai suka kara sanya daraja ga wannan kabila ta Kuraishi. Suka rika cewa lalle Kuraishawa al'amarinsu da magana, kabilar Allah ce. Dubi yadda Allah ya yi musu yaki, har ya tsare su daga abokan gabansu!

Kai, ya kamata mu dawo hakanan daga wannan dogon ratse da muka yi. Wannan shimfiđa ta tarihi ta isa ta sanya kowa a cikin kogin tunani na Mađaukakin daraja wanda ke tare da wannan zuriya ta Annabi Isma'ila đan Annabi Ibrahim,

da Maɗaukakin daraja-wanda ke tare da wannan ƙasa ta Makka wadda Allah ya shirya za ta zama mahaifa ga Imamul Mursalina Shugabammu Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

## Auren Mahaifan Annabi

TO, a lokacin da Abdul Muɗɗalabi ya ga ya kamata ya yi wa Abdullahi aure, sai Maɗaukakin Sarki Allah ya nufe shi da zaɓen wata wai ita Amina, 'yar Wahabi. Su kuwa gidansu babban gida ne, mai daraja. Su ne shugabannin Banu Zahratu. Abdul Muɗɗalabi ya ga ita ce za ta dace da Abdullahi. Ran nan sai Abdul Muɗɗalabi ya fita, har ya je garin Banu Zahratu biɗar wa ɗansa aure. Ya biɗa aka ba shi, ya ba ɗansa. Aka yi aure irin na manyan gidaje aka gama.

Shi ke nan, Abdullahi ya yi zamansa tare da matarsa Aminatu. Bai daɗe ƙwarai da ita ba, sai Allah ya nufe ta da samun ciki. Watau cikin Annabi Muhammadu ke nan, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Da ta sami ciki, sai shi Abdullahi ya yi shiri ya fita zuwa ƙasar Sham domin fatauci yadda ya saba, ya bar Aminatu ga tsohonsa.

Da suka je ƙasar Sham suka ƙare fataucinsu, suka juyo gida. Suna zuwa wajen ƙasar Madina, sai shi Abdullahi ya dakata ga danginsa na nono, don ya ɗan huta, a yi magama ke nan, a ji daɗin shiga Makka. Amma, Allahu Akbar, a nan sai rashin lafiya ya same shi, ya turo ayarinsu, ya ce su su iso gida, Makka.

Da suka zo suka ba da labarin Abdullahi na can ba ya lafiya sai mahaifinsa, Abdul Muɗɗalabi ya ta da Haris, ɗansa guda, ya ce ya je ya zo da shi gida. Haris na isa Madina sai ya sami labari cewa Abdullahi ya rasu ! Ya dawo gida cike da baƙin ciki, ya ba da labari. Abdul Muɗɗalabi da Aminatu suka yi baƙin ciki mai tsanani.

To, ana nan kwana tashi, sai ran nan Aminatu ta haihu. Ta haifi shugabammu Muhammadu. Mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici. Annabi Muhammadu ya fito mutum. Amma fa fiyayyen dukan mutane! Ya fito duniya idonsa a buɗe. Cibiyarsa a yanke, kana ga kaci ya. Ka ji kuma wata aya cikin ayoyin Maɗaukakin Sarki

Allah. Irin waɗannan ayoyi, da mu'ujizoji, suna da yawa cikin labarin zaman Annabi a duniya. Sai dai mu taƙaita kawai don taƙaitar ilmimmu.

Da Amina ta haihu, sai aka aika'Dakin Ka'aba, aka ce a je a gaya wa Abdul Muɗɗalabi, domin a lokacin yana can. Daga can ya zaburo ya nufo gida cike da farin ciki. Ya zo ya ɗauki jariri, jikansa, ya yi waje da shi. Bai zame ba sai'Dakin Ka'aba. A can Allah ya nufe shi da raɗa wa jaririn suna Muhammadu, watau da hausa "Abin Yabo."

Abin mamaki, wannan suna sai ya zama kamar baƙon suna ga Larabawa. Domin kuwa da su ba su sanya wa 'ya'ya suna haka. Amma kuma an san suna ne, mai ma'ana kuwa. Ashe, Sarki Allah ya mantad da su wannan suna ne. Yana jira ya aiko da Abin Yabo, ya zo ya karɓi wannan suna da ya dace da shi Muhammadu Abin-Yabo !

Wannan rana da aka haifi Annabi, ranar Litinin ce, sha biyu ga watan Rabi'u Awwal. A cikin wannan shekara ta giwaye. Malaman tarihi sun lissafta, sun ce watau ya kama wajen ran 20 ke nan ga watan Afril, Shugabammu, Annabi Isa, amincin Allah ya tabbata a gare shi, sa'an nan yana da shekara wajen 571 da haihuwa :

**Maraba Da Shugaba**

Maraba da kai Muhammadu ɗan Amina.
Maraba da shugaban duka Annabawa.
Muhammadu, sabulu mai wanke dauɗa,
Muhammadu, magani mai warke kowa.
Muna zuba godiya ga Ubangijimmu,
Da ya aiko ka domin kyautatawa.
Idan ganga ta sa wasu raira waƙa,
Ni yabonka ka sa ni zarya da rausayawa.
Muhammadu, sonka addini zakiyyi,
Wanda duk ke sonka ya wuce taɓukewa.
Mu tashi mu tsaitsaya don girmamawa,
Ga Annabi, shugaban duka Annabawa.
Gaba ɗaya mui salati gun Muhamman,
Mabuɗin duk abin da ka rurrufewa.
Rabbi salli ala Muhammadu, shugabammu,
Muna bayanka ranar tambayawa.
Muhammadu ya taho domin bayani,
Ya miƙe abin da da ka rikirkicewa.
Da kalmar gaskiya ya taho gare mu,
Ya taimaki gaskiyar da ka karkacewa.
Muhammadu yai kira mai so ya karɓa,
Mu kā samu cikin waɗanda ka gaskatawa.
Ka shaida mun yi imani gare ka,
Rabbi shi ɗai, kai cikon duka Annabawa.
Tamat wa bi hamdihi mun i da wannan,
Da ikon Rabbu Sarki mai iyawa.
A nan zam bar ku littafi na fari,
Allah ka ban ikon da zan iya ƙarasawa.
Ina daɗa godiya, Alhamdu lillah,
Allah, ka gafarce mu domin kuskurewa.

## SALAMU ALAIKUM

GODIYA ta tabbata ga Maɗaukakin Sarki Allah, wanda a cikin ikonsa da yardarsa, da baiwarsa, muka sami damar gama juzu'i na farko cikin wannan tarihi na Annabi, har kuma ga shi ya ba mu ikon gama wannan na biyu. Ya Allah, muna roƙonka, cikin rahamarka, ka nufe mu da ganin mun cika sauran wannan buri namu.

Tun a juzu'i na farko, muka nuna cewa akwai littattafai da dama, a cikin harsuna iri iri, waɗanda mutanen yanzu suka yi ƙoƙari suka rubuta, a kan wannan tarihi na shugabammu Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Har a nan ƙasar Arewa sau da dama, ka kan ji makafi ko musakai, suna bara da wannan tarihi na Annabi. Sai dai abin baƙin ciki, shi ne da dama daga cikin waɗansu irin littattafan can, da kuma irin makafin nan, sai ka ji bayaninsu ba ya bin hanya wadda za ta ba da sahihiyar surar mutumin da su ke ƙoƙarin bayyanawa, watau shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici! Annabin aminci, wanda aiko shi duniya ta zama babbar rahama ga 'yan Adam.

Maimakon ka ji tarihi, wanda zai bayyana irin wannan mutum, sai ka ji ana faɗa waɗansu maganganu, waɗanda ba a ɗebo su ba daga sahihin kogi na wannan tarihi. Misali, sai ka ji masu bara na cewa, "A Yaƙin Badar, sai da Sayyidina Ali, ya yi kogi da jinin Kafirai!" Wannan ƙarya ne.

Cikin sahihan littattafan larabci, waɗanda aka rubuta su tun shekara wajen dubu, a kan wannan tarihi na Annabi, ba ɗayan da ya ce haka. Irin wannan tarihi na kuskure, wanda ke ƙirƙira daga Kitabur Ra'asi, aibinsa ya fi gyaransa yawa. Domin kuwa ta haka ne yaro ya kan girma yana tunanin Annabi, da sahabbansa a kan waɗansu irin jarumawa ne aka yi a duniya, waɗanda suka yi ta kisan jama'a! Allahu Akbar.

Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata gare shi, shi da sahabbansa, yardar Allah ta tabbata a gare su, ba a aiko shi duniya da rundunar kisan jama'a ba. Annabi an aiko shi duniya ne, domin ya kawo hanyar zama na aminci, da salama, da lafiya, da zama lafiya, ga 'yan Adam. Don haka ma ne a ke kiransa Nabiyun Rahamati, watau Annabin Rahama

Sabo da haka, burimmu da shirya wadannan littattafai, shi ne mu gina sahihiyar tarbiyya a zukatan yara. Su karanci halaye irin wadanda za su yi kwaikwayo da su. Kuma mu goge irin wadancan kuskure, mu sake rubuta tarihin Annabi sahihi, a cikin zukatan yara, da mata, da kamarmu wadanda ba su sami damar yin karatu ba mai yawa. Mun sani wannan ba ƙaramin aiki ba ne. Domin kuwa koya wa mutum, wanda bai san abu ba, kuma shi ya zama ya san bai sani ba, yana da sauƙi. Amma ka ga koya wa mutum wanda bai sani ba, amma shi bai san bai sani ba, wannan yana da wuya. Sai dai kuma Allah shi ne mai sani!

Ban da wannan, burimmu na biyu kuma, muna roƙo, wannan tarihi ya zama harsashi na ginin taƙaitaccen bayani, wanda mu ke da niyyar yi na addinin musulunci. Idan har Allah ya ba mu ikon cika wannan nufi, hakika babban burin da mu ke da shi na zama a duniya ya cika.

A juzu'i na farko, mun zana kadan daga cikin littattafan larabci wadanda ke gabammu, sa'ad da mu ke rubuta wannan tarihi. Da mun yi niyya, ko wane shafi muka cika, mu fadi littattafan siyari wadanda suka ba mu abin da muka rubuta a ciki. Sai malamai suka ce mana wannan zai rikitar da jama'ar da mu ke rubuta littattafan nan dominsu, watau yara, da mata, da wadansu kamata, wadanda ba su sami yin karatu mai zurfi ba. amma duk da haka, in wani na so ya ƙara sakankance wani abu da muka rubuta, to, ya sani abubuwa da dama na cikin wannan juzu'i na biyu sun fito ne ko daga tafsirin Jalalaini, ko kuwa daga juzu'an mashahurin littafin nan na siyari wanda a ke kira Ibn Hisham.

**Littattafan Tarihi**

A wannan wuri, muna roƙon wadanda za su karanta wadannan littattafai na mu, kullum kada su zama sun manta da wannan babbar magana da za mu yi. Ga ta : Ko da mu ke yi wa mashahuran littattafan siyari, watau tarihin Annabi, irin su Ibn Hisham, Ibn Sa'ad, da 'Dibri, kirarin sahihanci, sai a lura ko su fa sahihancin nasu, ba irin wanda za a gwada shi ba ne da sahihancin ayoyin Alƙur'ani. Shi Alƙur'ani, Madaukakin Sarki Allah ya saukad da shi, kuma shi ya yi alkawarin kiyaye zancensa, yadda sahihancinsa zai dawwama har ƙarshen zamani.

Ko wane Musulmi, kai har ma wanda ba Musulmi ba in dai yana so ya san gaskiya ƙwayarta na irin halayen Annabi, gaskiy wadda babu gauraye, to, ya sani Alƙur'ani shi ne kadai shiriya

mai yi wa Annabi jagora. Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, a cikin irin zancensa, hadisi, ko a cikin irin ayyukansa, ko halinsa na zama a duniya, ko na zama da mutane, bai taɓa cira ƙafa ɗaya ba, ya taka saɓanin shiriyar Alƙur'ani. Ashe kuwa in har kana so ka san Annabi sahihinsa, to, karanci Alƙur'ani.

Tun Annabi yana da rai ya ke bayyana cewa ba ya aikata abu sai abin da Ubangiji ya hore shi da aikatawa. Ubangiji Allah kuma da zatinsa ya bayyana cewa Annabi ƙa ya huruci da son zuciyarsa, sai dai ɗa abin da wahayi ya zaike masa da shi. Watau zancen da Alƙur'ani ya tattara.

Mashahurin shaihin nan na musulunci, wanda kowa ya sani, Imam Ahmadu ibn Hambali, ya gargaɗi jama'a a kan kada su riƙa ɗaukar nassin tarihi kamar ayar Allah. Su duka littattafan tarihi, har su waɗanda mu ke yi wa kirari sahihanci, ba ɗaya da za a iya tabbatarwa ya tsira ga barin kuskure. In aka riƙe wannan sharaɗi, sai a ci gaba da karatu.

Amma duk da wannan bayanin, mai karya gwiwa, sai ku tabbata a cikin wannan tsari namu na tarihi, muna ƙoƙari, iyakar ƙoƙari, mu zazzaɓo muku igiya sahihiya, mai ƙarfi ta tarihin Annabi, wadda in kun yi lilo kanta, ba za ta tsinke da ku ba, in Allah ya so.

Ba zan iya wuce wannan wuri ba, sai na ƙara roƙo ga Sarki Allah ya saka wa Shaihu Awad, shugaban Makarantar Ilmin Arabiyya ta Kano da malaman nan na makarantar waɗanda suka sake taimakona ga bin wannan juzu'i kuma na biyu, bayan da na gama shi. Kuma in roƙi Allah ya saka wa Alhaji Baba Ahmed Balaraben Shijiɗa, limamin Kolej ta Gwamnati ta Zariya, da sake haƙuri da ya yi, na karanta masa wannan juzu'i na biyu bayan da na gama, ya kuma sake ƙara ni da bayani kamar yadda ya yi a juzu'i na farko.

A ƙarshe duka, ina roƙo, ya Allah ka karɓi wannan aiki namu, kuma ka gafarce mu ga abin da muka yi kuskure kansa Ya Allah ka nufi wannan aiki namu, na bayyana Annabin Rahama, wanda aka aiko da saƙon aminci zuwa ga duniya, ya zama asali ga sauya hanyar tarbiyar manyan gobe, da tunaninsu, yadda zai koma ga tunanin rahama da aminci, da kafa lafiya da zama lafiya a duniya — Saƙon da Annabin Rahama ya kawo.

ALHAJI ABUBAKAR IMAM
'Dan Alƙalin Kagara M. Shaihu Usuman

# ANNABI MUHAMMADU

## Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi

YA Allah ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici !

A juzu'i na farko na wannan littafi na tarihi, mun bayyana kaɗan, daga tarihin Larabawa, da na ƙasar Makka, tun kafin bayyanar musulunci. Mun bayyana tarihi kaɗan na daga waɗansu manzanni waɗanda Sarki Allah ya aiko a duniya. A ciki muka faɗo ga tarihin Annabi Ibrahim, muka biyo shi a taƙaice, tinkis tinkis, har muka zo ga haihuwar Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Ba shakka duk wanda ya karanci juzu'i na farko, na wannan tarihi, zai san nitsommu ya yi nisa a cikin wannan bincike. Amma kuma duk da haka zurfaɗfawar ba ta zama aibi, muddin za mu tsamo lu'ilu'in da mu ke bukata. Tun farko, mun ce muku Annabi Muhammadu mutum ne, ya kuwa fito ne daga tsatson mutane. Saboda haka, yadda ko wane mutum ke da dangi, haka shi ma ya ke da dangi. Bari mu ɗan tsaya wannan wuri, mu gusura muku kaɗan daga cikin dangoginsa. Ta haka a nan gaba, im mun ƙunduma cikin ƙungurmin dawan da ke gabammu na tarihinsa, kuka ji wani suna, na wani danginsa, za ku iya sanin yadda suka gamu.

Mun gaya muku dai, a littafi na farko, cewa Kusayyi shi ya haifi Abdu Manafi. To, ba shi kaɗai ya haifa ba, shi ma ne ya haifi Abdu Dari da Abdul Uzza. Shi Abdul Uzza, ɗan Kusayyi, ya haifi Asadu, Asadu ya haifi Huwailid. Huwailid ya haifi Hadijatu da Al'awwam. Shi Al'awwam ya haifi Zubairu. Ka ji nasu layi.

Abdu Manafi kuwa ɗan Kusayyi guda, shi ya haifi Muɗallibu, da Abdu Shamsi, da Hashim, layin su Annabi. To, shi Abdu Shamsi, ya haifi Umayyatu. Umayyatu ya haifi Harabu. Harabu ya haifi Sufyan. Abu Sufyan ya haifi Mu'awiyya Duk za ku ji su a gaba.

A layin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, mun ce muku Hashim shi ya haifi Abdul Muďďalibi, kakan Annabi. To, shi Abdul Muďďalabi ba uban Annabi kawai ya haifa ba. A'a, shi ma ne ya haifi Haris, da Abu Ďalib, da Abi Lahabi, wanda Sarki Allah ya yi zancensa cikin surar "Tabat Yada," da Abdullahi tsohon Annabi, da Abbas da Hamza, da Zubairu da Safiya. Kun ga watau duk waďannan iyayen Annabi ne. Domin kuwa daga wan mahaifinsa, sai ƙanen mahaifinsa.

To, cikin su Abu Talib ya haifi Ja'afaru, da Aƙilu da Ali, sarkin yaƙin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Shi Aƙilu ya haifi Muslimu. Ali kuwa ya haifi Hasan da Husaini da Mushasan jikokin Annabi. Duk dai za ku ji labarin a gaba, in Allah ya so. Waďannan su ne kaďan daga dangogin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

## KAFIN YA ZAMA ANNABI

TO, yanzu fa za mu fara ba da tarihin Muhammadu, tun kafin ya zama Annabi. A taƙaice dai wannan shugaba da aka haifa, da zai zama mai cikakkiyar daraja, shi ne Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Kun ji dai sunan ubansa Abdullahi, sunan kakansa Abdul Muďďalibi. Watau a yanzu za mu kira shi Muhammadu ďan Abdullahi, jikan Abdul Muďďalibi. Sunan uwarsa Aminatu 'yar Wahabi. Mun ce an haife shi a Makka ne, a ranar Litinin, 12 ga watan Rabui'l'awal. Yana daga cikin wata kabila ta Larabawa da a ke kira Kuraishu. Yanzu za mu fara ba da tarihinsa tun kafin ya zama Annabi.

Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, kun ga ashe ya tashi yana maraya ne, domin kun ji ubansa ya rasu tun yana da wata kaďan a ciki.

To, ga al'adar Larabawa, su kan biya waďansu mata kuďi don su ba jiriransu mama, kuma sun fi so a reni jiriri a ƙauye, don shi zama hazlƙi. To, a lokacin da aka haifi Annabi, uwarsa ita ta fara renonsa. Ta fara da taimakon Suwaiba baiwar Abi Lahabi, ďaya daga cikin baffansa shi Annabi. Daga baya waďansu matan ƙauye suka shigo Makka neman jirirai. Amma duk suka ƙi yarda su ďauki Muhammadu, don sun ji an ce

ubansa ya rasu, suna gudun a rasa biyansu lada mai yawa. To, daga cikin matan nan na ƙauye da suka zo, akwai wata, wadda a ke kira Halimatus Sa'adiyya. Ita da ta biɗi jariri ta ga ta rasa samu ko ina, sai ta zo ta ce ta yarda ta ɗauki Muhammadu haka nan.

Da can kuwa Halimatu da mijinta Abu Kabshu matalauta ne, amma da zuwan jaririn nan Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sai suka ga suna ta samun arziki da wadata. Awakansu suka yi ta haihuwa, suka yi ta samun nono isasshe.

To, ita Halimatu tana da wata 'ya ƙanƙanuwa, wadda a ke kira Shaima'u, ko da yaushe ita ke renon Muhammadu, har ta kan riƙa yi masa waƙa, tana cewa :

"Ya Rabbana, abƙi lana Muhammada,
Hatta narahu yafi'an wa'amrada.
Summa narahu sayyidan musawwada.
Wakbit a'adihi ma'an walhussada.
Wa'aɗihi izzan yadumun abada!"

Ma'anar wannan waƙa tata ita ce : "Ya Ubangijimmu ka raya mana Muhammadu, har mu ga ya girma, ya zama shugaban jama'a. Kuma ya Allah ka karya dukan maƙiyansa, masu yi masa hassada. Ya Allah ka ba shi ɗaukaka madawwamiya!"

Allahu Akbar! Kun ji waƙar da a ke yi wa Annabi rawa da ita tun yana jinjiri. Duk abin da yarinyar ta roƙa Allah ya karɓa.

## Mala'iku Sun Tsaga Kirjinsa

Lokacin da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya cika shekara huɗu, ran nan yana kiwon tumaki, a kusa da gida, tare da abokinsa, sai ga waɗansu mutane biyu, masu fararen tufafi, sun zo inda su ke. Daga nan ɗayan mutanen nan ya dubi Muhammadu, ya tambayi abokin tafiyarsa, ya ce, "Shi ne wannan ?" Abokin ya ce masa, "I, shi ne." Shi ke nan, sai sauran yara abokan kiwonsa suka ga mutanen nan sun kama Muhammadu, sun kwantad da shi. Suka fasa cikinsa, suka lalabo wani abu daga cikinsa, suka ɗebe shi, suka yi jifa da shi.

Da ganin haka, sai yaro guda ya sheƙa a guje, ya nufi gida, ya shaida wa Halimatu da mijinta. Suka rugo, suka [illegible] shi

ke da sauri, suka tarad da shi duk kamannunsa sun sake. Da suka tambaye shi abin da ya same shi, sai ya gaya musu, abin da waɗannan mutane suka yi masa.

Ashe su waɗannan ba mutane ba ne, mala'iku ne, Allah ya aiko su don su zo, su ɗebe rabon Shaiɗan daga cikin ƙirjin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Wannan al'amari ya ba Halimatu tsoro mai yawa. Don haka sai ta mai da shi Makka gun uwarsa, a sa'an nan yana da shekara huɗu da haihuwa. Ko da Annabi ya girma bai taɓa mantawa da irin alherin Halima ba da taimakonta a gare shi, sa'ad da yana ƙarami. Saboda wannan godiya Halima ta zama abar girmamawa ga Musulmi.

Wata shekara, da Halima ta zo Makka, Annabi ya gan ta, sai ya tashi da murna yana cewa, "Uwata, uwata!" Ya shimfiɗa mata mayafinsa don ta zauna bisa, saboda girmamawa da tuna alherin baya. Wata shekara kuma da aka yi wani mugun fari a ƙasar Makka har Halima ta zo Makka daga ƙauyensu. Da za ta koma Annabi ya yi mata alheri mai yawa, na raƙuma da tumaki.

### Mahaifiyar Annabi Ita Kuma Ta Rasu

Mu koma ga labarimmu. Da dai Halima ta ga irin halin nan na Annabi sai ta mai da shi Makka, wurin uwarsa Aminatu. Ba a daɗe ba, sai uwar ta ɗauke shi, ta tafi da shi Madina, don su ga danginsa na wajenta. Suna dawowa, sun kawo wani gari wai shi Abwa, sai rashin lafiya ya kama Aminatu, a nan Allah ya nufe ta da rasuwa. Shi ke nan, Annabi Muhammadu bai cika shekara shida ba, ya zama maraya ɗungum, ba uba, ba uwa! Sai renonsa ya koma hannun kakansa Abdul Muɗɗalibi. Ya rungume Muhammadu a cikin gidansa, ya shiga taimakonsa, da tattalinsa, yana mai tausayi a gare shi. Abin ikon Allah, bayan shekara uku, sai shi kuma Abdul Muɗɗalibi ya rasu. Allahu Akbar, watau Muhammadu bai cika shekara takwas ba ke nan duk ya rasa uwa da uba da kaka.

Amma ko kafin Abdul Muɗɗalibi ya rasu, sai da ya danƙa Muhammadu a hannun ɗansa Abu 'Dalib. Abu 'Dalib kuwa shi ne ya gaji Abdul Muɗɗalibi ga riƙon 'Dakin Ka'aba, da shugabancin jama'ar Makka. Watau yanzu rikon Annabi ya koma hannun baffansa ke nan, Abu 'Dalib, mahaifin Sayyidina Ali.

Allah gwani! Kowa renon Muhammadu ya faɗa hannunsa, sai ya ga ba ya da abin ƙauna kamarsa. Wannan baffa nasa, Abu Ɗalib yana yabon halayen Muhammadu ko da yaushe, har ma ya kan ce shi bai taɓa ganin Muhammadu yana irin faɗace-faɗacen nan da yara kan yi ba. Kuma bai taɓa jin bakinsa ya fito da wata magana mummuna ba. Ko da yaushe, idan an kawo abinci, don ya ci tare da sauran yaran gida, sai sauran yara su riƙa yin wasoso. Amma shi ba ruwansa. Sai ka ga shi ya koma waje ɗaya yana ƙallonsu suna wasoso. Shi abin da duk ya samu ya ishe shi.

Kai, tun Annabi yana ƙarami, aka san shi da kamun kai, da mutunci, da sanin ya kamata, kana ga gaskiya da riƙon amana. Abu Ɗalib ya kan ce shi tun da ya ke tare da Annabi, tun yana yaro bai taɓa jin ƙarya ta fito bakinsa ba. Hasali dai, saboda irin waɗannan halaye ne har AbduƊalib ya zamo yana sonsa ƙwarai da gaske, fiye ma da yadda ya ke son 'ya'yan cikinsa—Muhammadul Aminu, Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana !

Ana nan haka sai wata rana, sa'ad da yana da shekara kamar sha biyu, baffan nasa ya yi niyyar ya tafi fatauci a ƙasar Sham. Kun kuwa sani cewa ita wannan ƙasa tana-da nisa daga Makka, tun ba a wancan lokaci ba. To, don tsananin son da Abu Ɗalib ke yi wa Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sai ya ga ba shi iya tafiya Sham ya bar shi gida. Shi kuma don tsananin son da ya ke yi wa baffan nan nasa, ba shi iya so ya rabu da shi lokaci mai tsawo irin wannan. Sabo da haka sai shi Abu Ɗalib ya ɗauki Muhammadu suka tafi tare.

A can ƙasar Sham, sun isa Birnin Busura, sai suka haɗu da wani babban malamin Nasara, wanda a ke kira Bahira. Da ya dubi Muhammadu da kyau, ya kuma ji irin halayensa masu bam mamaki, sai ya gane alamomin annabci a gare shi, kamar yadda ya karanci siffofinsa. Da ganin haka, bai ɓoye kome ba, sai ya ce wa Abu Ɗalib, "Ka kula da wannan yaro da kyau. Wata rana Allah zai aiko shi da annabci!" Magana ta fito kamar ta ba'a, ashe ilhami ne na Maɗaukakin Sarki Allah. Shi ke nan da suka ƙare harkarsu a ƙasar, ba su daɗe ba, suka dawo gida.

## Hada Kai Don Hana Zalunci

Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana da shekara ashirin da ɗaya ya halarci wani taro da manyan Makka suka yi wanda a ke kira Hilful Fulul. Shi wannan taro an daɗe da kafa shi a ƙasar Makka, tun kafin bayyanar Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Amma a lokacin bayyanar Annabi taron ya mutu. Sai daga baya, Zubairu Ibn Abdul Muɗɗalib, watau baffan Annabi guda, kuma ɗaya daga cikin ginshiƙan Makka, ya yi niyya ya sake ta da shi.

Ran da za a sake ta da shi, sai manyan Kuraishawa suka yi taro a gidan wani wai shi Abdullahi Ibn Jada'an. A nan suka ɗauki alkawarin cika burin wannan taro. Su duka suka ɗauki alkawarin idan aka zalunci mutum ɗaya daga cikinsu, ko kuwa wani mutum dabam a cikin Makka, baƙo ko ɗan gari, lalle za su yi tsaye, su ga am mayar masa da haƙƙinsa, su ga adalci ya tabbata.

To, mutane da yawa sun kawo kokensu ga waɗannan mutane, sun kuwa sami biyan bukata da taimakonsu. Annabi Muhammadu kuma, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya yi babban aiki a cikin waɗannan jama'a. Domin kuwa halayen da Sarki Allah ya sanya masa sun yi daidai da burin wannan taro, watau kafa adalci da kyautata halayen jama'a.

## Auren Annabi Da Hadija

Da Annabi ya kai kamar shekara 25 da haihuwa, sai labarin gaskiyarsa da riƙon amanarsa ya cika kunnuwan wata tajira Baƙuraisha, wai ita Hadija. Saboda haka ta roƙi baffansa, da shi, ko za a yarda ya riƙa yi mata fatauci, don-ta ji yadda kowa ke yabon gaskiyarsa da riƙon amanarsa. Shi kuwa Muhammadu bai ƙi ba, kuma baffansa bai ƙi ba, duk suka yarda.

Tajiran nan Hadijatu, ta gama shi da wani yaronta, wanda a ke kira Maisaratu. Ta ba su dukiya mai yawa suka koma ƙasar Sham. Maisaratu ya ga abubuwan mamaki game da Annabi a lokacin wannan tafiya tasu !

Wata rana suna cikin tafiya, sai suka iso ga wata itaciya. Sai aka ga kawai Muhammadu ya tsai da ayari, ya sauka, ya zauna gindin itaciyan nan. Lokacin da wani shaihun malami na ahlil

kitabi. wanda a ke kira Nasďura ya ga Muhammadu zaune a gindin wannan itaciya, sai ya matsa kusa da Maisaratu, ya ce masa, "Wannan shi ne annabin ƙarshen zamani!" Ku lura fa duk waďannan abubuwa suna aukuwa ne, tun ana saura kamar shekara 15 a aiko wa Muhammadu da saƙon annabci.

A cikin wannan fatauci Hadija ta ga ta sami riba a hannunsa, irin wadda ba ta taɓa mafarkin za ta samu ba. Yaronta kuma, Maisaratu, da suka dawo ya riƙa ba Hadija labarin tsananin gaskiyar Annabi Muhammadu, da tsananin riƙon amanarsa, da tsananin tsarkin zuciyarsa.

Labarin nan fa da Hadija ta ji, da abin da ta gani da idonta, suka ƙayatad da ita har ta kai ga roƙon Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ko zai yarda ya aure ta. Annabi bai tozarta ta ba, sai ya karɓa. Aka yi aure. A lokacin ita tana bazawara ke nan, da shekara wajen 40 na haihuwa. Shi kuwa ga shi ďan shekara 25, auren fari! Su a gare su da, wulakanci ne mutum ya auri bazawara. Da aka yi aure, sai Hadija ta mallaka wa Annabi dukan dukiyar da ke gare ta. Da karɓa shi kuwa, me ku ke zato ya fara yi da dukiyar? Sai ya ce duk bayin gidan ya 'yanta su! Wannan al'amari kuma ya ƙara girgiza Larabawa. Kuma ga abin mamaki, dukan 'ya'yan da Annabi ya haifa a duniya su bakwai daga wannan mata Hadijatu suka fito, sai guda kawai shugabammu Ibrahim, shi ne ďam Mariyatu.

To, ana nan, bayan wannan aure, sai aka gama gyara ginin Ɗakin Ka'aba. Domin a lokacin duk ya rurrushe. Da za a gina kabilun Kuraishawa duka suka taru ga gini, ko wace kabila tana burin samun albarkar wannan 'Daki. Ku lura fa, musulunci bai bayyana ba, amma kun ga yadda Sarki Allah ya nufi Larabawa da riƙon wannan 'Daki da daraja, alhali kuwa ga su ba Musulmi ba.

Da aka ƙare gini, sai rigima ta tashi a kan kabilar da za a yarda ta ďauki Hajarul Aswadi, watau Baƙin Dutse, ta aza shi inda ya ke. Ko wace kabila tana ganin wadda duk aka bari ta yi wannan aiki ita ke nan ta zama mafificiya a cikin kabilun Kuraishawa.

Ana cikin haka, an yi cirko-cirko, an rasa yadda za a yi, sai wani tsoho ya kawo dabara. Ya ce duk a yarda, mutumin duk da Allah ya nufa ya fara zuwa nan a tambaye shi, ya

zama alƙali, ya raba wannan gardama. Abin da ya faɗa kuwa duk a ɗauka. Aka ce hakanan ne, hakanan ne.

Abin mamaki, wa ku ke zato Allah ya turo, don ya zama wannan alƙali? Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Ana tsare an zazzare ido ko wace hanya, can sai duk suka ce, "A, ga Muhammadu nan zuwa." Da ya iso suka gaya masa rikicin da su ke ciki duka. To, da kai ne aka zaɓa wannan alƙali, me za ka yi? Ce mini ni zan ɗauka in aza musu don ni da kabilarmu mu sami darajar.

Amma tsaya ka ji yadda shugaban Annabawa ya yi wannan hukunci. Da jin maganarsu, sai ya cire mayafin jikinsa, ya shimfiɗa shi a ƙasa, ya ɗauki Dutsen ya aza bisa mayafin, kana ya ce duk kabilun Kuraishi da suka yi wannan gini, su kewaye, kowa ya kama, su ɗaga Dutsen su duka a haka, su aza shi inda mazauninsa ya ke. Da suka yi, shi Annabi ya sa hannu ya gyara masa zama. Wannan shari'a ta faranta wa ko wace kabila rai, suka watse suna mamakin wannan fasaha. A nan suka tabbatar da wannan suna nasa, Muhammadul Aminu, Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana.

### Saƙon Sarki Allah Ya Sauka—Annabci

Mun sani duk an lura da cewa, tun fara tarihin nan da muka yi har ya zuwa nan, Ubangiji bai aiko wa Annabi da saƙon annabci ba tukuna. Mun kira Muhammadu da suna Annabi tun a baya, don kada jahilai su zarge mu ne kawai. Amma a haƙiƙa daga nan gaba kaɗan ne za ku ji inda ya kamata da mu fara kiran Muhammadu da suna Annabi.

Sai dai fa tun kafin Maɗaukakin Sarki Allah ya aiko masa da annabci, al'adarsa, ita ce ya tafi kogon wani dutse wai shi Hira, ga shi nan mil uku daga Makka, duk alhazai sun san shi Sai ya shiga ciki, yana ta ibada da tuntuntuni cikin zuciyarsa tsarkakka. Allah bai aiko wa Muhammadu da annabci ba, sai da ya cika shekara 40 da haihuwa. Ran nan ne fa, Ubangiji Allah, ya aiko Mala'ika Jibrilu, da babban saƙo, annabci, zuwa ga Babban Shugaba, Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Mala'ika Jibrilu ya iske shi a cikin kogonsa na Dutsen Hira.

A cikin Buhari, an nuna cewa, surar Alƙur'ani wadda aka aiko wa Muhammadu da annabci da ita, ita ce surar Iƙra'a.

Watau sura ta 96. Annabi ya dawo gida yana mai ɗimauta saboda ziyarar Mala'ika Jibrilu a gare shi, su biyu cikin wannan kogon Dutse na Hira.

Da Hadija ta ji abin da ya gaya mata, na ziyarar wannan mala'ika, ta kuma lura da yadda fuskar mijinta ta sauya, sai ta ce masa, "Kada ka damu, yi farin ciki, Allah ba zai kawo ƙasƙanci ba a gare ka. Yaya kuwa Allah zai kawo ƙasƙanci gare ka ga shi ko yaushe ba abin da ka ke yi sai alheri ga 'yan'uwanka, ga kada taimakon wanda duk ya kamata a taimaka, ga ka da liyafa ga baƙi ga ka da taimako ga gajiyayyu da matalauta, ga ka da taimako ga maƙwabta, ga ka ba ka taɓa faɗar magana ba ta ƙarya, ba ka taɓa ɗaukar alkawari ka saɓa ba. Hasali dai irin halinka na karimai ba a ganinsa sai ga zaɓaɓɓun mutane! Allah ba ya wulakanta ka!"

Wannan shi ne abin da muka ciro daga mashahurin littafin nan da a ke kira Buhari, Babin Wahayi. Allahu Akbar! Ka ji shaidar mata ga miji, Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana! Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi!

### Annabi Ya Fara Kira!

Daga nan fa sai aka tafi da Annabi ga wani mashahurin shaihu, masanin Linjila, ana kiransa Waraƙa. Shi kuwa yana cikin zuriyar su Hadija ne. Da ya ji abin da ya faru ga Muhammadu a Kogon Hira, sai ya ce, "Wannan ai shi ne mala'ika wanda aka aiko ga Annabi Musa, tun shekaru aru aru." Ya ce, "Kash, da ma Allah zai tsawanta raina, har in ga ranar da za a kore ka daga wannan gari naku, da lokacin nan na taimake ka." Annabi ya dube shi ya ce, "Za a kore ni daga wannan gari namu?" Shaihu Waraƙatu ya ce, "Ai kamarku duk korarsu a ke yi. Wannan jawabi ya ba Annabi mamaki. Ya duba ya ga shi wane laifi ya yi wa jama'arsa da za su kore shi daga gari ya rasa.

Ana nan, shiru, wahayi bai sake sauko masa ba, sai bayan kwana 40. Ran nan kuma sai Sarki Allah ya sake aiko Mala'ika Jibrilu zuwa gare shi da wahayi na biyu. Ga ayoyin nan cikin Alƙur'ani. Su ne ayoyi na farkon surar Ya'ayyuhal mudassiru. Ga fassarar da malaman tabsiri ke yi ga waɗannan ayoyi da mu ke zance: "Ya kai wanda ya lulluɓe jikinsa da mayafi, tashi, ka yi gargaɗi ga al'umma, kuma ka ɗaukaka Ubangijinka,

ka tsarkake tufafinka, ka nisanci munanan ayyuka. . . . "

Allahu Akbar! Malam dubi, bayan Allah ya aiko wa Annabi da umurnin ya tashi ya yi gargaɗi ga jama'a ya kuma girmama Ubangijinsa, sai me? Ka ga sai umurnin tsarki. Ashe ba yadda waɗansummu suka ɗauka ba, cewa wanki da wanka barikanci ne, daudar jiki, da ta tufa, su ne a ke so, su ne alamar tsoron Allah !

Hasali dai, tun a wannan rana da Ubangiji ya ce wa Annabi ya tashi ga kiran jama'a zuwa musulunci, Annabi kuwa ya tashi. Ba wani shiri, ba wani tunani, ba wata shawara, sai ya ga kawai ya fara. Amma fa bai fita fili sosai ba.

Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, daga gidansa ya fara bayyana wannan saƙo da Allah ya aiko shi da shi. Duk a duniya kuwa, matarsa Hadija, ita ce mace ta farko da ta fara karɓar musulunci. A cikin manya kuwa na waje, babban abokinsa Sayyadina Abubakar shi ne farko.

Shi kuwa Sayyadina Abubakar babban aboki ne ga Annabi Muhammadu tun da. Kuma shi mutum ne mai arziki da muhibba ga jama'a. In ya gitta kara a lokacin, mutane da yawa ba su ƙetarewa a Makka, don muhibbarsa. Ga shi kuma da ɗabi'o'i ababan yabo ga kowa. Da Annabi ya yi kiransa ga addinin musulunci, bai tsaya wata-wata ba sai ya karɓa. Ya karɓa don ya rigaya ya yi imani a ransa Muhammadu dai ba ya ƙarya !

Shi ke nan, Annabi ya sami 'yar ƙungiya ta waɗanda suka ba da gaskiya da shi, suka fara yin ibadarsu a asirce. Su taru, su ya su, iyakarsu, su yi salla a asirce. Ran nan suna yi, sai Abu Talib watau mahaifin Sayyadina Ali, kuma baffan Annabi ya gane su. Ya tsaya a baya yana duban wannan irin abu da su ke yi, ga ɗan ɗansa ciki. Da suka ƙare. Abu Talib ya kira ɗan, watau Sayyidina Ali, ya ce masa, "Kai Ali, me ku ke yi haka ?" Sayyidina Ali ya ce, "Addinin Mala'iku ke nan, da Annabawan Allah, shi mu ke biye. Shi ne kuma addinin Annabi Ibrahim, amincin Allah ya tabbata a gare shi." Ya ci gaba da ba tsohonsa labarin musulunci, ga shi kuwa ɗan yaro, ɗan shekara kamar sha biyu ko sha uku. Da ya gama ba shi bayani, sai shi uban ya girgiza kai, ya umurci Sayyadina Ali da ya riƙe wannan sabon addinin, domin shi Abu Talib ya yi imani a ransa, Muhammadu ba zai ɓaddasa ɓata ba.

To, a haka, a ɓoye a ɓoye, Annabi ya ci gaba, har shekara kamar uku. Daga nan fa Maɗaukakin Sarki Allah ya aiko gare shi da umurni ya fito fili ya fara kiran jama'a ga abin da aka umurce shi, watau musulunci. Aka hore shi kuma da ya nisanci masu tsafi. Ga wannan umurnin nan cikin Alƙur'ani.

Daga ran nan maganar ɓuya ta ƙare! Wata rana Annabi ya hau tudun Safa, ya tara danginsa, ya riƙa kiransu kabila kabila, ya zuwa ga musulunci, yana cewa, "Allah ya aiko ni in shaida muku, ba wani amfani da za ku samu a nan duniya, ko a gobe lahira sai kun yi imani da gaskiya, cewa babu wani abin bautawa sai Allah." Da jin wannan jawabi sai suka watse, suna gunaguni wai Muhammadu ya ɓata musu lokaci. Har wani baffansa Abi Lahabi ya yi hushi ya ce, "Da saboda wannan magana kawai ka tara mu? Kaitonka da abin da zai same ka har iyakar ranka!"

Daga nan Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ci gaba da cewa, "Allah ya aiko ni a gare ku, ba wani Balarabe da ya taɓa kawo muku baiwa kamar wannan da na kawo muku. Na zo muku da albarkatai na duniya da na lahira. A cikinku wa zai taimake ni burin iyad da wannan saƙo?" Duk aka yi tsit.

Daga can, sai aka ji muryar wani ɗan yaro ya ce, "Ya Annabin Allah, ko da shi ke ni ne mafi ƙanƙanta, mafi ƙuruciya a wurin nan, na yi alkawari ni zan zama sadauki a cikin wannan kira naka." Da aka duba a ga ko wa ke wannan magana, sai aka ga ashe ɗan yaro ne, Ali ɗan Abi Talib. Allahu Akbar— Ka ji karɓawar Aliyu, Zakin Allah mai rinjaye, Aliyu Ibn Abu'Dalib!

A haka, mutane na zato kamar abin na wasa ne, sai suka ga abu bai daina ba. Maimakon Annabi ya gaji ya watsar, yadda da waɗansu ke zato, sai suka ga Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sai gaba gaba ya ke ta yi. Ga shi sai kaɗan kaɗan ya ke samun masu yarda da shi, amma duk da haka shi himmarsa ko wace rana sai ƙara ƙaruwa ta ke ta yi. A taƙaice abin da ya ke kiran jama'a zuwa gare shi shi ne wannan : Babu abin bauta wa sai Allah, kuma shi manzonsa ne. Saƙon da aka aiko shi da shi kuwa shi ne abin da Alƙur'ani ya kawo, shi ne kuma abin da ya ke so jama'a su saurare shi ya

gaya musu. Kun ga watau tun farko musulunci ya fito ne da kira ga saɓanin abin da kafiran Makka suka saba da ji.

A'a, da fa dai jama'ar Makka suka ga Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, da gaske ya ke yi, ba da wasa ba, suka kuma ga yadda ya ke aibanta addininsu na bauta wa gumaka a fili, ba ya tsoronsu balle ya ɓoye wani abu, ga shi kuma yana samun mabiya, sai tunaninsu ya fara waiwaya bisa kansa.

## Mutanen Gari Sun Fara Damuwa Da Annabi

Ana nan ran nan sai manyan gari suka taru a Hijira Isma'ila, suka ta da maganar Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata gare shi. Suka ce, "Jama'a mu fa lura, tun da mu ke fa ba mu ga abin da muka yi haƙuri a kansa ba kamar halin wannan mutum Muhammadu. Ya zagi iyayemmu, ya zagi addinimmu, ya raba kabilarmu, ya zagi allolimmu! Ba shakka, mun fa yi haƙuri a gare shi, ga kuma al'amari mai girma."

Suna haka, sai ga Annabi, kamar an jeho shi. Ya zo ya shiga ɗawafi, yana kewaya 'Dakin Ka'aba. Duk sa'ad da ya kewayo ta wajensu sai su zunɗe shi. A ran nan dai suka watse ba su ƙulla kome ba. Da gari ya waye kuma aka sake taruwa. Suna cikin shawara dai sai ga Annabi kuma. Sai suka zaburam masa, suka ce, "Kai ne ka ke ce mana kaza da kaza, ka ke aibanta allolimmu da addinimmu?" Annabi ya karɓa ya ce, "Na'am, ni ne!"

Daga nan sai Sayyadina Abubakar, yardar Allah ta tabbata a gare shi, ya zaburo ya shiga tsakani ya ce, "Yanzu ku yalla za ku iya kashe mutum don kawai ya ce Ubangijina Allah?" Da jin haka sai suka lafa, taro ya watse suka rabu da Annabi.

Ana cikin wannan hali ran nan sai wani shugaba, wanda a ke kira Utubatu Ibn Rabi'atu, ya ce, "Ya jama'ar Kuraishi, kun yarda in tafi ga Muhammadu, in yi masa magana, in yi masa alkawuran al'amura da yawa. Kila ya yarda ya ɗauki ɗaya daga ciki, mu kuwa mu ba shi, ko ya ƙyale mu a hakanan?"

Jama'a suka ce, "Mun yarda. Tafi ka yi masa magana." Utubatu ya tafo, ya zauna kusa da Manzon Allah, ya ce masa, "Ya ɗan'uwana. Kai dai namu ne, tun iyakar sanimmu. Ga ka

ka fito daga zuriya maɗaukakiya. Yanzu kuma ga shi, ka zo wa jama'arka da wani sabon al'amari babba, wanda ka rarraba taronsu da shi, ka aibanta allolinsu da addininsu, ka kafirta iyayensu da suka shuɗe. To, ka saurare ni. Zan zana maka abubuwa, kai kuma ka zaɓa ka gaya mana abin da ka ke so ciki mu ba ka".

Annabi ya karɓa, ya ce masa, "Faɗi, ina saurarenka !" Utubatu ya ce, "Ya ɗan ɗan'uwana, in dai abin nan da ka zo da shi, sabo na biɗar dukiya ne, to, za mu tara maka ita daga dukiyarmu har ka zama kai ne ka fi duka dukiya. In kuwa ɗaukaka ka ke so, to, za mu shugabantad da kai bisa kammu. Ƙuma za mu bi ka har yadda ba za mu ƙulla wani abu ba, sai tare da yardarka. In kuma mulki ka ke so, ka sani mun yarda za mu mallaka maka kawunammu".

Da Annabi ya ji ya gama zane, sai ya ce masa, "Ka gama ?" Utubatu ya ce, "I". Sa'an nan Annabi ya ce, "To, saurare ni !" Ya shiga karanta masa ayoyi tun daga ta farko, cikin sura ta 41. Watau amsarsu ke nan. Kun lura da wannan ? Wannan zance na Allah ita ce amsar Annabi, shi ba shi da tasa dabam. Utubatu ya yi zungum yana saurare. Da, Annabi ya kai wajen ayar sujada, ta cikin wannan sura, ya yi sujada, sa'an nan ya dubi Utubatu, ya ce, "Ni ba na burin abin da kuka ce. Ni ban zo da abin da na zo muku da shi ba don biɗar dukiyarku, ko ɗaukaka bisa gare ku, ko mulkin kanku. Ni Allah ne ya aiko ni gare ku, manzo. Ya kuwa aiko mini da Littafi (watau Alƙur'ani) ya umurce ni in zama mai bushara a gare ku, kuma mai tsawatarwa Na kuwa zo muku da saƙon Ubangijina. Na yi nasiha gare ku. Idan kuka karɓi abin da na zo muku da shi, rabonku ke nan duniya da lahira. Idan kuka ƙi, ni zan yi haƙuri ne ga al'amarin Allah, har ya hukunta abin da zai hukunta tsakanina da ku". Da wannan kalami, Utubatu ya taso, ya rabo da Annabi, ya juyo zuwa ga jama'arsa.

Da jama'arsa suka gan shi tafe, sai suka ce, "A'a haka ! Mun ga fuskar Utubatu ta sake, ba yadda ta ke ba sa'ad da ya tashi". Da ya iso ya zauna suka ce masa, "Yaya ? Ya ce, "Wallahi na jiwo ƙauli irin wanda ban taɓa jin kamarsa ba. Wallahi, ba waƙa ba ce, ba kuwa sihiri ba ne, ba bokanci ba. Ya ku jama'ar Kuraishi ku bi zancen da zan gaya muku, mu rabu da mutumin nan da abin da ya ke ciki. Wallahi a cikin

zancen da ya faɗa, lalle akwai farkarwa mai girma. Idan muka kuskura muka bari Larabawa suka rinjaye shi lalle mu mun faɗi. Idan kuwa ya rinjayi Larabawa, to, mulkinsa shi ne mulkimmu, girmansa shi ne girmammu.

Sai jama'a suka ce, "Wallahi ya dai sihirce ka da harshensa!" Utubatu ya ce, "To, ni dai ra'ayina ke nan. Ku kuma ku aikata abin da ya bayyana a gare ku".

## An Taru Wai Za A Kure Annabi

Al'amari fa ya taru ya cakuɗe ga zuriyar Kuraishawa. Sai suka sake dabara, wai su ƙure Annabi, su kunyata shi ga jama'a, su nuna musu shi ba kowa ba ne, a daina yarda da shi. Saboda haka ran nan suka sake taruwa don su sake saduwa da Annabi.

Da aka taru, sai suka ce, "Ya kai Muhammadu, (kun san ba su yarda su ce masa Annabi) da shi ke ka ƙi karɓar ko ɗaya daga cikin abubuwan da muka ambata maka. To, ga wani abu. Ka dai san ba jama'ar da ta fi mu ƙuncin gari, ko ƙarancin ruwa, ko wuyar abinci. To, ka roƙa mana Ubangijin nan naka, da ka ce wai ya aiko ka, ya ɗauke mana waɗannan nauyayan abubuwa da suka danne mu. Ya yalwata mana garuruwammu, ya cika mana ƙorammu da ruwa, kamar ƙorammun ƙasar Sham, da na ƙasar Iraƙ. Bayan haka ka roƙe shi ya mayar mana da iyayemmu, da kakanimmu, waɗanda suka mutu. Amma kuma ka ce masa cikin waɗanda zai mayar mana ɗin nan, ya gama har da Kusayyi, don kuwa mun ji shi tsoho ne, mai gaskiya. Idan aka mayar mana da Kusayyi, in ya zo shi za mu tambaya, ya gaya mana koa bin da ka ke faɗa ɗin nan gaskiya ne, ko ba gaskiya ba. Idan shi Kusayyi ya zo yagaskata ka, kuma kai ka roƙa mana aka yi mana abubuwan nan da muka zana, sa'an nan ne kai kuma za mu gaskata ka, mu kuma san matsayinka ga Allah, wanda ka ke cewa wai shi ya aiko ka".

Annabi ya karɓa ya ce, "Ni ba da wannan saƙo aka aiko ni gare ku ba. Ni na zo muku ne da abin da Allah ya aiko ni da shi. Na kuwa iyad da saƙon da ya aiko ni da shi zuwa gare ku. In kun karɓa, rabonku ke nan duniya da lahira. In kun ƙi karɓa ni mai haƙuri ne ga al'amarin Allah, har ya aikata abin da zai aikata tsakanina da ku.

Suka ce. "Af, to, idan dai ka kasa yin wannan ne, ga wani. Ka roƙi Ubangijinka, ya aiko da mala'ika wanda zai shaide ka ga abin da ka ke faɗa. Kuma ya ba ka taskoki na dukiya mu gani, ko ka wadata, don kuwa mun ga wadatar dai ka ke biɗa. Ta haka za mu darajanta ka ga Ubangijinka in har shi ya aiko ka kamar yadda ka ke cewa."

Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya sake karɓawa ya ce, "Ni ba mai aikata haka ba ne. Ni ba a aiko ni gare ku da haka ba. Ni Allah ya aiko ni ne in yi muku bushara, kuma in yi muku gargaɗi."

Ɗaga nan sai suka husata suka ce, "To, sauko da samaniya ta danne mu domin kuwa ka ce wai Ubangijinka in ya so yana iya yin haka! Ba mu ma ba da gaskiya gare ka, sai ka sa an yi mana haka!"

Annabi ya ce, "Wannan al'amari na Allah ne, in ya so ya aikata haka, sai ya aikata."

Suka ce, "Ya Muhammadu, ashe da Ubangijin naka bai san za mu taru nan tare da kai ba ne, mu yi maka waɗannan tambayoyi, mu ƙure ka? Me ya sa shi Ubangijin naka bai zo ba da kansa ya riƙa sanad da kai abin da za ka riƙa gaya mana? Kuma ya gaya maka abin da zai yi da mu idan mun ƙi yarda da kai? Kai, mun dai gane asirinka. An gaya mana cewa, wani mutum na ƙasar Yamamata, wanda a ke kira Malam Rahmanu, shi ne ya koya maka wannan abu. To, mu kuwa Wallahi ba mu ba da gaskiya ga Malam Rahmanu har abada! Kuma ka sani ya Muhammadu, mun fa yi haƙuri da halinka iyakar haƙuri. Yanzu kam haƙuri ya isa. Ba mu kuma sake ƙyale ka da abin nan da ka ke kawo mana, sai mun halaka ka, ko kuwa kai ka halaka mu." Sai wani ya karɓa ya ce, "Ba mu ba da gaskiya da kai sai ka zo mana da Allah, da mala'iku duka baki ɗaya." Da haka taro ya watse. Annabi ya tashi ya rabu da su, yana mai baƙin ciki.

### Dabarar Abu Jahali Wai Zai Kashe Annabi

Da Annabi ya ba da baya, sai Abu Jahali ya ce, "Ya ku jama'ar Kuraishawa, ku lura fa, kun ga Muhammadu ba zai daina aibanta ibadarmu ba, da zagin iyayemmu da zagin allolimmu. To, ni ga shawarata, gobe zan ɗauko ƙaton dutse ne, idan ya zo Ɗakin Ka'aba, zai yi sujada z[illegible] yi irin sallan nan

tasa, ni kuwa sai in laƙaƙa, in kwantsama masa dutsen a kai, kan ya ratsattsake, ya mutu a huta. In ya so in ɗanginsa za su dafa ni ne daga baya, su ɗafa ni. Kun yarda da wannan shawara tawa, ko kuwa?"

Duk taro suka ce, "Mun yarda!" Da asubahi duk suka zo suka mammaƙe, don su ga abin da zai faru. Da Annabi ya shigo, ya kabbara salla, ya fara, ya yi ruku'u, ya yi sujada, sai Abu Jahali ya kinkimo dutse daga rabin 'Dakin Ka'aba; ya nuho Annabi. Yana zuwa kusa sai ya ga hannunsa ya ƙage, ya yiwo baya sai da aka ƙwaƙwale dutsen daga cikin hannunsa. Jama'ar da ke mammaƙe da suka ga ya sheƙo, sai suka ce masa, "Me ya faru, ya Uban Hikima!" Sai Abu Jahali ya ce, "Ai da na kusance shi sai na ga wani abu kamar amalen raƙumi ya taso mini baki buɗe zai halaka ni!"

Daga nan sai wani da a ke kira Nalaru Ibn Harsi, ɗaya daga cikin manyan shaiɗanun Makka a lokacin, ya miƙe tsaye ya ce, "Ya ku jama'ar Kuraishi, Wallahi babban al'amari ya sauka gare ku. Ku fa lura cikimmu Muhammadu ya tashi, yana yaro. Ya tashi a kan ba yardajjen yaro kamarsa, ba mai gaskiya kamarsa, ba mai riƙon amana kamarsa. Yana nan haka har ga shi yanzu ya girma, ya kawo mana abin da ya kawo mana, wannan irin sabon addini. Da muka ji muka ce masa wai shi mai sihiri ne. To, Wallahi ku sani, Muhammadu ba mai sihiri ba ne. Mun sha ganin ayyukan masu sihiri, mun san irin nasu. Mun ce masa boka. To, ku sani Muhammadu ba boka ba ne. Mun sha ganin bokaye, da irin ayyukansu. Mun ce masa mahaukaci. To', ku sani Muhammadu ba mahaukaci ba. Mun sha ganin mahaukata, da irin ayyukansu. Ya jama'ar Kuraishi, ku buɗe ido, ku lura da wannan al'amari. Ba shakka, Wallahi al'amari babba ya sauka gare mu." Jama'a suka yi masa tsaki suka watse. Amma duk da haka wannan jawabi nasa ya soki zuciyarsu, tun ba ma da ya fito daga bakin da ba a zato ya faɗe shi ba.

## Hamza Ya Doki Abu Jahali

Muna fata, ya masu karatun wannan littafi, kuna biye da mu da idon basira. Domin kuwa ko da shi ke a taƙaice mu ke tafe, duk da haka mataki mataki mu ke biye na nuna yadda wannan

al'amarin addinin musulunci ya shuku a duniya, da yadda ya tsira, da yadda ya ke girma.

To, ana nan ran nan, ina ya Allah, babu ya Allah, sai Abu Jahali ya yi wa Annabi ƙazamar magana. Annabi ya wuce bai ce masa kome ba. Sai can zuwa rana, Hamza, aminin Annabi ya dawo daga farauta. A lokacin shi Hamza bai musulunta ba. Da ya shigo gari sai ya sami labarin abin da Abu Jahali ya aikata ga ɗanuwansa. Bai tsaya wata wata ba, sai ya zabura, ya nufi inda shi abu Jahali ya ke, ya kwaɗa masa baka a kai. Faɗa zai tashi aka raba. To, shi wannan Hamza da ma ba wanda bai san shi ba a Makka, a kan jaruntaka. Duk Kuraishawa suna shayinsa ! A nan wurin Hamza ya ce shi ya musulunta. Ya yi alkawari kuwa zai taimaki ɗan ɗanuwansa har ƙarshe.

To, a cikin wa'azin da Annabi ke yi kullum, ba ya rabuwa da 'Dakin Ka'aba, domin nan ne babban matattara na kowa da kowa. A ran nan yana ƙofar 'Dakin Ka'aba, yana kiran jama'a su bar bauta wa gumaka, alhali kuwa ga gunki 360 a ciki, sai haushi ya kama mutane, suka zaburo za su halaka Annabi, sai wani mabiyin Annabi da a ke kira Haris Ibn Halah ya shiga tsakani. A cikin wannan tarzoma har wani ya kashe shi Haris Ibn Halah, amma ba a san ainihin hannun da ya kashe shi ba. Watau wannan sahabi, Haris Ibn Halah shi ne ya fara yin mutuwar shahada ga addinin musulunci.

Da Kuraishawa suka ga sun yi rarrashi, sun yi faɗa amma Annabi Muhammadu bai daina abin da ya ke yi ba, sai ma ƙaruwa ya ke yi, sai suka tafi ga kawunsa Abu Talib, suka ce lalle ya hana shi, im ba haka ba kuwa, to. Abu Talib ya kira Annabi ya gaya masa. Ya shawarce shi, kada ya ɗauki kayan da ya fi ƙarfinsa. Annabi ya karɓa, ya ce, "Ya ammi, in da Kuraishawa za su aza rana a bisa hannuna na dama, su aza wata a bisa na hagu, ba zan daina kiran jama'a ba, su gaskata cewa babu Sarki sai Allah. Zan iyad da saƙon da Sarki Allah ya yiwo mini. Zan kafa wannan addini na musulunci a duniya, ko kuwa im mutu bisa wannan niyya."

Amminsa Abu Talib, ya girgiza da wannan amsa ta ɗansa, ya ce, "Ya ɗanuwana, ci gaba da aikinka. Ba mai ƙarfin taɓa ka. Ni kam har abada ba na rabuwa da kai." Allahu Akbar ! Ya Ubangiji ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, n[illegible]

buɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarkinka madaidaici.

## Abi Lahabi Ya ce Tsakaninsa Da Annabi Ba Amana Sai Gaba !

Da dai Abu Talib ya ga irin wannan niyya ta Annabi, ya ga kuwa ya kasa kau da shi daga barinta, sai ya tara danginsu duka, Bani Hashim, ya gaya musu yadda Kuraishawa ke kawo ƙarar Muhammadu a gare shi. Ya ci gaba da cewa da shi ke Muhammadu ya ƙi ya hanu ga abin da ya ke faɗa, yana roƙonsu, su yi alkawari su duka baki ɗaya ga kiyaye Annabi. Ko da ba za su ba da gaskiya da shi ba. Domin kuwa in ji Abu Talib, Muhammadu ba shi wani hali na ƙi. Duk dangi suka yarda da haka, sai Abu Lahabi shi kaɗai ya fandare. Ya nuna shi tsakaninsa da Muhammadu ba amana sai gaba !

A Makka, gidan da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ke, kusa ne da gidan su Abu Lahabi. Sabo da haka in su Abu Lahabi sun yi yanka, ko na akuya, ko tunkiya, ko rago, sai shi Abu Lahabi ya ɗauko tumbin, in ya ga Annabi na salla, sai ya yaɗa masa a kai. Shi kuwa Annabi sai kawai ya fito ya ce, "Ya ku Bani Abdu Manafi wace irin maƙwabtaka ce haka ?" Iyakar maganar ke nan, manya ɗan Abdullahi ! Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana !

A wannan wuri ya kamata mu ƙara bayyana wa jama'a cewa ko da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya zo fa ya iske jama'ar Makka da ma sun san akwai Allah. Sai dai duk da haka ga irin addininsu na lokacin, su kafiran Makka suna zaton gumakan nan nasu su ne tsani, waɗanda su ke kama ƙafafinsu su kusantad da su ga Allah. Kuma suna zato ko sun yi saɓo, in sun zo wurin gumakan nan suka tuba, suka biɗi cetonsu, shi ke nan sai gumakan su gafarta musu. Ga shi ayar Allah ta ce Ubangiji ya fi jijiyar wuyan ɗan Adam kusanci a gare shi, amma su kafiran Makka suna cewa wai su suna bata wa gumaka ne, don su gumakan su kusantad da su ga Allah. Watau sun kama ƙafafunsu ke nan su gumakan su cece su.

## HIJIRA ZUWA KASAR HABASHA

TO, jama'a, ana nan fa, a kwana a tashi, sai dai Annabi ya ga azabar da Kuraishawa ke gwada musu ta yi yawa, iyakar yawa! Shi a gwada masa azaba, waɗanda suka ba da gaskiya da shi kuma a gwada musu. Da ya ga abin ya wuce kima, ga mutane sun ba da gaskiya da shi, amma ba su da 'yancin yin ayyukan addini cikin aminci, sai ya ga ya fi kyau ya rage waɗansu da dama daga cikin mabiyan nan nasa, ya kau da su ya kai su Kasar Habasha, wurin sarkin ya ba shi ajiya. Ita Kasar Habasha ita ce a ke kira Kasar Abyssinia yanzu.

Sarkin nasu na lokacin, ana kiransa Najjashi. Shi kuwa Kirista ne. Sunansa ya yi tambari ko ina a lokacin. Ba don kome kuwa ba, saboda tsananin riƙonsa ga addininsa, da adalcinsa, da nagartarsa, da kirkinsa, da alherinsa. Saboda haka ya zama abin a ba shi amana. Amma kuma ku dubi wannan al'amari! Annabi da mabiyansa su 'yan kaɗan ga shi kuma sun sake raguwa. Maimakon Annabi ya bar su kusa da shi, su ƙara yawa da ƙarfi, sai ya kau da su domin tsananin tausayi a gare su. Shi kuwa da saura suka zauna cikin wannan garwashin wuta na azaban Kuraishawa, wanda Sarki Allah ya nufe su da zama ciki.

A cikin waɗannan sahabai da Annabi ya aika da su Kasar Habasha, har da 'yarsa da surukinsa Sayyadina Usumanu. Shi kuwa Usumanu mutum ne mai arziki, da mutunci ga kowa. Annabi na murna ya kau da su daga azaba, amma su da sonsu ne, sun fi ƙaunar ya bar su kusa da shi, in za a halaka su ne, a halaka su baki ɗaya. Allahu Akbar!

Kada fa mu manta, laifin Annabi kawai a gare su, shi ne ya ce su yarda Allah shi kaɗai ya ke. Kuma su daina bauta wa gumaka, su daina ƙwace da sata, su daina bizne 'ya'yansu mata da rai, su daina shan giya, su daina caca, su daina cutar 'yan'uwa, su daina miyagun ayyuka, su ba da zakka a taimaki kaƙirai, da masakai, da baƙi waɗanda ba su da kowa, a taimaki ma waɗanda ba Musulmi ba, waɗanda suka sanya ransu ga samun wannan taimako. To, idan Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana da laifi ga Kuraishawa a lokacin, wannan shi ne misali na irin laifinsa.

Bari mu koma ga jama'ar Annabi, wadda muka baro ta nufi Kasar Habasha bisa ga umurnin shugaban ma'aika.

Sa'ad da jama'an nan ta Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, suka sauka Kasar Habasha, Sarkin ya karɓe su da irin halayen nan nasa da ya shahara da su. Hasali ma bari ka ji abin da ke rubuce na yadda su kansu su ke ba da labarin maƙwabtakarsu ga wannan sarki. Ga abin da suka ce :

"Da muka sauka Kasar Habasha, mun maƙwabtaci fiyayyen maƙwabta, shi ne Najjashi, sarkin Habasha na lokacin. Muka sami amincewa ga addinimmu, muka ci gaba da bauta wa Allah ba mai cutarmu. Ba ma mai yi mana wata magana wadda za ta ɓata mana rai."

To, da Kuraishawa fa suka ji yadda jama'an nan suka sami zama lafiya a ƙarƙashin wannan adalin sarki na Kirista, sai suka yi zama shawara, suka tara kyauta mai yawa, suka tada mutum biyu, Abdullah Ibn Abi Rabi'ata, da Amru Ibn Asi, suka aike su da kayan har zuwa Kasar Habasha. Suka ce musu in sun tafi, kafin su bidi ganin sarki, su yi ta rarraba rashawa ga na kusa da shi. Bayan sun cika musu bakuna da rashawa, sa'an nan su bidi su kai su, su ga sarki. In sun je gaban sarki, su yi iyakar ƙoƙarinsu, yadda za su sa sarki ya kori baƙin nan. Watau sahabban nan na Annabi, su Sayyidina Usumanu, su Ja'afaru, wadanda ya aike da su can.

Da manzannin Kuraishi suka kai, suka aikata wannan dabara da aka koya musu daga gida. Sa'an nan suka bidi a kai su ga sarki. Da suka isa, suka yi gaisuwa. Sa'an nan suka shiga iyad da saƙon jama'ar Kuraishi suka ce, "Ya wannan sarki mai girma, wadansu jama'armu, masu tsananin wauta sun tafo, wai sun ɓuya a ƙarƙashin inuwarka. Watakila ya sarki, ba ka san abin da ya fito da su ba ne daga gida. Sun rabu ne da addinin iyayensu da kakanni, na bauta wa gumaka, sa'an nan kuma ga su sun zo, sun ƙi shiga addininka. Su da ka ke gani nan, ya mai girma, wani irin addini su ke yi, na dabam, wanda suka ƙago. Kai ma, ya mai girma, Wallahi ba ka san irinsa ba, mu ma ba mu san irinsa ba. Saboda haka, ya wannan sarki mai arziki, manyan garimmu, da iyayensu, su wadannan wawayen da suka gudo, da danginsu, su suka aiko mu gare ka. Suka ce mu bidi izninka, ya mai girma, ka ba da su a koma da su gida. Su za su kula da su fiye da kowa, kuma za su taimake su fiye da kowa, don kuwa su danginsu na gida su suka san ainihin abin da ya same su."

Manzanni suka yi tsit, su ji irin karɓawar da sarki zai yi musu. Kafin ya karɓa, sai wani ɓafade, wanda aka cika masa ciki da rashawa ya yi faraɪ, ya riga sarki magana, ya ce, "Allah ya ba sarki nasara. Lalle manzannin nan suna da gaskiya. Jama'arsu ta garinsu za su fi kula da su, da-taimakonsu domin su suka san abin da ya same su. In-sarki ya yarda sai ya ba su 'yanuwansu su mai da su garinsu, cikin ɗanginsu".

Da jin haka, sai sarki ya husata, ya ce, "To, yanzu ne kuma na ƙi im ba da su ! Yaya mutane za su maƙwabtace ni, su sauka ƙasata, su zaɓe ni bisa gak owa, sa'an nan in ƙore su a haka, ba da na kira su ba, na tambaye su-ga abin da waɗannan manzanni suka faɗa ? Idan abin da manzannin nan suka ce gaskiya ne, sai im ba su 'yanuwansu su koma da su gida. Idan kuwa ba gaskiya ba ne in hana su su. Maimakon haka ma sai in ƙara kiyaye su".

Sai sarki ya ce a je a kira waɗannan sahabbai na Annabi ya tambaye-su. Da suka zo, suka yi gaisuwa, sarki ya ce, "Wane irin addini neku ke bi, wanda jama'arku ta rarraba da ku a kansa, kuma ga shi ku ba ku shiga nawa addinin ba, ba ku kuwa shiga wani addini ba da muka sani ?"

Daga nan sai Ja'afaru, ɗan Abi 'Dalib, watau ammin Annabi, ya karɓa, ya ce, "Ya wannan sarki mai arziki. Mu mutane ne na cikin ahalin jahiliyya. Muna bauta wa gumaka, muna cin mussai, muna ayyukan alfasha, muna ƙin zumunta, muna cutar Maƙwabta, mai ƙarfi abincinsa mara ƙarfi. Muna nan cikin haka, har Maɗaukakin Sarki Allah ya aiko mana da manzo daga cikimmu. Manzo wanda muka san asalinsa, da gaskiyarsa, da riƙon amanarsa, da kyaun halinsa. Ya zo ya kira mu ga mu bi Allah, mu kaɗaita shi. Ya ce kadamu tara shi da kowa. Ya umurce mu da yin salla, da ba da zakka, da yin azumi. Ya dai bayyana mana al'amuran musulunci. Muka gaskata shi, muka yi imani a gare shi. Muka bi shi ga saƙon da ya zo da shi daga Ubangiji. Muka haramtu daga abin da ya haramta a gare mu. Muka halattu ga abin da ya halatta a gare mu. Ganin haka fa sai jama'armu, waɗanda ba su ba da gaskiya da shi ba, suka ƙulla gaba da mu, suka yi ta ba mu azaba, suka yi ta fitinarmu ga addinimmu. Suka yi ta ƙoƙari su hana mu bauta wa Sarki Allah, su mai da mu ga bauta wa gumaka. Abubuwan ɓarna da da mu ke yi, yanzu

muka bari, duk suna ƙoƙari su sa wai mu koma gare su. To, da suka rinjaye mu, suka tsananta zaluntarmu, suka tsananta matsi a gare mu, suka hana mu sakewa ga ibada ta hanyar addininmu, sai muka fito, muka nufo ƙasarka, muka zaɓe ka, muka bar kowa, muka kwaɗaita da mu maƙwabtace ka, muka yi fata mun tsira-daga zalunci, tun da mu ke ƙarƙashin inuwarka, ya wannan sarki mai arziki".

Daga nan Sarki Najjashi ya karɓa masa ya ce, "To, kana da wani abu daga cikin saƙon da Sarki Allàh ya aiko manzon nan naku da shi ?"

Ja'afaru ya ce, "I", ya karanta masa ayoyi daga cikin surar Kahe. Yana karantawa sai aka ga sarki na kuka. Ya ji abin da wannan Annabi ya kawo bai zama kishiya ba ga abin da addininsa na Kirista ya kawo. Sai ya juya ga manzannin Kuraishawa yace musu, "Ku tafi, ba ni ba ku !" Aka watse, manzannin suna masu baƙin ciki.

Da gari ya waye manzannin nan suka yi shawara, sai suka ce wai za su gaya wa sarkin cewa Musulmin na ce wa Annabi Isà bawa. Sabo-da haka suka biɗi a sake kai su ga sarki. Suka ce suna da sauran magana. Aka isa da su, suka yi gaisuwa, sa'an nan suka ce masa, "Ya wannan sarki mai arziki. Ai ba ka san abin da Musulmin nan ke ce wa Isa ɗam Maryama ba ? Babbar magana ce. Aika su zo, ka tambaye su, su gaya maka da bakinsu ka ji".

Nan ɗanan sarki ya aika aka kira baƙin nan, ya tambaye su, "Me ku ke ce wa Isa ɗam Maryama ?" Sai Ja'afaru ɗan Abu Ɗalib ya karɓa ya ce, "Muna ce masa abin da Annabimmu ya gaya mana ne na daga labarinsa. Ga shi. Shi Isa ɗam Maryama, bawan Allah ne, kuma manzon Allah ne, kuma ruhin Allah ne, kuma kalmar Allah ce wadda ya jefa zuwa ga Maryama".

Da jin haka sai zuciyar sarki ta yi fari. Ya dubi Musulmin nan ya ce musu, "Ku tafi duk inda kuka ga dama a cikin ƙasata, kuma tare da aminci !" Ya kwashi kyautar da manzannin can suka zo da ita, ya ba su abinsu ya ce, "Ga kayanku, ba na bukata. Ni sa'ad da Allah ya aza ni bisa wannan gado, bai karɓi rashawa ba daga gare ni, balle ni kuma ni karɓi rashawa don ina bisa gadon". Sai suka yi waje, suka bar ƙasar. Musulmi kuwa suka zauna ƙarƙashin inuwar wannan sarki, adali, cikin mafificin gida, tare da mafifitan maƙwabta.

## Musuluntar Sayyidina Umar

Duk har ya zuwa wannan lokaci, Sayyidina Umar bai musulunta ba tukuna. Hasali ma yana cikin manyan maƙiya musulunci. Zaman Sayyidina Umar kuwa a haka maƙiyi, abu ne ba ƙarami ba. Domin shi Sayyidina Umar mutum ne ƙaƙ-ƙarfa, ƙarfi irin yadda sai Wane da Wane ke da shi haka. Tsaya ka ji abin mamaki. Shi Sayyidina Umar, yana da wata 'yar'uwa 'yar Haɗɗabi, watau tsohonsu ɗaya ke nan da Sayyidina Umar. Ita 'yaruwar ashe ta musulunta, mijinta ma Sa'idu Ibn Zaidi shi ma ya musulunta. Amma duk wannan labari shi Sayyidina Umar bai sani ba. Su kuma duka biyu suna jin tsoron Sayyidina Umar ɗin ainun, saboda haka suka riƙa ɓoye masa cewa su sun musulunta.

Ana nan ran nan sai al'amarin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya cika wa Sayyidna Umar ciki. Sai ya zaro takobi, ya riƙe shi tsirara, ya fita biɗar Annabi. Aka ce masa suna can sun taru, su talatin da tara suna ibadarsu a gindin tsaunin Safa. Aka ce masa har su Hamza, ɗan Abdul Muɗɗalibi, da Sayyidina Abubakar, da Sayyidina Aliyu ɗan Abu Dalib duk suna can.

Sayyidina Umaru ya nufi wurin fagam fagam, da takobi tsirara, idanunsa duk sun yi ja. Sai ya gamu da Nu'aimu ɗan Abdullahi. Nu'aimu ya tambaye shi, "Ina zuwa haka, ya Umar?" Sayyidina Umar ya ce, "Za ni wajen Muhammadu ɗan yaron nan, wanda ya rarraba al'amuran Kuraishawa, ya aibanta addinimmu yana zagin-allolimmu, in je dai in sare shi, kowa ya huta. In ya so abin da duk zai auku, ya auku!"

Sai Nu'aimu ya ce masa, "Wallahi ya Umar, zuciyarka ta ruɗe ka. Ba ka komawa gidanka tukuna ka gyara shi kafin ka fito gyaran waje?" Sayyidina Umar ya ce, "Me zan gyara a gidana?" Nu'aimu ya ce masa, "Ba ka sani ba danginka, su Wane da su Wane, har da 'yar'uwarka duk sun musulunta. Suna bayan Annabi ne, ba bayanka ba?"

Daga nan wurin, Sayyidina Umar bai yi gaba ba, sai ya juya gida da hanzari. Yana zuwa ya tasam ma inda 'yar'uwarsa ta ke, sa ya ji wani malami wai shi Habbab yana karanta mata Alƙur'ani. An ce a cikin surar "Dahe' su ke. Da suka ji motsin Sayyidina Umar yana zuwa, sai Amina ta ɓoye Alƙur'ani kada ya gani. Ashe tun yana waje ya riga ya ji karatun.

Da ya shigo ya fara tambayarsu, "Wai kun musulunta ?" Sai surukinsa ya yi tajin tajin ga ba da amsa. Da Sayyidina Umar ya lura, sai ya hau shi da duka. Yar'uwarsa ta zabura ta shiga tsakani, ita ma ta sami nata. Daga nan sai ita ta ce da Sayyidana Umar, "Ya ɗan'uwana, musulunta dai, mun musulunta. Mun yi imani da wannan addini na gaskiya, kuma mun yi imani da manzon da ya kawo shi. Daɗa abin da za ka yi da mu kuma duk sai ka yi ! Ba abin da zai warware imanimmu !"

Wannan jawabi ya sa jikin Sayyadina Umar ya yi sanyi. Ya karɓi surar da su ke karatu Suratul'Dahe, ya fara karanƫawa, jikinsa na sanyi. Daga nan ya ce, "Wannan shi ne abin da Muhammadu ya zo da shi ?" Suka ce, "I". Sai ya ce, "Ku nuna mini inda shi ke !"

Sayyadina Umar ya tashi da ƙansa, ya iske Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Da Annabi ya gan shi, sai ya yi zaton ya zo ne da niyyar cuta domin kuwa Annabi ba ya zaton Umar zai zo gare shi da wata niyya a lokacin, ba ta cuta ba. Amma Aflalul Mursalina, bai kula ba, sai ya buɗe baki ya ce masa, "Ya ɗan Haɗɗabi, lafiya ka zo a wannan lokaci ?"

Ba abin da ya fito bakin Sayyadina Umar sai aka ji ya ce, "Na zo ne don in yi imani ga Sarki Allah, da manzonsa. Kuma in yi imani da abin da manzon nan ya zo da shi". Annabi ya ba da amsa da hamdala ga Ubangiji, sa'an nan ya ce, "Ba shakka Allah ya shirye ka ya Umar". Sai Annabi ya shafi ƙirjinsa shi Sayyadina Umar, ya yi masa addu'ar tabbata cikin musulunci. A wannan lokaci, lokacin sallar azahar ta yi. Jiya Annabi ya roƙi Allah ya ƙarfafa addininsa da ɗayan Umar biyu, ko dai Umar Ibn Hisham watau Abu Jahali, ko kuwa wannan Umar Ibn Haɗɗab, Allahu Akbar ! Ashe Allah ya karɓa ! Umar Ibn Haɗɗab shi zai zo.

To, da gama musuluntarsa, aka umurci Bila a yi kiran salla a yi zahar. A lokacin a ɓoye su ke yin kiran salla. Da Sayyadina Umar ya gani, sai ya ce, "Mene ne haka ?" Sai ya ce, "Wallahi ba mu ɓoye abin da Allah ya bayyana". Sai ya hau soro, ya yi kiran salla, kowa ya ji. A nan ya sami laƙabinsa na Faruƙu. Watau mai rabe shiriya da ɓata.

Wannan al'amari ya firgita Larabawa. Domin a da ana can ana jira zai zo da kan Annabi. To, shi kuwa Sayyadina

Umar da ya tashi daga nan gaban Annabi, bai zame ba sai gidan Abu Jahali. Da ganinsa Abu Jahali ya tarye shi da murna. Yana cewa, "Maraba maraba da ɗan 'yaruwata, lafiya?" Sayyadina Umar ya ce, "Na zo ne in gaya maka ni na musulunta. Na yi imani da Allah, na yi imani da manzonsa Muhammadu. Na kuwa gaskata abin da ya zo da shi."

Da ji sai Abu Jahali ya bugo ƙofa da ƙarfi ya rufe, kamar zai buge fuskar Sayyadina Umar da ita ƙofar. Ya ce da Sayyadina Umar, "Allah ya munana ka, ya munana wannan baƙin labari da ka zo mini da shi." Kun san fa da su Sayyadina Umar da su Abu Jahali a da ɗanyen ganye a ke yi, domin kuwa su ne manyan jigogin Kuraishawa maƙiyan Annabi.

A wannan lokaci fa al'amari ya ƙara ruɗe wa Kuraishawa. Ga dai Sayyadina Hamza da Sayyadina Umar sun musulunta. Musuluntarsu kuwa mun gaya muku ba ƙaramin al'amari ba ne. Manyan jigogi ne na kafirci suka koma jigogin musulunci, manyan maƙiya ne, suka koma manyan masoya. Abu na biyu kuma, hasali a ko wace rana kiran Annabi sai ƙara shiga ya ke yi cikin kunnuwan jama'a. Ganin haka fa sai maƙiyansa suka tashi, suka koma ga Abu 'Dalib da hushi, suka ce lalle lalle ya yi wa Annabi faɗa, ya bar abin nan da ya ke yi tun da wuri. Suka tsananta alkawarinsu na irin azabad da zai jawo idan bai bari ba.

Abu 'Dalib ya kira Annabi ya ce, "Ka ji abin da dattijan nan suka ce," Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata gare shi, ya karɓa ya ce, "Ai ni kalma guda kawai na ke so su faɗa. Su ce, "La'ilaha Illallahu, kuma su daina bauta wa gumaka."

Sai dattijan nan suka tafa hannu suka ce, "Kai so ka ke yi duk allolimmu ɗa mu ke bauta wa masu yawa, mu watsad da su, mu koma ga bauta wa Allah guda ɗaya tak?" Sai taro ya watse, watau sun ji maganar wauta, maganar ban haushi! Ba su sani ba wautar gare su ta ke.

### Sabuwar Shawara Ta Azaba

Wannan lokaci kam, in dai waɗanda ba su ba da gaskiya ba ga Annabi, suna da wani lokaci da za su kira, rikitacce, to, wannan shi ne rikitaccen lokacinsu. In sun duba sai su ga al'amarin Annabi, maimakon ya riƙa ci baya yadda su ke so

su gani, sai ci gaba gaba ya ke ta yi. Ga jama'arsa a ƙasar Habasha, sun so a koro su, amma sai ƙara samun aminci su ke yi. Ga manyan ƙasa su Sayyadina Abubakar, su Sayyadina Usmanu, su Sayyadina Ali duk sun ɓi shi. Irinsu kuma sai ƙaruwa su ke yi, zuwa gare shi.

Saboda haka, sai manyan kafiran-nan, su Abu Jahali suka yi shawarar hudo da wata hanya ta yi wa Annabi da mabiyansa azaba. Suka rubuta takarda, suka yi doka, kada kowa ya sake sayen wani abu daga waɗanda suka musulunta. Kada kuma kowa ya sake sayar musu da wani abu. Ko wanzamai kada a kuskura a ga wani wanzami yana yi wa Musulmi aski. Hasali ma dai kada wani ya sake ba wanda ya bi Annabi aure. Kada kuwa wani ya kuskura ya auro 'yarsu. Wannan doka suka ce ta game har da dangin Annabi Bani Hashim waɗanda ba Musulmi ba, don suna taimako.

Manya duk suka sa hannu, aka kafa wannan doka a 'Dakin Ka'aba. A cikin wannan lokaci ne, ran nan Abu Lahabi ya fito, sai ya gamu da wani, wai shi Hakimu da 'yar alkama, ya nufi unguwar Bani Hashim, watau inda Musulmi su ke, inda aka hana shiga da abinci. Shi kuwa ya yi nufi ne ya kai wa aminiyarsa Hadijatu, ɗiyar Huwailadi, don ita ta musulunta, amma shi bai musulunta ba. To, duk da haka yana tausayinta, ka san zumunta.

Da Abu Lahabi ya gan shi, sai ya ce, "A, a, a, za ka kai musu abinci ko, to, na kama ka! Sai kuwa na kunyata ka a garin nan." Suna cikin haka sai ga waɗansu cikin kafiran Makka, suka taru, suka riƙa ba Hakimu kashi. Ka ji irin halin da Musulmi suka zauna a ciki, har wajen shekara biyu.

An ce, a cikin wannan lokaci ne, da Abu Lahabi ya matsa ga Annabi, sai surar Tabat yada ta sauka. Ciki aka yi maganarsa shi Abu Lahabi da matarsa. To, da matar ta ji, ita kuwa ana kiranta Ummu Jamila, sai ta ɗafi ta ɗauko wani dutse ta nufo 'Dakin Ka'aba da shi, tana biɗar Annabi. Da ta zo ta iske yana ciki, tare da Sayyidina Abubakar. Amma da ta duba, sai Allah ya makantad da ita daga ganin shi Annabi. Sai Sayyidina Abubakar kawai ta gani. Ta tambaye shi, "Ina abokinka, na ji an ce yana zagina? Ya yi arziki da na iske shi, da wannan dutse na kwaɗa masa a baki!" Ta juya tana zage-zage.

Haka dai duk wanda ya musulunta ya ke zaune a Makka a

lokacin. Da mutum ya ce ya musulunta, shi ke nan wannan ya jefa kansa cikin azabar dangi. Amma kuma abin mamaki, wannan azabar ba ta hana mutane musulunta ba, sai ma ta zama kamar ita azabar ke ƙara turo mutane zuwa ga musulunta.

Kai, hasali dai im mun ce za mu ƙidaya azabobin da su Annabi suka sha, wurin ƙoƙarin iyad da wannan saƙo da Sarki Allah ya aiko Annabi da shi, sai mu ga ashe ba su ƙidayuwa. Ko hanya ce maƙiyan Annabi suka san yana binta, to, sai su sa ƙaya. Wata rana, in ya fito, har jifarsa a ke yi, da eho, ga mahaukaci ! Watau ku lura fa, wai mahaukaci ne shi, ba don yana bugun kowa ba, ba don kuwa yana zagin kowa ba, sai dai kawai don ya ce 'abu Sarki sai Allah. Kuma a bar bauta wa gumaka, a bauta wa Sarkin da ya hallicce su'.

Waɗannan azabobi iri iri, da Annabi ke sha, mun sha gaya muku cewa ba gare shi kawai azabobin suka tsaya ba, har ga dukan waɗanda suka ba da gaskiya. Wani maƙeri wai shi Habbab, wanda ya musulunta, ya shahara kuma ga ibada, sai Kuraishawa suka kama shi ran nan, suka kwantad da shi bisa garwashin wuta, sai da ta mutu. Wai laifinsa kawai ya yi imani da cewa 'Babu Sarki sai Allah, kuma Muhammadu manzonsa ne'.

Wani bawa kuma, mutumin ƙasar Habasha, wanda a ke kira Bila, a rana aka kwantad da shi, aka kawo dutse mai zafi aka aza a jikinsa, aka ɗauko bulala aka yi ta tsala masa, wai sai ya warware imaninsa, ya ce ya bar musulunci. Amma shi Bila, maimakon bakinsa ya fitad da wata murya ta kuka, sai kawai ya yi ta cewa, "La'ilaha illallaha, Muhammadu Rasulullahi". Ana tsala masa bulala, yana faɗar haka,. Watau shi kukansa ke nan. Allahu Akbar ! Haushi ya ƙara kama Kuraishawa. Sai suka ɗaura masa igiya, suka yi ta jansa a ƙasa. Amma duk dahaka kalmar da ke fita bikin Bila ba ta sauya ba. Ita dai ke nan guda : "La'ilaha Illallahu Muhammadu Rasulullahi". Ka ji Bila babban bawa ! Sarkin Ladanan Musulunci !

Hasali dai wani bawa ma da a ke kira Yasir, taga shi jama-'ar Makka suka yi kamar takarda, wai kawai don ya yi imani. 'Ba Sarki sai Allah, Annabi Muhammadu kuwa manzonsa ne' Ba maza ba, har mata waɗanda suka musulunta haka suka yi ta shan azaba. Wata da a ke kira Sumayyaka she ta Dungum aka yi.

Ya jama'a, wannan al'amari na Annabi bai isa gayar mu'ujiza ba abar mamaki? Ga wuta ta kama za ta cinye kafirci, amma kafiran Makka sun kaša bice ta, sai kewaye kewaye su ke yi ga hayaƙi, wutar kashe kafirci kuwa sai ƙara haɓaɓɓaka ta ke. Amma kuma a wata fuska ai ba bin mamaki ba ne. Domin Maɗaukakin Sarki Allah ya rigaya ya sanar, a cikin Al'ƙuraninsa mai girma cewa, ya yi alkawarin zai cika wannan haske nasa ga duniya ko da matsafa ba su so ba!

## Hijirar Sayyidina Abubakar Ta Fari

Ana cikin haka, azaba da fitina suka yi wa Sayyidina Abubakar yawa, sai ya biɗi izni daga Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ce yana so ya fita ƙauye ya shaƙata. Annabi ya ba shi izni, ya shirya ya fita. Yana cikin tafiya, ya yi kusan kwana biyu rabonsa da Birnin Makka, sai ya gamuda wani danginsa, shugaban wata kabila. Da ya gamu da shi, ya ce masa, "Ina zuwa ya Abubakar?" Sayyidina Abubakar ya karɓa ya ce, "Jama'armu su suka fito da ni, sun dame ni da azaba, sun tsananta matsi a gare ni". Shugaban nan ya ce, "Sabo da me. Kai da na sani mai taimakon dangi, mai aikata ayyuka nagari. Mu koma gida ni zan ɗauki amanar kiyaye ka!" Suka komo gida. Shugaban nan ya tashi a bainar jama'a, ya ce, "Ya ku jama'ar Kuraishawa, ku shaida na ɗauki amanar kiyaye Abubakar. Kada wani ya sake taɓa shi sai fa in da niyyar alheri ne". Shi ke nan, Sayyidina Abubakar ya sami 'yar kwanciyar rai.

To, shi Sayyidina Abubakar yana da masallaci a ƙofar gidansa. Kullum in ya shiga ciki yana salla, yana karatun Alƙur'ani, sai ya riƙa kuka, domin kuwa ko da ma shi mutum ne mai sanyin rai. In yana sallan nan yana kuka, sai yara, da mata, da bayi, su zo su rarraɓe suna kallonsa, suna nuna alamar jin tausayi a gare shi. Ran nan, wani daga cikin kafiran Makka yana wucewa, sai ya ga haka. Bai zame ba sai gidan shugaban can da ya ɗauki amanar kiyaye Sayyidina Abubakar, ya ce masa, "Ya Wane, in ji dai ba ka suhurto Abubakar ba ne, don ya zo ya cuce mu Shi fa wani irin mutum ne in ya fara salla, yana karatun abin nan da Muhammadu ya zo da shi, sai ya riƙa kuka. To, ina tsoro kada yarammu, da matammu, da bayimmu, da jama'armu, masu raunin zuciya, su riƙa jin tausayinsa. Gaya

masa in zai yi sallarsa ya yi a cikin gidansa, amma ba a fili ba".

Sabo da haka shugaban ya tashi, ya tafi ga Sayyidina Abubakar ya ce masa, "Ya Abubakar, ni fa ban yi alkawarin kiyaye ka ba don ka cuci jama'armu. Riƙa shiga cikin gidanka kana sallarka da ibadarka yadda ka- ga dama". Sayyidina Abubakar ya karɓa ya ce, "Im ba haka ba kuwa, im mayar maka da alkawarinka na kiyaye ni, in yarda-da alwarin kiyayewar Sarki Allah".

Shugaban nan ya ce, "To, na fitad da hannuna gare ka !" Ya ce wa jama'a, "Ku sani, daga yau na fitad da hannuna ga Abubakar. Abin da ku ke so ku aikata a gare shi duk ku aikata. Ba ruwana da shi !" Sayyidina Abubakar ya yi godiya ga Allah.

## Takardar Alkawarin Azaba

Ana nan haka, sai wadansu manya, mutum biyar daga cikin kafiran Makka, suka duba, suka ga azaban nan da su ke gwada wa Bani Hashim, watau dangin Annabi, ta dai isa hakanan ! Ran nan an taru a Dakin Ka'aba, wani daga cikin mutanen nan biyar ya yo ƙuna baƙin wake, ya miƙe, ya ce, "Ya ku jama'ar Makka, ku lara fa, mu duka muna cin abinci, muna sanya tufafi. Ga Bani Hashim can mun hana a sayi wani abu daga gare su, mun hana a sayar musu. Wallahi ni kam ba na zaunawa, sai kun keta takardar alkawarin nan, azzaluma !"

Farat sai Abu Jahali ya miƙe, ya ce, "Karyarka, Wallahi mu ba mu keta wannan takarda !" Daga nan sai wani ya karɓa wa Abu Jahali ya ce, "Kai ne maƙayarci. Da ma mu ai ba mu goyi bayan a rubuta wannan takarda ba, ku ne kuka-yi !" Jama'a da dama suka ce, "Haka ne fa, da ma mu-ba mu goyi bayan a rubuta wannan takarda ba !" Sai Abu Jahali ya ce, "Wannan lalle munafinci ne aka ƙulla da dare ! Ba a kawo maganan nan wajen shawara ba".

Ba wani tsaye tsaye, sai wani dattijo, da a ke kira Muɗi'imu ya tashi ya nufi inda takardar ta ke a kafe, a bangon Dakin Ka'aba. Ya miƙa hannu zai keta, sai ya iske ashe ma gara ta rigaya ta cinye ta. Ba abin da ya ragu cikin rubutun sai kalma biyu, ga su "Biismika Allahumma" ma'anarsa "Da sunanka ya Ubangiji".

**Hana Jama'a Shiga Musulunci**

A kullum, yadda Annabi ke famar kiran jama'a zuwa ga musulunci, haka kafiran Makka ke bi hanya hanya, suna hana jama'a karɓa kiran Annabi. Wata rana wani mutum daga cikin kafiran Makka ya shiga gari, ya ce wai yana bidar Annabi ne. Kuraishawa suka ce, "Meka ke bida gare shi ?" Baƙauyen nan ya ce, "Na zo ne im musulunta". Da 'yanuwansa, kafiran birn suka ji haka, sai suka ce masa, "Me, ka zo ka musulunta? Hala ba ka sani ba, Muhammadu fa wai ya haramta zina" Baƙauyen nan ya ce, "Ai ni wannan da ma ba na cikinta. "Suka sake ce masa, "Ban da wannan kuma ai wai ya haramta giya" Sai baƙauyen ya ce, "A'a, a, tun da sh ke haka ne, sai in koma gida, bana, in yi ta sha, in yi ta sha sai na ƙoshi da ita, in ya so baɗi in zo im musulunta". Shi ke nan ai ya juya. Shaiɗan ya ribaci wannan. Masu tarihi sunce wai shi wannan baƙauyen, daga wannan shekara, Allah bai nufes hi da kaiwa baɗin ba.

To, a can baya kun karanta labarin musuluntar Sayyidina Umar da su Hamza. Mun gaya muku musuluntarsu ba ƙaramar nasara ce ba Annabi ya samu. Tun ran da Sayyidina Umar ya musulunta, sai labari ya bazu ko ina. Har sahabban Annabi waɗanda muka ba ku labarin zuwansu ga sarkin Habasha suka sami labari. Suka ji ma an ce wai sabo da musuluntar Sayyidina Umar, yanzu fitina ta yi sa uƙi ga Musulmi. Domin ko wane mutum na Makka yana shayin Sayyidina Umar Suka ji an ce yanzu Musulmi sun sami damar su fito fili su yi salla. Sabo da jin wannan labari, da yawa cikinsu, su waɗanda ke ƙasar Habasha, sai suka yiwo sallama da Sarki Najjashi, suka dawo gida. An ce-da ma a cikinsu, duka duka-wata kamar uku suka yi a can. Kun ga watau ashe ko da su ke can cikin salama, su a ransu sun ɗio so su dawo Makka kusa da Annabi cikin azabar, yadda dai muka ce muku tun ran fitarsu.

**Abu Jahali Na Tsoron Annabi**

Abin mamaki ya tabbata ga irin zaman Abu Jahali da Annabi. Da farko dai duk cikin kafiran Makka, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ba wanda ke gwada masa ƙiyayya kamar Abu Jahali, ga shi kuwa ɗanuwan mahaifinsa. Kamar yadda muka nuna a juzu'i na farko, Amma

kuma abin mamaki shi Abu Jahali, ba wanda ya ke tsoro kamar Annabi.

Wata rana, wani Balarabe daga cikin mutanen ƙauye waɗanda ba su musulunta ba, ya zo Birnin Makka da raƙuminsa, sai Abu Jahali ya saya. Ba ƙauye ya yi bi, ya yi bi, kuɗi suka ƙi fita. Sai ran nan ya fito zuwa bin bashi. Ya nuho wajen Kakin Ka'aba, sai ya ga taron mutane a kusa da Ɗakin. Sai ya ce musu, "Ya ku jama'ar Kuraishi, wa zai taimake ni ga Abu Jahali? Ni baƙo ne, matafiyi. Ya sayi raƙumina, amma ya hana ni biya."

Ashe taron mutanen nan duk na kafiran Makka ne, 'yam birni. Cikinsu kowa ya san ƙiyayyar da ke tsakanin Annabi da Abu Jahali. Saboda haka, da suka hanga can, suka ga Annabi zaune, sai suka ce wa baƙauyen nan, "Je ka, ga mutum can zaune, ka tambaye shi, zai ƙwatam maka kuɗinka." Ba su ce haka ba, sai don lalata, wai don su gama faɗa.

Shi baƙauye bai san da niyyar lalata suka tura shi ga Annabi ba. Hasali ma shi bai san ko wane ne ba. Sai dai ya nuho gare shi ya ce masa, "Bawan Allah! Abu Jahali ne ya sayi raƙumina ya ƙi biya. Na kawo ƙuka ga mutanen can na zaune ko na sami wanda zai taimake ni, in sami kuɗina. Sai suka nuno ka, suka ce in zo gare ka, wai kai ne za ka iya taimakona."

Ba da wata tsayawa ba, sai Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya miƙe, ya ce wa baƙauye, "Mu tafi gidansa!" Da mutanen can na zaune suka ga Annabi ya nufi gidan Abu Jahali tare da baƙo, sai suka bi su, wai su je su yi kallon faɗa. Da zuwan Annabi sai ya buga ƙofar gidan Abu Jahali! Abu Jahali ya ce, "Wane ne?" Sai Annabi ya ce, "Muhammadu ne, fito!" Sai Abu Jahali ya fito. Yana arba da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sai jikinsa ya ɗauki rawa. Annabi ya buga masa tsawa ya ce, "Biya wannan mutum haƙƙinsa!" Abu Jahali, jiki na rawa, ya karɓa ya ce, "To." Ya shiga ya kawo masa. Baƙauye ya dubi Annabi ya ce, "Ba shakka akwai gaskiya ga sha'aninka!"

Mutanen da suka biyo, don su yi kallon faɗa, suka yi ta mamaki. Suka ce wa Abu Jahali, "Allah wadanka, ka ba mu kunya. Me ka gani ya ba ka tsoro haka?" Abu Jahali ya ce, "Ku ne za a ce wa Allah wadai ba ni ba. Ku kuna nan ba ku san abin da na gani ba. In gaya muku, Wallahi, da Muham-

madu ya buga ƙofata na fito, sai na ga amalen raƙumi a gabana. ya yage haƙora kamar jira kawai ya ke yi in yi jinkiri ya halaka ni!" Mutanen suka yi ta yi masa dariya.

Irin wannan taimako ga musakai, da matalauta, da marayu, da maƙwabta, da matafiya, da waɗanda aka zalunta, shi ne irin aikin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Saboda haka duk wurin da ya zauna, sai ka ga matalauta sun zo sun kewaye shi. Kamar dai cewa su ke yi, ga mataimakimmu. Su kafiran Makka kuwa, idan sun ga haka, sai su riƙa nuna Annabi da baki, suna zunɗensa suna cewa, "Dube shi, ba ya da abokai sai matalauta. Wai daga irin waɗannan ne za mu ji gaskiya da shiriya. Ka san dai da saƙon nan nasa na alheri ne, da mu ne abokansa, ba waɗannan matalauta ba."

## Mai Gaskiya Yana Tare Da Allah

Jama'a ku lura da wannan zance, kun ji watau irin wannan abu da Annabi ke yi, su ne a wannan lokaci a ke sanyawa cikin halaye marasa kyau. Abin mamaki na biyu kuma shi ne wannan Ku dubi yadda Annabi ya ke, a Makka aka haife shi, ga uwa, ga uba, ga dangi, ba daga sama aka sako shi ba, balle a ce wani mala'ika ne dodo. Ya taashi kuma ƙa maraya, ba kuma wani tajiri ba, ga shi shi kaɗai ba sanda ba bulala, amma duk da haka al'umma duk tana tsoronsa! Wannan al'amari ya isa ya zama mana babbar aya.

Da ma, ko a yanzu kuka lura, sai ku ga ashe haka Allah ya shirya al'amarin zaman 'yan Adam, tun can da har zuwa yanzu. Duk mutum in dai ba ya da gaskiya, kome ilminsa, kome tsufansa, kome ƙarfinsa, kome ƙarfin halinsa, kome girman sarautarsa, sai ka ga a tsorace ya ke zaune. Da ɗan yaro ya kaɗa masa ganye sai ka ga jiki ya ɗauki rawa, to, ba gaskiya! Wanda kuwa ke tsaye bisa gaskiya, kome rauninsa, to, ana tsoronsa. Ya yiwu a yi ƙoƙari a ɓoye tsoron, amma duk ƙarya ne tsoron na nan. Yaya kuwa za a kasa jin tsoron mai gaskiya, wanda kullum yana tare da Allah?

Bai kamata mu wuce wannan wuri ba, sai mun gaya muku wani labari, na cikin wannan tarihi na Annabi. Kila ku ɗauki labarin mai ban dariya, kila kuwa ku ɗauke shi mai ban mamaki. Yana nan dai cikin mashahurin littafin nan na siyari, wanda mu ke biye, wanda a ke kira Ibn Hisham.

An ce, wata rana, wani mutum wanda a ke kira 'Dufaili ya yi niyyar zuwa Makka daga garinsu. Shi kuwa ɗan manyan mutane ne. Da zai fito, sai iyayensa suka ce masa, "In ka shiga Makka, ka guji saduwa da wani mutum yana nan, wanda a ke kira Muhammadu. Zancensa kamar sihiri ne. In ya yi wa mutum shi, ka ga ya raba mutumin nan da danginsa, kai, kai, sai ma ya raba mutum da tunaninsa kansa. To, in ka shiga birni, kada ka kusance shi. In kuwa har ka ci karo da shi, to, babban alheri a gare ka, shi ne kada ka yi magana da shi. Kuma kada ka saurari jawabinsa". Ka ji, watau gaskiya ita a ke gudun kada a ji.

Shi ke nan, sai 'Dufaili ya shigo gari. Ga shi nan, ga shi nan, sai 'Dakin Ka'aba. Kwaram sai ya ci karo da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana wa'azi a can. Karaf sai zancin Annabi ya faɗa kunnen 'Dufaili. Ya ji magana ta shige shi. Sai ya ce, "A'a, me ya sa akahana ni sauraren wannan mutum. Ga maganarsa kuwa da daɗin saurare. Bari im matsa kaɗan, in na ji maganar kamawa cikin zancensa in kama, wadda na ji ba ta kamawa ba in watsar". Sai ya bi Annabi. Me ku ke zato ya faru, ai bai rabu da shi ba, sai a kan ya musulunta. Da 'Dufaili ya koma gida sai ya shiga kiran al'ummarsu zuwa ga musulunci. Ya kuwa musuluntad da mutane da yawa nasu. ka ji aikin manya ɗan Abdullahi : Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana !

## Abu 'Dalib Ya Rasu

Annabi Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a, gare shi, yana cikin wannan hali na karɓar azaba daga Kuraishawa daga shi har mabiyansa, kamar yadda kuka karanta a baya, har ya shekara kamar goma da saukar annabci a gare shi. To, a sa'ad da ya shekara kamar goma ɗin nan a annabci, sai abubuwa biyu manya, na baƙin ciki suka auku a gare shi. Na farko dai amminsa Abu 'Dalib ya rasu. Shi ne muka ce ya ɗauki garkuwar taimakonsa tun rasuwar Abdul Muddalibi. Kuma a lokacin ne Hadija babbar uwargidansa ta rasu. It kuwa ce mace wadda ta fara karɓar musulunci a duniya. Wannan shekara, har Larabawa na kiranta shekarar baƙin ciki. Kuraishawa kuwa, waɗanda ba su musulunta ba, sai murna, wai garkuwar Muhammadu ta faɗi ! Allahu Akbar, ba su sani ba, Allah shi ne

garkuwar. Shi ya saukad dà musulunci, shi kuma ne da zatinsa ya yi alkawarin tsare abinsa !

Wannan rasuwa ta sanya Annabi baƙin ciki ainun. Amma abin farin ciki, ashe ko da shi ke Abu'Dalib bai furta da baki ya musulunta ba, zuciyarsa ita ta musulunta tuni, ta-yi imani da Annabi da abin da ya kawo.

Mu juya ga Kuraishawa. A wajensu kam, a'uzu billahi, mina Shaiɗani rajimi ! Mun gaya muku rasuwar Abu'Dalib a gare su ta zama kamar gangami ne ta cewa, mai son cutar Annabi duk ya fito fili, garkuwa ta faɗi ! A cikin wannan lokaci, na farin cikin maƙiyan Annabi, har aturc su ke yi masa, idan ya fito yana kiran jama'a zuwa ga bauta wa Maɗaukakin Sarki Allah. Ran nan da ya fito aka watsa masa ƙasa a kai. Da ya dawo gida, sai ya ɗebo ruwa ya duƙa, 'yarsa na wanke masa, tana kuka. Sai ya ce mata, "Bari kuka, Allah yana kiyaye da ubanki !"

## Zuwan Annabi Birnin 'Da'ifa

Mu koma ga Aflalul Mursalina, shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a ruɓe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryawa ga tafarki madaidaici ! To, shi wane hali ya ke ciki a wannan shekara ta baƙin ciki ?

Me fa ya ke ciki ? Ai sai ma aka ga kamar rasuwar waɗannan masoya nasa guda biyu, ƙara masa himma ta yi ga iyad da saƙon Allah. Tsaya ka ji. Ana cikin wannan shekara ne ta baƙin ciki, ran nan shi da ya tashi, bai zame ba sai Birnin'Da'ifa. Annabi ya tafi can don ya kira su zuwa ga addinin musulunci.

A wannan gari 'Da'ifa, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya gamu da azabobi iri iri. Ya iske jama'ar da taurin kai kamar mutanen Makka. Tun buɗa bakinsa ma ga fara magana a gare su, da ya ce, "Allah ne ya aiko ni gare ka". Sai wani ya yi farat ya ce masa, "Allah ne ya aiko ka gare mu? Watau du kAllah ya rasa wanda zai aiko gare mu sai kai !" Wani ya karɓa ya ce, "Kai ma ka fi shi da ka ke karɓa masa. Ai ni ko magana da shi ba zan yi ba !"

Hasali dai da suka ji ya shiga bayanin addinin musulunci a gare su. Yana ce musu su gaskata Sarki Allah, su bar tsafi, su bar shan giya, su bar bizne 'ya'ya mata, su bar zalunci, su bar fashi, su bar miyagun abubuwa kaza da kaza da kaza. Maima-

kon ma su ƙyale shi, ya yi ta wa'azinsa in ya so kar su karɓa,sai suka koro shi. Suka sa yara suka biyo shi da jifa, jikinsa duk na jini sabo da rotse. Daga shi kuwa sai abokin tafiya guda Zaidu. Hasali dai, suka juyo, har Allah ya kawo su ga gonar waɗansu mutanen Makka, waɗanda a ke kira Utba da Shaiba, suka dakata a nan.

Ganin halin da su ke ciki, har masu gonar, Utba da Shaiba, suka ji tausayinsu, suka kawo musu abinci, inabi. Suka yi godiya. Bawan da aka aiko ya kawo musu abincin, ana kiransa Addas. Da miƙa musu abinci, sai Annabi ya shiga bayyana masa musulunci. Malam ka lura da wannan al'amari. Dubi fa halin da ya ke ciki ! Nan take bawan nan ya musulunta.

Daga wannan gonar, ina ka ke zato Annabi ya nufa? Kowa zai ce gida, don kuwa kowa zai ga in da shi ne da can ya nufa. Amma Muhammadul Aminu, Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana, shi ba gida ya nufa ba. Sai ya nufi wani wuri wai shi Nahla. A can kuma ya samu ya musuluntad da waɗansu manyan wuri. Wannan shi ya zama kamar share baƙin cikin abin da ya faru gare shi a 'Da'ifa na rashin samun kowa, ba na azabad da aka gwada masa ba. Wannan ba ya baƙin ciki da ita.

Wannan tafiya ta Annabi Muhammadu zuwa 'Da'ifa, tana ba ko wane malamin tarihi na duniya mamaki. Wani mashahurin Bature, Kirista, wanda ya yi suna ƙwarai ga sanin tarihin Annabi Muhammadu, ana kiransa William Muir, cikin ƙaron littafin da yarubuta da turanci, a kan tarihin Annabi Muhammadu, da ya zo ga wannan wuri, ga abin da ya ce, "Ba shakka akwai abin mamaki ga jaruntakar da Muhammadu ya nuna ga yin wannan tafiya zuwa 'Da'ifa. Mutum ya tashi shi kaɗai, ga shi ya san danginsa ma duk sun tsane shi, balle waɗansu, amma a nufi wani birni, na waɗansu mutane dabam, da sunan Allah a baki. Ya ce wai Birnin nan da ke bauta wa gumaka, shi zai kira shi kaɗai ga tuba da komawa ga bauta wa Maɗaukakin Sarki Allah ?" William Muir ya ce, "Ba shakka, wannan ya nuna ƙarfin imanin Muhammadu ga wannan kira da shi ke yi !"

### Isra'i

Bas hi yiwuwa ga mai rubuta tarihin Annabi duka ya wuce wannan wuri, bai taɓo babban labari da zam faɗa ba, wanda ya

auku ga Annabi, a cikin wannan shekara, shi ne labarin Isra'i. Labari ne wanda a da na ga kamar zurfinsa zai wuce zurfin tunonin irin mutanen da na ke rubuta wannan lirrafi dominsu, watau 'yan yara da mata da kamata, waɗanda ba su sami yin karatu mai zurfi ba. Amma duk da haka, darajar labarin Isra'i, da girmansa a cikin tarihin Annabi, ya fi ƙarfin a ƙetare shi, kome wuyar fahintarsa da yara za su yi.

Duk ko wane mashahururin littafi na siyari, tarihin Annabi, ba wanda ya ɓaɓa ga cewa cikin dare da a ke kira Daren Isra'i. Maɗaukaki Sarki Allah ya tafiyad da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, daga Masjidil Harami, Masallacin Makka, zuwa Masjidil Aƙsa, Masallacin Baitil Mikdasi. Daga nan kuma Allah a cikin ikonsa, ya ƙara tafiyad da shi zuwa sama. Shi a ke cewa Mi'iraji. Ku lura Allah ba a sama ya ke ba. Allah ba inda ba shi. Ya tafiyad da Annabi zuwa sama domin kawai saman ya nufa ya tafiyad da shi. Da ya nufi tafiyad da shi zuwa ƙasa ne, da can ya tafiyad da shi. Domin ga Annabi Musa, da shi ke shi a Dutsen'Durisinina aka nufi munajati da shi, a can aka yi.

Wannan labari na Isra'in Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi, za ka same shi a ko wane littafi da aka rubuta na tarihin Annabi, hasali ma ga shi nan a cikin Alƙur'anin Allah mai girma.

A maganar Isra'i mun gaya muku ba saɓani. Ga shi nan cikin Alƙur'ani. Abin da sahabban Annabi suka yi saɓani a kai guda ɗaya ne tak, shi ne, yalla da ruhi ne kawai Ubangiji ya tafiyad da Annabi zuwa sama a wannan dare, ba da gangan jikinsa ba, ko kuwa har da gangan jikinsa aka tayfid da shi ! Waɗansu sun ce da gangan jiki ne, waɗansu kuwa suka ce a'a, da ruhi ne, gangan jikinsa bai rabu da wurin da ya ke kwance ba.

A'ishatu, matar Annabi Muhammadu, sallallahu alaihu wasallama, ita tana cikin waɗanda suka ce da ruhi ne. Ta ce, "A daren da Annabi ya yi Isra'in, gangan jikinsa bai rabu da wurin da ya ke ba kwance.

Mu'awiyya kuma, ɗan Abu Sufuyana, shi ma in an tambaye shi labarin Isra'in nan ya kan bayyana cewa da ruhi ne, ba da gangan jiki ba. Sai dai fa abin da annabawa suka gani a mafarki kullum haka abin ya ke. Har shi Abu Sufuyana ya kan jawo ayoyin Alƙur'ani waɗanda ya dogara da su ga tabbatad da cewa

da ruhi Annabi ya yi Isra'i, ba da gangan jiki ba. Kamar aya ta 102 cikin sura ta 36. Abu Sufuyana ya ce, "Wahayi daga Allah ya kan zo ga Annabawa a farke, kuma ya kan zo musu a suna barci.". Watau a ƙaulinsa da na A'ishatu, matar Annabi, abin da Annabi ya gani a daren Isra'i a halin yana cikin barci ya gan shi da ruhinsa.

Iyakar inda za mu tsaya ga wannan magana ke nan. Iyakar sanin kowa dai a wannan dare na Isra'i Allah ya ganad da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, abin da ya ganad da shi, dada ko yana barci ne a lokacin, ko yana farke. Cikin haluluwan nan duka biyu kuwa ba wanda ya ke mabuwayi ga ikon Allah. Allah yana iya isra'i da shi a halin yana farke, ya tafiyad da shi da ruhinsa da gangar jikinsa. Allah yana iya isra'i da shi a halin yana barci ya tafiyad da shi da runinsa ya bar gangan jikinsa kwance bisa gado.

To, duk cikin halayen nan guda biyu, ko wanne ne aka yi isra'i da Annabi, in ka dubi al'amarin, sai ka san lalle akwai aya a ciki, wadda za ta ƙara shiryad da kai ga tabbatad da cewa lalle Maɗaukakin Sarki Allah shi kaɗai ya ke. Ba ya da abokin tarayya.

To, da dai Ubangiji ya ga sharri iri iri da azaba iri iri sun tasam ma Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sai ya saukad da aya ta 94 zuwa ta 96 ta cikin sura ta 10. Ciki aka umurci Annabi da ya iyad da abin da aka umurce shi, kuma aka ba shi izni ya bijira ga mushrikai. Aka kuma ƙara sanad da shi ana kiyaye da shi.

Ba shakka musulunci ya kawo babban sauyi ga tunanin 'yan Adam na lokacin. Yaya kuwa Kuraishawa za su kasa ƙin zancen Alƙur'ani, ga shi Annabi ya zo da shi, yana kiran mutane su yi imani da shi, alhali kuwa shi Alƙur'ani sai cewa ya ke yi su rabu da munanan abubuwa waɗanda suka ƙallafa wa kawunansu. Kuma shi Alƙur'ani ba ya bambantawa daga matalauta da masu arziki. Maimakon ya nuna cewa mai arziki, ko mai sarauta, ko jinin wane su suka fi daraja, Alƙur'ani sai bayani ya ke sani wanda ya fi ku taƙawa, shi ne wanda ya fi ku girma a wurin Allah. Ga ayan nan a suratul Hajarati ita ce aya ta 13, in kana so ka'ga lafazinta na asali. (Abin da a ke ce wa taƙawa shi ne bin abin da Allah ya umurce ka da yi, gwargwadon ƙoƙarinka da barin abin da ya hane ka.)

Tun sa'ad da aka umurci Annabi da ya fito fili ga kiran jama'a zuwa musulunci, sai ya kama bin hanyoyin fatake masu shiga Makka yana kiran baƙin nan zuwa ga karɓar musulunci.

Ban da wannan kuma, ko wace shekara, in Larabawa na ƙasa ƙasa sun taru a Makka, domin yin irin hajjinsu na lokacin, shi kuwa sai ya yi ta binsu yana kira ga bauta wa Maɗaukakin Sarki Allah. Ko yaushe Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbatá a gare shi, in ya tari ayarin fatake, yana yi musu wa'azi, sai Abu Lahabi ya riƙa bi, yana ƙaryatawa. Wata rana Annabi ya tsaya Mina kan hanyar fatake, kamar yadda ya saba, suna wucewa yana kiransu kabila kabila yana ce musu, "Ya ku kabilar Wane, ni manzo ne na Allah zuwa gare ku. Allah ya umurce ku da ku bauta masa shi kaɗai. Ku rabu da bauta wa gumaka, ku ba da gaskiya gare shi. Ni kuwa ku sani manzonsa ne, ku gasƙata ni. Ku bar ni har in gaya muku saƙon da ya aiko ni da shi zuwa gare ku."

Yana gamawa, sai Abu Lahabi da ke biye da shi ya karɓa ya ce, "Ya ku kabila kdza, kada ku yarda da maganarsa. So ya ke wai ku kwance bauta wa allolimmu su Lata da su Uzza, ku koma ga wannan sabon addinin da ya ƙago na bidi'a da ɓata. Kada ku yarda da shi, kada ma ku tsaya sauraronsa, ku wuce abinku, mahaukaci ne!"

La'ilaha illallahu, Muhammadan rasulullahi sallallahu alaihi wasallama. Malam, ka ji jawabin manyan kafirai! Ya Allah ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici.

A shekara ta 11 da saukar annabci a gare shi, a cikin taryar fatake da ya ke yi, sai ya gamu da Larabawa waɗanda suka fito daga Birnin Yasriba. Shi kuwa ko a sa'an nan mashahurin birni ne, ga shi nan arewacin Makka. Wannan birni, shi ne daga bisani aka riƙa kiransa Madina. Shi ne Birnin Madina na yanzu, wanda alhazai ke ziyarta. Allah ya nufa, tun fil azal, ashe nan ne zai zama fadar musulunci.

A cikin wannan gamuwa, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya samu ya musuluntad da waɗansu 'yam mutane kaɗan, daga cikin waɗansu kafirai, waɗanda suka zo daga Madina. Su waɗannan, su suka koma

da musulunci garinsu, Madina. Ta haka suka zama su ne suka fara seuka shi a can. Amma ko kafin su rabu, sai da suka ɗauki alkawari a gaban Annabi, cewa : Ba za su tara bauta wa Sarki Allah da bauta wa wani ba. Ba za su yi sata ba. Ba za su yi zina ba. Ba za su bizne 'ya'yansu mata ba idan sun haifa. Ba za su tafiyad da hannuwansu ba, ko ƙafafuwansu zuwa ga mugun aiki. Ba za su aikata wani abu mummuna ba.

Da suka yi wannan alkawari, za su koma, sai Annabi ya gama su da wani sahabi nasa wanda a ke kira Mus'aba ya ce ya bi su can Madina ya je ya ci gaba da bayyana musu addinin musulunci, su waɗannan da suka karɓa.

Da shekara ta kewayo kuma, waɗansu mutanen Madina, mutum kamar 73, har da mata biyu, duk su ma suka yi alkawarin sun karɓa kiran musulunci. Suka koma Madina da niyyar baza wannan saƙo. Ta haka saiwar musulunci ta sami kafuwa sosai a Madina. Alhali kuwa ga Aflalul Mursalina a Makka shi bai tafi ba.

Amma su kuma waɗannan Annabi ya sadu da su ne a wurin da ya sadu da na farko. Watau Aƙba. Sabo da haka su ma ba su rabu da shi ba, sai da suka ɗauki alkawari, aka sa hannu kamar yadda aka yi da ayari na bara. Sabo da haka ma ne a ke kiran wannan 'Alkawarin Aƙba Na biyu', kamar yadda a ke kiran wancan 'Alkawarin Aƙba Na Farko'. Su kuma waɗannan ga alkawarin da suka ɗauka : Mun yi mubaya'a, bisa ga mun ji, mun kuwa yarda. Mun yi mubaya'a, a cikin matsuwarmu da wadatarmu, a cikin son rammu da ƙin rammu duk mu dai za mu faɗi gaskiya duk inda mu ke. A cikin kiyaye al'amari na Ubangiji Allah duka, kuma ba ma tsoron zargin mai zargi".

To, ana nan, ana nan, a kuwana a tashi, sai kafiran Makka suka ga dai a ko wace safiya al'amarin Annabi sai ƙara ƙasaita ya ke yi, bisa ƙasaitarsa ta jiya. Sai suka taru, suka sake sabuwar shawara dai, kun san kullum sabuwa a ke sakewa. Suka yi alkawari a wannan shawara za a yi ta ta ƙare. Wai za su dai kashe Annabi ɗungum duk su huta.

Sai suka ceko wace kabila su kawo mutum guda, a taru, da dare a auka wa Annabi, a kashe shi. Ta haka, laifin kashe shi, sai ya zama an raba ko wace kabila ta samu. Suka ce in har suka kasheMuhammadu kuwa sun tabbata sun kashe wannan sa

hon addini ke nan. addinin musulunci. Su sun yi imani a ransu, cewa Muddin Muhammadu ya mutu. musulunci kuwa ya mutuke kan Domin su sun yi imani a ransu cikin mabiyansa ba mai ƙarfin tarbar tumbin dukan kabilun nan na Makka in sun gama kai. Malam, lura da wannan jawabi. Me ka fahinta a ciki ? Ka lura da huruci wanda ya tabbatad da ainihin tsoro da Sarki Allah ya aza cikin zuciyar ko wane Balarabe game da Annabi. Ka ga su sun yarda shi yana iyar tarbar tumbinsu, amma wani ba shi iyawa. Muhammadu ɗan Abdullahi !

Ɗuk fa ku lura, wannan dabara ce wadda aka shirya asirce, ba da sanin Musulmi ba. Amma Allahu Akbar ! Allah shi ne Fiyayen Mai Dabara. Ana gama ƙulla shawara, sai wahayi ya zo ga Annabi daga Maɗaukakin Sarki Allah, aka sanadda shi cewa ga ain da a ke ƙullawa wai za ayi masa. Maɗaukakin Sarki Allah, Fiyayyen Dukan Makiyayi, ya umurci Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, da ya yi hijira daga Makka, a wannan dare, ya koma Madina. Maɗaukakin Sarki Allah kuma ya umurce shi da ya sami wani, ya kwanta a bisa kan gadonsa, shi Annabi, don masu niyyar zuwa kashe shi a wannan dare, su amince kamar shi ne ke kwance. Sabo da haka Annabi ya tambaya, to, wa zai kwanta a gadona ? Wa ka ke zato ya karɓa ? Sayyidina Ali, Zakin Allah mai rinjaye, Aliyu ɗan Abu Talib ! Ya san haɗarin da ke akwai, amma shi ya fi so ya sayad da ransa don Annabi ya tsira.

Abin mamaki, ga shi kafiran Makka, na dabara su kashe Annabi, amma kuma su da kansu sun yi imani da sanin duk Makka ba mai gaskiya da riƙon amana kamar Muhammadul Amin. Hasali ma, ba su da wurin kai ajiyar kayayyakinsu masu daraja sai gare shi. Sabo da haka, a wannan dare, wanda zai yi hijira zuwa Madina a cikinsa, sai ya ba Sayyidina Ali dukan kayan nan da aka ba shi ajiya, ya ce ya ba masu su abinsu. Ka ga kuma wani abin mamaki. Annabi ya yi imani a ransa, cewa ko shi Sayyidina Ali da zai kwanta bisa gadonsa, maimakonsa, Allah ba zai bari kafiran Makka su kashe shi ba. Ka ga har yana masa saƙo, alhali kuwa zai kwanta ne a gadon wanda za a kashe.

**Magariba na yi, mutanen da aka zazzaɓo suka kewaya gidan Annabi. Abin ƙaddara, can da dare su duk sai Maɗaukakin Sarki Allah ya sako musu da barci. Annabi ya raɓa ya fita.**

Sayyidina Ali ya haye bisa gadonsa. Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya yi wannan hijira tare da babban abokinsa Sayyidina Abubakar, su ke nan.

Da za su fita, fuskar Annabi na cike da hawaye, ya dubi 'Dakin Ka'aba ya ce, "Ya Makka, duk duniya ba garin da na ke ƙauna kamar ki. Amma 'ya'yanki sun hana ni zama a ciki." Da wannan kalami Annabi ya yi ban kwana da mahaifarsa, cikin wannan dare, ya kama hanyar Madina. Allahu Akbar! Ya Allah ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici.

## Kiran Musulunci

Kai jama'a, a wannan wuri, ya kamata mu ƙara dakatawa mu yi zulumi, kuma mu yi tunani, shin wai me Annabi ya yi wa jama'an nan tasu haka har da za su riƙa gwada masa waɗannan irin azaba shi da waɗanda suka ba da gaskiya da shi ? Ba abin da ya yi musu. Laifinsa kawai wai ya kira su zuwa ga addinin musulunci.

Sai dai kuma ko da muka yi tunani, ya kamata mu ƙara tunani, yaya kafiran Makka kuwa za su jitu da Annabi a wannan lokacin, alhali duk abin da suka saba da shi, shi ne musulunci ke cewa su daina. Musulunci ya ce su bar bauta wa gumaka, su koma ga bauta wa Maɗaukakin Sarki Allah shi kaɗai. Ya ce su daina kisan juna, su daina shan giya, su daina kusantar mata ba kulawa kamar dabbobi, su daina bizne 'ya'ya mata da rai. A wajen sha'ani da juna, musulunci ya ce wa dillalai su daina rantsuwa bisa ƙarya, don a sayi kayansu, a daina tarbe abinci bisa hanya ana hana shi zuwa kasuwa. Ya ce masu awo su cika mudu, su daidaita sikeli. Musulunci ya hana sayen abinci a ɓoye sai ya yi tsada a fitar a sayar, ya hana cin naman alhanzir, da na kare, da na su jaki, da mussai. Musulunci ya kira jama'a a kan kowa da kowa ya yi noma. Ya ce wanda ya yi noma tsuntsaye ko mutane suka ci, ya yi sadaka ne. Musulunci ya haramta ba da bashi da ruwa. Ya hallatta cin bashi, amma ya haranta ci a ƙi biya. Ya yi umurni da a raba gado kowa ya samu, kada ko yaushe a bar babban ɗa shi kaɗai ya danne dukiya, sauran dangi su zauna a wahalce. Musulunci ya hana a yi wasici da cewa a ba wani dukan dukiyarsa in ya mutu. Ya hana a ɓoye shaida. Ya hana shaidar zur.

A wajen maganar tsabta, musulunci ya yi umurni da tsarkake wurin zama, a wanke hannu in za a ci abinci, a rufe abinci, a yi wanka, a yanke akaifa, a aske gashi har na hammata. Musulunci ya hana zama cikin ƙazanta. Ya hana maza kusantar mata in suna haila. Ya hana mutum kura ido ga kallon matar da ba tasa ba. Ya hana mace ƙura ido ga kallon mijin da ba nata ba.

A wajen dabbobi kuma, musulunci ya ce a ji tausayin dukan dabba mai rai. A ba su ruwa idan sun ji ƙishi, kada a ɗora musu kayan da ya fi ƙarfinsu. In an ga sun gaji a sauke su su huta. Hasali dai ko yaushe, kiran musulunci, zuwa ga waɗanda suka ba da gaskiya da shi ba ya nisa da cewa a taimaki matalauta, da musakai, da gajiyayyu, da matafiya, watau waɗanda suka baƙunce ku ba su da kowa. Har kiran ya kan ci gaba da cewa hatta waɗanda ba su musulunta ba a riƙa taimakonsu da sadaka tun ba idan sun sanya rai ga su sami taimakon sadakar ba.

Musulunci ya yi hani ga musanyar 'ya'ya. Wannan ya ba ka 'yarsa ka aura, kai kuma ka ba shi taka ya aura kamar musanyar bisashe ko haja. Ya ce kada ma a aurad da 'ya sai an sami iznin yardarta. A wajen sakin aure kuma, musulunci ya ce ko da ya ke Allah ya halatta a sake aure, duk da haka kuma Allah na fushi da wannan abu. Hasali ma musulunci ya ce sakin aure shi ne halas wanda Allah ya fi da ƙi. Watau ga shi halas ne, amma kuma Allah ba ya son shi.

Musulunci ya ce ko mutum ka gani zai aza wa dabbarsa kaya, ka tsaya ka taimake shi. Im mutum ka gani ya ɓata hanya, ka tsaya ka nuna masa, ka taimake shi. In a bisa hanya ka ga kaya, ko wani abin da zai riƙa cutar matafiya, ka dakata ka kau da shi. Im mutum ya yi maka magana, za ka mayar masa, to, ka mayar masa da mai daɗi. Im mutum ya yi maka sallama ka karɓa masa da wadata da daɗi. Kai, ko duban ɗan'uwanka za ka yi, musulunci ya ce ka dube shi da fuskar fara'a ta rahama. Hasali dai musulunci ya ce ko wace gaɓa ta hannun mutum akwai aikin lada da ya kamata ta yi a ko wace rana!

Musulunci ya hana yawo tsirara, ya hana alfasha, da zagi, da yi da wani, da tsegumi, da gami, da zunɗe, da bidi'a. Musulunci ya hana ƙarya, da karya alkawari, da cin amana! Ya yi umurni ga bidar sani ko wane iri, kuma wanda Allah ya ba ya-

yi umurni gare shi ya bayar. Addinin musulunci ya yi umurni da a gama kai, a so maƙwabci, a taimake shi, a yi biyayya ga iyaye, a taimake su, a yi biyayya ga sarakuna, in dai ba ga umurnin da ya ke saɓon Allah ba ne. Su kuma sarakuna da aka yi umurni a bi su. Addinin musulunci ya ce, 'kowa Allah ya ba ikon mulkin wadansu, sa'an nan ya ƙi bi da su ta hanyar nasiha, ba zai shaƙi ƙanshin Aljanna ba'. Musulunci ya hana girman kai. Ya hana alfahari domin asali, ko ilmi, ko sarauta. Ya hana riya, ko alheri domin riya. Ya hana in mutuncin ɗanuwa da keta haddinsu. Ya hana zalunci, da lalaci, da zama cikin jahilci. Ya hana rowa, ya hana kuma mubazzaranci.

Musulunci ya yi umurni da a yi imani da Allah kuma a aikata abubuwa nagari. Ya ce ba a ce wa mutum mumini cikakke sai in ya zama abin da ya ke so ga kansa, shi ya ke so ga ɗanuwansa.

Addini duka, in ka duba shi, sai ka ga nasiha dai ce Ubangiji Allah ya saukar ga al'umma.

Hasali dai waɗannan sun isa su sa kowa ya gane misalan irin abin da musulunci ya kawo ta hannun wannan manzo, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

To, duk azabar da kuka ga Annabi ya sha, ko kuka ga sahabbansa sun sha ba sabo da wani laifi ba ne dabam, a'a, laifinsu kawai yi wa jama'a gargaɗi ga bin wannan saƙo da Sarki Allah ya aiko ga 'yan Adam.

## Kogon Sauru

To, a baya mun tsaya ga cewa Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya yi hijira zuwa Madina a daren da aka kewaye gidansa wai za a kashe shi. To, da fitarsu bayan gari, sai Annabi ya ce nufi wani dutse da a ke kira Dutsen Sauru, da shi Annabi da babban abokinsa Sayyadina Abubakar. Da suka isa gindin dutsen, sai Annabi ya ce su hau su shiga cikin kogonsa. Suka shiga suka zauna.

Da safiya ta yi, Kuraishawa suka ƙaƙka ba Annabi, sai Sayyadina Ali, sai baƙin ciki da haushi suka kama su. Suka bazu gari da kewaye suna biɗarsu. Biɗar, da bin sau, ta kawo su har kogon nan na Dutsen Sauru. A nan Sarki Allah ya aikata abin da ya aikata. Ga su bakin kogo, su Annabi na kallonsu.

amma su Allah ya makantad da su ga ganin su Annabi. Hasali dai kwanan su Annabi hudu cikin wannan kogo.

Da Sayyadina Abubakar ya gansu, ga su tsaitsaye a bakin kogon, sai ya tsorata ya rada wa Annabi, ya ce, "Ga su fa sun zo !" Annabi ya karɓa masa ya ce, "Kada ka yi baƙin ciki, Allah na tare da mu !" Allahu Akbar ! Allah kuwa na tare da su. Domin da ikonsa ya makantad da maƙiyan nan na Annabi, suka ƙare leƙe-leƙensu, ba su gansu ba, suka koma.

A rana ta hudu da himmar Kuraishawa suka yi sanyi cikin farautar, sai su Annabi suka fito daga kogon, suka kama hanya, suka tasam ma Madina. Bayan sun kwana guda suna tafiya, ba dare ba rana, sai suka yi kiciɓis da wani Badawi, Balaraben ƙauye, wai shi Suraƙa, wanda ya sami labari Kuraishawa sun ce wanda duk ya zo musu da su Annabi, za a ba shi ladan raƙumi ɗari.

Da Suraƙa ya zaburi dokinsa ya taso wa Annabi Muhammadu, yana zuwa kusa, sai kawai ya ga dokin ya yi sassarfa, sai ya faɗi ƙasa. Suraƙa ya dakata ya yi ƙuri'a ya gani ko ya ci gaba da bi, ko ya tsaya, don faɗuwar dokinsa ta ba shi tsoro. Sai ƙuri'a ta nuna masa kada ya ci gaba. Ya yi kamar ya bi abin da ƙuri'a ta nuna, ya kuma yi tunanin raƙumin ɗari, ya ga ba shi iya barinsu. Sai ya watsar da zancen ƙuri'a, ya sake hawa doki, ya sake zabura ya bi. Yana zuwa kusa kuma, doki ya sake faɗuwa. A wannan karo fa zuciyar Suraƙa ta yi sanyi. Ya haƙiƙance a ransa lalle al'amarin nan na Annabi na Allah ne, ɗan Adam ba ya hana shi yaɗuwa. Tsoro ya cika shi, sai ya nufi Annabi da zuciyar salama, ya je ya roƙe shi gafara. Annabi ya ce masa ba kome ya tafi abinsa. Allah ya gafarta mana mu duka. Wannan labari duk yana cikin Buhari, Babin Hijira.

To, sa'ad da Annabi da Sayyadina Abubakar suna cikin wannan tafiya ta Hijira zuwa Madina, sai kuma suka gamu da wani wai shi Zubairu cikin waɗanda suka musulunta, yana tafiya zuwa ƙasar Sham fatauci. Shi wannan falke, Zubairu, shi ya taimaki Annabi da tufafi, da abinci ya kuma ce masa ba da. daɗewa ba, zai dawo ya zauna tare da shi a Madina.

Annabi ya ci gaba, hasali dai an ce kwansu takwas suna tafiya, sa'an nan suka isa. Wannan Hijira ta Annabi, daga Makka zuwa Madina, ita ta zama sabon shafi a cikin tarihin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Wannan hijira ta Annabi, babban al'amari ne a cikin tarihin musulunci. Sabo da muhimmancinta, ka ga shekarar musulunci, daga gare ta a ke fara ƙidaya su. Watau bana hijira na da shekara 1372. Amma ta Kirista su daga haihuwar Annabi Isa, bara da amincin Allah su tabbata a gare shi, suka fara lissafi. Bana shekararsu ta 1953 a ke ciki.

Amma kuma ku lura, ko da muka ce Annabi ya iso Madina, bai shiga gari ba kai tsaye. A'a, sai ya tsaya a bayan gari, a wani ƙauye da a ke kira Kuba. Ga shi nan kamar mil biyu bayan Birnin Madina. Annabi ya tsaya nan, ba don hutu ba, sai domin ya gina masallaci. Shi da kansa ya shiga cikin masu gini, aka gina masallaci na Kuba.

Allahu Akbar ! Muhammadu ɗan Abdullahi, mataimakin gaskiya da gaskiya. Dubi yadda ya fito Makka ana farautarsa za a kashe, amma ka ga da zuwansa Madina, bai shiga gari ba, sai ya tsaya bayan gari ya kama aikin Allah. Duk zaman da Annabi ya yi a Madina kusan ko wane mako ya zo wannan masallaci ya yi salla a ciki. Littattafai da dama na addinin musulunci, har da Buhari a babin Hijira, sun ruwaita cewa wannan masallaci na Kuba, shi ne Maɗaukakin Sarki Allah ya yi maganarsa a cikin Alƙur'ani.

Bayan kwana 14 sa'an nan Annabi ya hau taguwarsa, jama'a suka yaɓe shi, ya shigo Birnin Madina. Wannan ranà kuwa Jumma'a ce. Yana zuwa fikin Bani Salim, sai ya ga azahar ya yi, bai tsaya ya isa masauki ba, sai ya ja. Ya sauka a nan aka yi sallar Jumma'a. Sabo da tunanin wannan rana da wannan salla ta farko da Annabi ya fara yi a Madina, sai mutanen Madina suka gina Masallacin Jumma'a a wurin.

Daga nan, Annabi ya hau taguwarsa, jama'a na biye, ya shiga Birnin Madina. Yi tunani a ranka, ga Annabi ya shigo gari, amma bisa taguwa, amma kuma duk garin ba wani mutum ɗaya wanda zai ce wajensa ya zo, balle a nuñ gidansa. Sabo da haka, ina ka zata za a? Ina fa, tun da shi ke shi Annabi ba wanda zai ce gare shi ya zo. Sabo da haka ko wane ƙofar gida sai mutanen gidan su fito su tarye shi suna cewa, "Zo ka sauka gidammu, ya Annabin Allah. Zo ka sauka gidammu".

Duk gari ya ruɗe. Annabi ya ce a bar taguwarsa ta bi inda ta ga dama, tana bisa ga umurnin Allah ne. Kofar gidan duk da ita da kanta ta tsaya, to, nan ne Sarki Allah ya zaɓa masa ya

zama masaukinsa, nan kuwa zai sauka. Shi ke nan, sai aka saki akalar taguwa, aka ba ta hanya ta yi ta tafiyar ta, ta zo wannan gida ta wuce, ta zo wannan ta wuce, jama'a na kallon su ga ikon Allah. Tana zuwa ƙofar gidan wani, wai shi Abu Ayuba, sai aka ga ta tsaya a nan, ta durƙusa da kanta, don Annabi ya sauka.

Abu Ayuba ya fito da murna, ya shiga da babban baƙo cikin gida. Babban baƙo, wanda Maɗaukakin Sarki Allah ya saukad da shi a gidansa. Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya zauna a gidan Abu Ayuba wata bakwai. A cikin lokacin nan ne ya gina babban masallacinsa na Madina. Wanda ɗukan alhazai ke ciyara. Liƙe da masallacin kuma aka gina wa Annabi gida. A wannan wuri ne, Annabi ya yi zamansa na Madina.

Jama'ar Madina da shi Annabi kansa suka yi waɗannan gine-gine. Ana gini jama'ar Madina na waƙa, suna cewa : "Ya Ubangiji, ba wata lada, ba wata albarka, sai lada da albarka na gobe lahira. Ya Ubangiji yi jinƙai ga waɗanda suka zo, da waɗanda ka iske—Muhajirina da Ansarina".

Da farko wannan gini, ba wani gini ba ne mai ƙaye. Gida ne aka yi, kamar na kowa, da masallaci irin wanda kowa ya saba gani. Daga baya ne, aka yi ta gyara masallacin, har ga shi yanzu yana cikin gine-gine masu ƙayatarwa a duniya.

Amma fa, ko da shi ke wannan gida da aka gina wa Annabi a Madina, gida ne irin na kowa, ba wani fadi gare shi ba. Amma duk da haka, ka ga masallacin nan da Annabi ya gina a Madina, tauraro ne a tarihin musulunci. A cikin wannan gida Annabi da sahabbansa suka yi mafi tsawon zamansu na duniya a Madina. A gefen wannan masallaci ga wuri da aka keɓe wa matalauta, waɗanda ba su da abinci nasu na kansu, sai abin da suka samu daga gidan Annabi ko daga sadakar waɗansu masu zarafi.

Tun a wannan lokaci Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya tara sahabbai, aka yi shawara, aka ba Bila, baƙin mutum, bawa, mutumin Habasha, daraja ya zama ladan, a wannan masallaci mai daraja na Annabi Muhammadu. In an jeru wurin salla, Billa suna can sahun gaba, gaf da babban liman, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Yadda aka fara kiran salla, tun a lokacin har yanzu lafazinta ke nan, ba ta sauya ba.

To. ga Annabi ya baro Makka bisa ga umurnin Mahaliccinsa. Maɗaukakin Sarki Allah. Ina labarin sahabbansa? Ga su can am baro su kamar 'yan tsaki ba uwa a tsakanin kafiran Makka. Tashin Annabi ke da wuya, sai kafiran Makka suka ce wa sahabban Annabi da wa aka gama mu, ba da ku ba? Tilas, ko dai sahabban nan su kwance imaninsu su koma ga bautar gumaka, ko kuwa su ma su bar garin su koma Madina, ƙarƙashin inuwar Annabi. Wannan shawara ta biyu ita suka zaɓa. Suka yi ta kwarara Madina. Waɗansu daga cikinsu haka kawai su ke zuwa ba abinci, ba abin sutura, ba wurin kwana. Abin da kaeai ke gare su, shi ne ƙarfin imaninsu ga Maɗaukakin Sarki Allah.

Da Annabi ya ga haka, sai ya zo da dabara wadda har yanzu malaman tarihi na duniya su ke ta mamakinta. Ga ta : Da zuwansa sai ya tara mutanen Madina, ya shawarce su da cewa ga 'yanuwansu na zuwa daga Makka, yana so ya ƙulla musu zumunci da su. Abin da ya ke so, ko wane mai gida na Madina, ya yi 'yanuwantaka da wani ɗanuwansa na addini wanda ya taho daga Makka. Wannan zumunci da Annabi ya ƙulla, ya zama kamar zumunci da aka gama jini.

## Aminci Da Yahudawa

Madina a lokacin mazaunanta sun kasu ne kashi biyu, ga dai Arna, ga kuma Yahudawa. Babban aiki kuma da Annabi ya yi a Madina da farkon nan, shi ne yadda ya yi har ya ƙulla amincin zama lafiya da shi da Yahudawa. Ga sharuɗan da Annabi ya zana aka sa hannu kansu :

Na ɗaya : Da Musulmi da Yahudawa kowa ya sami 'yancin yin ibadarsa sosai ta hanyar addininsa.

Na biyu : Da Musulmi da Yahudawa su zauna cikin abota tare da juna.

Na uku : In yaƙi ya zo musu, to, da Musulmi da Yahudawa su taimaki juna.

Na huɗu : Da Musulmi da Yahudawa kada wani ya ƙulla aminci da waɗansu sai ya shawarci ɗanuwa.

Na biyar : Dukan manyan maganganu na shari'a a tsara hukuncinsu ga hannun Annabi. Shi kuwa in zai yi hukunci ga

wani, sai ya bi shari'ar da addininsa ta ajiye. Wannan duk yana cikin mashahurin littafin nan na Siyari wanda a ke kira Ibn Hasham, juzu'i na farko.

Ko da shi ke a wannan wuri, kuna ji kamar shimfiɗar musulunci ta tsira, to, ba ta tsira ba. Wahalolin da Annabi ya sa wurin iyad da wannan saƙo na Maɗaukakin Sarki Allah, kamar mu ce yanzu ne za su fito. Na baya kamar share hanya ne kawai. To, ɗa fa Kuraishawa suka duba, suka ga Annabi ya ƙaura ya koma Madina, kuma har ga shi jama'arsa sai zurarewa su ke yi, daga Makka suna binsa Madina. A can Madina kuma suka ga Annabi da sahabbansa duka suna zama karɓaɓɓu, ba kama a Makka ba. Suka ga gashi har sun sami gidajen zama da sababbin dangi. Sai abin ya firgita su. Suka riƙa taro a Darin Nadwati, watau gidan shawararsu, inda su ke taro. Shi kuwa wannan gida asalinsa, gidan Kusayyi ne, ɗan Kilabi wanda a littafi na farko kuka karanta ta yadda Kuraishawa ke riƙe da shi da daraja. Shi ne kuma a zanen tsatson da Annabi ya biyo, kuka ga ya fito ta daga tsatsonsa.

Kun ga alkawarin da aka ƙulla da Yahudawa, kamar abin zai tabbata, amma ina? Sai suka watsad da alkawari, suka shiga ƙulle-ƙulle da munafunce-munafunce, na yadda wai za su rushe Annabi da addinin musulunci. Kun ji ɗaya.

Kuma a nan Madina akwai wani da a ke kira Abdulla Ibn Ubayyi Ibn Salul. A dà, shi ke cara a Madina. Ba abin da ya ke so ma kamar a mai da shi sarki. Kwaram sai ga Aflalul Mursalina. Irin halin Annabi, ya sa duk mutanen Madina, da Musulmi da waɗanda ba Musulmi ba, suka rungume shi. Muhammadul Aminu, Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana! Ganin haka fa sai shi kuma Abdulla Ibn Ubayyi Ibn Salul hassada ta shige shi, ta shige shi, ta shige shi. Ya himmatu ga shirya dukan abin da ya ke zato wai zai kawo rushewar Aflalul Mursalina, shugabammu Muhammadu. Kun ji biyu.

To, duk cikinsu, babban haɗarin da ya fuskanci Annabi shi ne mai fitowa daga Makka. Kun ji a baya, mun nuna muku cewa mutanen Makka da suka ga yadda musulunci ke fure yana 'ya'ya a Madina, sai baƙin cikinsu ya ƙara ƙaruwa. Suka yi rantsuwa lalle lalle, ba wata dabara sai su ɗauko rundunar yaƙi, su zo har Madina su niƙe Annabi, shi da mabiyansa duka, su yi ɗai ɗai da addinin musulunci!

Da farko sai suka shiga hura wutar ƙiyayyar Annabi ga zuciyar ko wace kabila ta Larabawa mai ziyarar Ka'aba. Suka shiga ɗamara. Kafin su aikata abin da su ke niyya, sai Abu Jahali, manyan uban kafirawa, ya aika da wasiƙa zuwa ga Abdulla Ibn Ubayyi Ibn Salul wanda muka ce muku yana Madina. Ga abin da takardar ta ce:

Bayan gaisuwa, mun ga kun ba mutanemmu mafaka. To, mun rantse har da allolinmu, ko dai ku kashe shi, ko kuwa ku kore shi. In kuwa ba ku yi masa ko ɗaya ba, za mu zo da rundunarmu mu halaka ku duka, mu mai da matanku bayi!"

## Makka Ta Fara Kawo Hari

Daga nan, mutanen Makka suka fara kawo zamiya ta hari ƙasar Madina. Cikin haka ne, wata rana har aka kame raƙuman Annabi aka tafi da su. Daga nan mutanen Madina suka zama cikin gawurtaccen hadari. Ko wane dare sauraro su ke yi, ko za a yi musu farmaki. Annabi kuwa, shi da ma, shi ne kamar sarkin gadi, in dare ya yi ba ya ko runtsawa har gari ya waye!

Allahu Akbar. Dubi Musulmi an koro su daga gidajensu na iyaye da kakanni, ba don wani dalili ba, sai don kawai sun yi imani da cewa la'ilaha illallahu, Muhammadu Rasulullahi sallallahu alaihi wasallama. Sun gudo da imaninsu, sun zo Madina sun ɓuya, ga mutanen Makka kuma na farautarsu har fidan ɓuyarsu, wai za su halaka su.

Ana cikin wannan hali, wahayi ya zo ga Annabi, daga Maɗaukakakin Sarki Allah. Allah ya ba da iznin yin yaƙi ga waɗanda aka tarye su da yaƙi. Domin kuwa su ne aka zalunta. Kuma Ubangiji ya sanad da shi cewa yana tare da waɗanda aka zalunta. In kana so ka ji ainihin lafazin ayar Allah wadda ta kawo wannan izni sai ka buɗa Alƙur'aninka sura ta 22 aya ta 39.

Wata kuma aya ta sake sauka ga Annabi daga Maɗaukakin Sarki Allah, aka umurce su da su yi yaƙi fi sabilillahi da waɗanda suka kawo musu yaƙi. Amma kada su zama su ne azzalumai. Domin kuwa sun sani Allah ba ya son azzalumai. Wannan aya kuma in kana so ka ji lafazinta na sosai, sai ka buɗa Alƙur'aninka sura ta 2 aya ta 190.

Wannan izni fa ya bayyana a fili cewa lokaci ya zo ke nan da ti las tilas Annabi ya ɗauki makamai, da shi da jama'arsa domin shi

tsare kansu, su tsare iyayensu da 'ya'yansu, da matansu, da gidajensu, da Madina birninsu.

A wannan wuri tilas mu yi bayani, domin akwai masu sukan addinin musulunci suna cewa wai da ƙarfi da yaji, da tsinin mashi aka sa jama'a suka bi shi. Wannan zance ne duk na rashin sanin ainihin al'amarin. Yaya kuwa za a ce da ƙarfi aka tilasta mutane bin addinin musulunci, alhali ga abin da Allah ya ce nan a cikin Alƙur'ani ayoyi dabam dabam waɗanda suka nuna ba a tilasta wa mutum ba ya bi addinin musulunci ? Allah ya bayyana cewa ya aiko Annabi ne domin ya zama rahama ga 'yan Adam duka. Amma am-ba shi iznin ya yaƙi waɗanda suka yaƙe shi har zaman aminci da salamasu tabbata a tsakaninsu.

In da mai so ya bi ayoyin nan a cikin Alƙur'ani domin ya ji ainihin umurnin da Allah ya bayar, sai ya duba. Ga waɗansu nan a sura ta 18 aya ta 30, da sura ta 10 aya ta 109, da sura ta 11 aya ta 256, da sura ta 16 aya a 125. Kai, ga su nan da yawa cikin Alƙur'ani.

Wannan sh -ne iyakar abin da muka yi burin ba ku a wannan juzu'i na biyu na Tarihin Annabi. Kun lura wannan juzu'i ya faro ne daga haihuwar Annabi har zuwa hijirarsa zuwa Madina. Allah ya ba mu ikon ganin mun iyad da juzu'i na uku a haka.

Alhamdu lillahi. Ya Allah ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya riga, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici.

## ASSALAMU ALAIKUM

Alhamdu lillahi ! Godiya ta tabbata ga Maɗaukakin Sarki Allah, Ubangijin talikkai, mai kyau a duniya, mai jin ƙai gobe lahira.

Na rubuta muku littattafan tarihin nan, na farko da na biyu, bisa ga abin da na ɗan karanta ne daga littattafai da dama na Siyari, tarihin Annabi. Amma kun ga, a cikin rahamar Ubangiji, ban gama rubuta tarihin nan ba sai da Sarki Allah ya sawwaƙe mani zuwa Makka da Madina bara. Na gano da idona abubuwa da yawa da yanzu zan rubuta muku cikin wannan juzu'i na ukku.

Ba sha, wannan tarihi na zaman Annabi a duniya ya fi ƙarfin a ce masa tarihi. Aya ce Allah ya saukar don ta zama abin lura ga masu hankali'

Ya Allah ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici.

Alhaji Abubakar Imam.
'Dan Alƙalin Kagara M. Shaihu Usman.

ZUWA GA M. ABUBAKAR IMAM,

Assalamu alaikum. Bayan gaisuwa, na yi murna da sanasheka. cewa littafinka na tarihi ya sadu da ni, game da takardar ka. Na bi shi tare da 'ya'yana, malaman makarantar ilmin Arabiyya. Mun gyara ɗan abin da ke bukatar gyara a cikinsa, kamar yadda ka nema, ko da shi ke dai kusan ince ba wani abin gyarawa a cikinsa.

To, yanzu ga littafin nan, na mayar zuwa gare ka, game da jawabi na gabatarwa, wanda ka neme ni da in rubuta masa. Ga shi. Amma ina son ka sani, ko da yaushe a shirye ni ke da in yi maka taimako irin wannan.

Da na karanta wannan littafi naka, M. Abubakar Imam, na same shi littafi mafi kyaun tsari, da ma'ana, a cikin irin wannan FANNI na tarihi. Domin kuwa ka gina masa harsashi da ba da labarin waɗansu Annabawa da fari, game da bayyana irin wahala, da azaba, da ƙiyayya, da gaba, waɗanda suka sha daga wajen mutanensu. Kuma ka bayyana yadda Annabawan nan suka jure wa irin waɗannan musibu, ta hanyar nuna kyakkyawan haƙuri, da zuciya mai dauriya, da niyya ta alheri mai ƙarfi, ba da sun nuna ƙosawa ba ko gajiya. Allah Ubangiji kuma ya ƙara taimakonsu, da mu'ujizai masu ƙarfi, da ayoyi bayyananni, ya kuma tsare, kyakkyawar tsarewa, har suka iyad da dukan saƙon da aka aiko su da shi. Suka koma zuwa ga rahamar Ubangijinsu madawwamiya, bayan sun bar wa jama'a addini mai tsarki da haluluka masu kyau, abin koyi.

Daga nan sai Allah ya aiko da manzanci na ƙarshe, cikamakin dukan manzanci, gamammen saƙo zuwa ga dukan duniya. babban abin buri, wanda kowa da kowa ya ke sauraren zuwansa, ta hannun cikamakin Annabawa da Manzanni, Fiyayyen Talikai, Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

To, wannan shugaban ne, ka shimfiɗa tarihinsa, ka bayyana shi ga mutane da kyakkyawar ibara, da lafazi mai fasaha, mai daɗi, mai sauƙin ganewa. Ga shi ka ba da tarihinsa tun kafin annabci da kuma bayan zamansa Annabi, ka kuwa kyautata shi

matuƙar kyautatawa. Ka ba da cikakken bayani wanda ya ishi 'yam mata da samari manyan gobe, abin riƙawa. Ka bayyana musu irin hanyar shiryuwa ta Musɗafa da irin kyakkyawar halulukansa a lokacin zamansa a duniya, domin ka shiryad da su bisa ga daidaitacciyar hanya, ka tsamo su daga kogon ɓata, don su ma rayukansu su tsarkaku, halulukansu su yi kyau idan sun yi koyi da irin kyakkyawan halulukan nan nasa.

Hakika ka zaɓo daga cikin tarihin Musɗafa, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, 'ya'yan itace masu zaƙi wanda ya fi halawa. Ka ƙawata shi da lafazi mai kyau, da hanya mai kyaun tsari, sai ya ƙara zaƙi a kan zaƙinsa. Ka rubuta shi littafi mai bayyana ƙashin gaskiya, mai shiryarwa bisa ga daidaitaccen mafarki, mai tace halulukan samarin yau, ya gyara su, ya mai da su zuwa ga kyakkyawar hanya, irin waɗda Shugaban Manzanni ya kawo, idan sun karance shi, sun fahince shi, sun kiyaye shi, sun yi aiki da shi. Bukatarsu ga littafi irin wannan tana da yawa, balle ma ga waɗanda ayyukansu sun hana su damar koyon larabci. To, irin waɗannan mutane za su samu matuƙar biyan bukata, mai wadatarwa, da shiryarwa, daga littafin nan naka.

Ina roƙon Allah ya tsare ka, ya taimake ka, ya ba ka ikon wallafa waɗansu littattafai masu amfani ga mutanenka da ƙasarka, irin aikin managartan mazaje masu ilmi game da aikatarwa.

Kuma ina son in ƙara bayyana cewa na samı babban taimako a wajen bin littafin nan naka daga 'ya'yana, waɗannan malamai na Makarantar Ilmin Arabbiya ta Kano. Su ne M. Inuwa Kano, M. Nasiru Kano, M. Haliru Binji Sakkwato, M. Abubakar Gumi Sakkwato da M. Bashiru Zariya. Saboda haka sun cancanci cikakkiyar godiya daga gare mu ni da kai. Wassalam.

AWAD MUHAMMAD AHMAD.

*Shugaban Makarantar Ilmin Arabiyya, Kano.*

## Aminci Ya Tabbata A Gare Ku

ZUWA ga dukan maluma da shugabanni na Nijeriya ta Arewa. Gaisuwa mai yawa, da girmamawa, da bidar albarka. Bayan haka, ina mai ƙasƙantad da kai a gare ku, ina mai bidar jin ƙanku, da tausayinku, da taimakonku, ba hushin

ku ba, ga shi na kawo wannan taƙaitaccen littafi ga yara, da mata, da maza irina, waɗanda ba su sami yin ilmi ba.

Na kawo wannan littafi, Allah ya sani, ba don izgili ba, sai domin ya zama taimako ga irina. Na lura na ga 'ya'yayemmu da yawa yanzu, maza da mata, tun suna ƙanana, su ke faɗawa makarantun elementare, daga nan sai midil, sai sekandare, sa Ibadan, ko Ikko, ko Ingila, ko Amirka!

A cikin wannan irin yawo da su ke yi na ɗalifta, suna cin karo da mutane masu addini iri dabam dabam. Saboda zama cikin irin waɗannan, ko yarammu na so, ko ba sa so, sai ka ji abokai na ta kalarsu da zance a kan maganar addini. Abin tausayi ne, ka liske an tatuke ɗam Musulmi a haka a wurin da ba ya dai lmi da zai tare kansa, kuma kila ba malamin addinin musulunci a kusa da zai taimake shi. Mutum wanda a zamansa, Allah bai nufe shi da shiga cikin irin wannan mutsumutsu ba, kila ba zai gane muhimmancin bayanin nan namu ba.

Mun sani bayyana tarihin Annabi dukansa, da bayyana addinin musulunci dukansa abu ne mawuyaci ko ga malam, balle ga Abubakar Imam! Amma duk da haka, yaro, ɗam Musulmi, ya sami ko da ɗan ɗigo daga bayanin addinin musulunci, abu ne mai amfani, ko da ma ga wanda ba ɗam Musulmi ba. Domin kuwa ai sanin ƙofar ɗaki, yana ƙara sanya mutum kwaɗayin shiga.

'Dalibai da yawa na nan ƙasar suna cike da himma ta biɗar ilmi. Sai dai kila da dama a cikinsu, himmarsu ta fi yawa ga biɗar ilmin sha'a'irul Islami, watau ayyukan da musulunci ya ce a yi, ba ilmin addinin ba shi kansa.

To, wannan fannin na bayanin addinin musulunci shi kansa, ba na bayanin ayyukan da ya ce a yi ba, shi ne na kama a waɗannan ƙananan littattafai da na ke son shiryawa. Ina da burin shirya shi, kamar yadda na faɗa da farko, don yara su sami abin riƙawa shiga duniya biɗar ilmi. Ba domin su sami abin jayayya ba. Musulunci ya yi hani ga yawanta jayayya kan maganar addini sai ga abin da zai kawo amfani.

To, kowa ya sani, ba sai wani ya gaya wa wani ba, a littafi irin wannan na addini, mutum ba ya da wani wayo ko ilmi nasa na kansa. A'a, iyakar nasa dai ya fassara, yadda ya naƙalci fassarar, daga shaihunnan maluma. Saboda haka, na shirya rubuta waɗannan littattafai, bayan na yi kamar shekara goma ina

karanta littattafan da na ke iya ganewa cikin wannan fanni, tare da tsananin tambaya ga maluma, da bincike a gare su.

Wannan juzu'i na farko, na rubuta shi bisa doron ayoyin AlƘur'anin Allah ne mai girma, ƙamar yadda fassararsu ta bayyana a cikin tafsiran jalalaini, tare kuma da nassosin tarihi da Abi Muhammad Abdul Malik Ibn Hisham ya rubuta, a cikin juzu'i na farko, na mashahurin littafinsa na siyari, wanda a ke kira a taƙaice "Ibn Hisham." Ban da su kuma na sha kai idona ga mashahurin littafin nan na tarihin Annabi, wanda mashahurin malamin nan na Masar Muhammad Husaini Haikal ya rubuta. Tare da duba irin jerin da mashahurin littafin nan na Sufi Muɗi'ur Rahman Bengalee na ƙasar Hindu, har ma da ɗaukar samfur daga mashahurin littafin nan na Muhammadu Muhuyiddini Abdul Hamid, wanda a ke kira Durusud diyanati-wal-Ahlaƙ. Juzu'i na farko da dai sauransu. Ina fata Allah ya saka musu duka da alherinsa.

Kuma har wa yau ina godiya ga Shaihu Awad na Kahartum, wanda ke koyarwa a Makarantar Ilmin Arabiyya ta Kano, domin ƙoƙarin da ya yi na karanta wannan littafi, har ya rubuta masa muƙaddama. Kuma ina godiya ga Alhaji Baba Ahmed, Balaraben Shijiɗa, limamin Koleji ta Gwamnati ta Zariya, domin ƙoƙarin da ya yi ga saurarena har na karanta masa wannan littafi duka bayan da na gama shirya shi. Ya kuwa taimake ni da shawarwari waɗanda suka yi mini amfani. Su kuma Allah ya saka musu da alheri.

Mu kuma muna roƙo, Allah ya gafarce mu, bisa ga kuskuren da muka yi. Kuma muna fata Allah ya ba mu tsawon rai da basira ta iyad da wannan aiki da muka fara. Sai mu cika da addu'a—Ya Allah ka nuna mana gaskiya, gaskiya, ka ba mu ikon bin ta, ka kuma nuna mana ƙarya, ƙarya ka ba mu ikon ƙin ta!

ABUBAKAR IMAM

Ɗan Alƙalin Kagara M. Shaihu Usuman.

Da ganinsu, sai wani bardcn Makka ya tambaye su, "Ku ne su wa ?" Ubaidatu ya ce, "Ni ne Ubaidatu Binu Harsi ! Sayyidina Hamza ya ce, "Ni ne Hamza !" Sayyidina Aliyu ya ce, "Ni ne Aliyu binu Abi Talib !" Sai suka ce, "Madalla yanzu kam ga daidai da mu". Daga nan malam, na bar maka sani ! Kura ta murtuke. Can sai aka ji Garga, Aliyu ɗan Abi Talib, yana kabbarawa. A duba fage sai ga kafiran nan uku da suka tarye su suna mirgina cikin jini !

Wannan nasara ta fusata rundunar kafiran Makka. Suka zaburo gaba ɗaya, su duka dubu, wai za su hadiye rundunan nan ta Annabi, mai mutum ɗari uku. Allahu Akbar ! Fage ya yi baƙi ƙirin da ƙurar barade. Musulmi a cikin rundunar kafirai, suka koma kamar furfura a bisa kan yaro. Ana cikin yaƙi, ƙura ta murtuke, sai aka zo wa Annabi da kan Abu Jahali. Aka ce masa, "Ya Annabin Allah, ga kan Abu Jahali, aduwwul Lahi !" Annabi ya dubi kan kafirin, ya ce, "Allahu Akbar ! Iko ya tabbata ga Sarkin nan da ba shi da abokin tarayya !"

### Nasara Ta Samu

Ana cikin wutar wannan baƙin yaƙi, mazaje idanduna sun jujjuye, sai takobin wani sahabi na Annabi, wanda a ke kira Ukkashatu ya karye. Sai ya zaburo, ya zo ga Annabi, don ya karɓi wani. Annabi ya karyi reshen itace ya ce masa, "Je ka yi yaƙi da wannan !" Da Ukkashatu ya girgiza reshen nan na hannunsa, sai ya ga ya zama kansakali, shafau ! A cikin tarihi, har ana kiran wannan kansakali na Annabi da suna "Al'aunu".

Hasali dai rundunan nan ta Annabi Muhammadu, ta mutum ɗari uku, ita ce da ƙarfin ikon Allah, ba da ƙarfinsu ba, suka yi wa rundunar kafiran Makka kaca-kaca, ta barade dubu ! Da kafiran Makka suka gudu, sai Musulmi suka shiga fagen fama, domin su ga gawawwakin manyan Makka waɗanda suka kashe. Annabi ya dubi gawawwakin nan na mashahuran Makka ya ce, "Ya ku masu bauta wa gumaka, ya Utbatu inu Rabi'ata, ya Shaibatu ibnu Rabi'ata, ya Umayyanatu, ya Abu Jahali ibnu Hisham na ce ko yanzu kun ga abin da Ubangijina ya yi mini alkawari gaskiya ne ?"

"Kuna tare da Annabinku, sai kuka ƙaryata ni, amma sai ga waɗansu sun gaskata ni. Kuka kore ni, sai kuka ga Allah ya

sa waɗansu sun ba ni wurin raɓawa. Kun zo ku yaƙe ni, ga shi kuma Allah ya ba ni nasara bisa kanku !"

Ɗa sahabban Annabi suka ji yana wannan magana da gawawwaki, sai suka ce masa, "Ya Annabin Allah yaya za ka riƙa magana haka da matattu !" Annabi ya karɓa musu ya ce, "Ai ko ku da ke nan ba ku fi su jin abin da na ke faɗa ba. Amsa ce kawai ba su da ikon ba ni !"

Daga nan Annabi ya ta da Abdullahi binu Rawahata, ya ce ya yi maza Birnin Madina ya kai albishir: Ya zabura sai birni ! Ya iske Sayyidina Usumanu ama sallaci, domin shi aka bari gari Ya ba shi labari, ya zana masa sunayen shahararrun maƙiyan Annabi waɗanda aka kashe, watau su Abu Jahali. Sayyidina Usumanu ya ce, "Kai, gaskiya kuwa ce ka ke gaya mini ?" Abdullahi ya ce, "Na'am Wallahi, gaskiya ce na ke gaya maka !" Sayyidina Usumanu ya yi kabbara, kuma ya yi hamdala ga Ubangiji.

Daga baya Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya tinkaro Madina, tare da rundunar sahabbansa. Ga kafiran Makka da yawa waɗanda aka kama da hannu an taso ƙeyarsu. A ran nan Birnin Madina wane ranar ko wace Idi !

Da aka lissafta, sai aka ga ashe mutum 14 kaɗai ne Musulmi suka rasa. Kafiran Makka kuwa mutum saba'in duk manyan barade. Wannan yaƙi na Badar shi ya zama ɗigon bismilla ga jihadodin da Aflalul Mursalina ya yi a zamansa na duniya.

## 'Dari Uku Ta Rinjayi Dubu !

Muhimmancin wannan jihadi, a cikin tarihin musulunci ba ya misaltuwa. Wannan nasara ta Badar ta jijjiga dukan maƙiyin musulunci na lokacin. Ta haka wannan nasara ta zama alfijir, wanda ya nuna gabatowar asubahin musulunci. Wanda ke shakkar gaskiyar wannan saƙo na Annabi, duk a ran nan, a jinin jikinsa ya fara jin cewa "Gaskiya dai ta bayyana. Karya ko kalmar musulunci sai su yi tsaki, yanzu, da sun ji, ba girma ba arziki, ba da ma sun san dalili ba, sai su ji jikinsu na haɗuwa, ciki ya yi ƙulululu.

Bari ku ji abin da wani mashahurin Bature, Sir William Muir ya faɗa a kan labarin wannan yaƙi na Badar cikin tarihin

da ya rubuta. Ba a kan yana son yabon Annabi ba, amma a wannan wuri tilas ya ce, "Lalle a yaƙin nan na Badar, Muhammadu yana da abin da ya kamata ya yi taƙama da shi har ya ce Allah ne ya taimake shi. Domin kuwa, ba nasarar kawai ta ba da mamaki ba, kamar yadda mutum ɗari uku suka rinjayi mutum dubu ! Kuma ba da wannan, waɗanda aka kashe na mutanen Makka duk zaɓaɓɓun baradensu ne. A bisa ga haka kuma, mutanen Madina na komawa gida, ba a daɗe ba, sai ga labarin cewa Abu Lahabi, manya uban kafirai, shi kuma ya mutu !" Kun ji abin da Baturen nan ya faɗa.

Da zuwa, Annabi ya raba wa Musulmi bayan yaƙi, waɗanda aka kamo, ya ce musu, ko wane Musulmi ya ba nasa bawan yaƙi abinci dafaffe, shi kuwa mai riƙe da bawa ya ci dabino. Annabi Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya riga, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici ! Ka ji halin nasa ! Wannan babban darasi ne a cikin misali, wanda ya fara koya wa duniya. Musulmi suka yi ta mamaki, amma kuma suna cika umurninsa. Da Musulmi na tsammani sun sami ganimar bayin yaƙi, amma ka ga Annabi bai riƙe su a haka ba. Sai ya ce masu arziki a gida, su fanshi kawunansu. Marasa arziki kuwa su yi alkawari ba za su sake ɗaukar makami ba don su yaƙi Musulmi ba. In sun yi haka a sake su. Malamansu kuwa, Annabi ya ce fansar kansu ita ce su koya wa 'ya'yan Musulmi rubutu da karatu.

A bisa ga umurnin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, Musulmi suka riƙe fursunan nan na yaƙin Badar, da zuciya wadda ke cike da alheri da taimako. Sabo da irin daɗin da fursunan nan na yaƙi suka ji, har daga baya, wani daga cikinsu, su fursunan, ya ke cewa : "Allah ya saka wa mutanen Madina da alheri. Muna kamammu, fursunan yaƙi, amma sai su sauka daga bisa raƙumansu, su ba mu mu hau, su kuwa su yi mana zagi. A dafa abinci, in sun ga ba zai isa ba, sai su su ba mu, su kuwa su dangana ga cin ɗiyan dabino".

### Abin Da Ya Bi Bayan Yaƙin Badar

To, bayan yaƙin nan na Badar, ba sai mun ƙara faɗa ba. Abin da muka ce a baya, zai nuna wa kowa ya sani cewa Annabi ya fuskanci haɗari ke nan. Ga misali, da mutanen Makka suka

ga a fagen fama abu bai yi ba, ran nan sai wani wai shi Umair da Safwan suka gamu a wani wuri da a ke kira Hajar su biyu. Suka ƙulla shawara sabuwa ful wai ta yadda za su fille kan Annabi. Sai Umair ya shafo wa takonsinsa guba, ya sunno shi, yana cewa wai shi ya zo ne ya fanshi ɗansa da aka kama a yaƙin Badar. Yana shigowa, sahabban Annabi suka lura da niyyarsa. Sayyidina Umar ya zabura zai mirɗe wuyansa, Annabi ya ce ya dakata. Ya dubi baƙo, Umair, ya yi masa maraba. Sa'an nan ya tambaye shi, "Ya Umair, me ya kawo ka nan ?" Umair ya ce, "Na zo ne im fanshi ɗana". Sa'an nan Annabi ya ce, "To, wannan takobi da ka maƙe fa ?" Sai Umair ya yi rakwas, kunya ta cika shi. Annabi ya ci gaba da cewa, "Abin nan da kuka ƙulla ku biyu da kai da Safwan a Hajar duk muna sane !"

Umair ya yi saƙo. Yana zato tasa ta ƙare. Ya kasa kunne yana shiri ya ji Annabi ya ba da oda a kashe shi, sai bai ji haka ba. Sabo da ganin irin wannan zuciya ta Annabi, ta gafara ga masu laifi, sai Umair ya yi sanyi. Ya tabbata lalle al'amarin Annabi Muhammadu na Allah ne. Sabo da haka, nan take ya ce ya musulunta. Allahu Akbar ! Ya Allah ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskya, mai shirywarwa ga tafarki madaidaici.

Kun ji abin da ya gudana ga Musulmi, bayan wannan nasara ta Badar. To, ina labarin abin da ya gudana ga kafiran Makka ? Su waɗannan, tun da waɗanda suka saura suka ba da baya a guje, ba su zame ba sai gida ! Labari mai baƙance ciki ya cika Birnin Makka. Aka tafi aka ba Abi Lahabi wannan baƙin labari. Domin shi bai fita yaƙi ba, a gida ya zauna. Amma ya aika da Asi ɗan Hisham ya wakilce shi a fagen fama. Da ma ga al'adar Larabawa na wannan lokaci, idan za a yaƙi, tilas ne babban mutum, ko ya je, ko ya aika da wakilinsa.

To, da wannan labari ya shiga kunnen Abi Lahabi sai ciwo ! Shi ke nan sai mutuwa. Ashe da ma tasa mutuwar tana biye da shi ne, jira ta ke yi sai kunnensa sun jiye masa abin da ya faru tukun, sa'an nan ta gama masa aiki !

Sabo da tsananin baƙin ciki sai matan Makka suka aske kawunansu, don baƙin ciki an kashe musu mazaje. Amma sai aka lura, duk abin nan, matar sarkin Makka na lokacin, Abu Sufuyana ba ta zubad da ko ɗigon hawaye ba. Ita kuwa

ana kiranta Hindu 'yar Utbatu. Da 'yanuwanta mata suka tambaye ta abin da ya hana ta kuka, ga shi an kashe mata uba, da 'yanuwa, da ammi, da dangi, sai ta karɓa ta ce, "In yi kuka, domin matan Musulmi da ke Madina su sami labari, su sami abin yi mana ba'a !" To, in na yi kuka, sabo da me? In da ma na san kuka zai iya cire mini baƙin ciki ne, da na yi. Amma ba shi iyawa!" Shi ke nan Hindu ta zauna bata shafa mai, ba ta kitso, ba ta wanka. Ba ta sake kuma kwantawa tare da mijinta ba, sarkin Makka, wai sai ya ɗauko fansa !

Shi kuma sarkin ya yi rantsuwa, ya ce ba zai kusanci 'ya mace ba, sai ya yaƙi Muhammadu, ya ɗauko fansa. Ku lura fa, muna rubuta wannan suna Muhammadu a haka, ba domin rashin ladabi ba ne, sai domin ku fahinci yadda abokan gaba ke kiransa ke nan a lokacin, ba wata kalma ta ladabi. Kun san ba su yarda su ce masa annabi. Don kuwa a lokacin ba su yarda annabin ne ba.

**Yaƙin Sawiƙi**

To, kun ji halin da kafiran Makka ke ciki sabo da baƙin cikin nasaran nan da Musulmi suka samu bisa kansu a yaƙin Badar. Sabo da wannan baƙin ciki, da kafiran Makka suka koma gida, sai sarkinsu, Abu Sufuyana, ya sake ɗamara. Ya taso, ba da ma ya tsaya wani babban shiri ba. Ya kwaso barade mutum alfen, dubu biyu, ya nufo Madina. Watau kun ga rundunarsa wannan ta riɓa ta farko sau biyu ke nan ! Ga shi nan, ga shi nan, ya dawo ! Kwaram, Annabi ya sami labarinsu. Nan da nan shi kuma ya shiryo runduna, ya fito ya tarye su. A wannan karo rundunar Musulmi ba ta tsaya wani cane-na-cane ba, sai ta auka musu bagatatan. Ta haka, rundunar Abu Sufuyana ta gigice, ta yamutse. Cikin wannan gigicewar sai duk suka fashe, suka yi baya da gudu. Cikin gudun ne suka yi zubad da guzurinsu na abinci da da suka yiwo na soyayyen gari. Shi ne a ke kira sawƙi da larabci. Musulmi kuwa suka fafaro su da kora, suna tafe suna tsintar salkunan garin da su ke gudu suna zubarwa. Sabo da haka ne ma a ke kiran wannan yaƙin Yaƙin Sawiƙi, watau "Yaƙin Zubad Da Gari."

Kada ku manta fa, Sarkin Makka Abu Sufuyana har yanzu dai bai kusanci 'ya mace ba, domin ya ce ba zai kusance ta ba sai ya ɗauko fansa. Ga shi ya tafi an ƙara koro shi. Fansa ta

zama biyu ke nan. Saboda haka ido a rufe ya shiga tara ɗimbin runduna. Ya yi ta biɗar gudummawa daga waɗansu kabilu. Ya samu daga Ahli Jamamata, da Bani Kananata, da waɗansunsu. Ya dai himmatu ga ƙulla runduna wadda ko ina ta tunkara a girgiza !

## Auren Nana Fatsima

Mun sani yanzu muna tsaka ne ga labarin jihadodin Annabi, amma duk da haka a wannan wuri, ba mu iya wuce wannan shekara, sai mun ba da labarin wani babban abu da ya auku ga Musulunci a cikinta. Wannan babban al'amari, shi ne auren Nana Fatsima, ɗayar Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. A wannan shekara ne, Annabi ya aurad da ita, ga ɗan amminsa Sayyidina Ali. Aliyu ɗan Abi Talib ! Sayyidina Ali kuwa shi ne ya zama halifa na huɗu bayan Annabi. (Amma dai muna zuwa kan wannan labari na halifofin da rai, kada in yi muku tsalle). To, wannan aure, ya shiga cikin abubuwan da duniya ke mamakinsa, game da halayen Annabi. Domin kuwa yadda ka san ana auren 'yar kowa, ba wata rigima, haka aka yi na wannan 'ya ta Annabi Muhammadu, tsira da aminci su tabbata a gare shi. Ita wannan 'ya ta Annabi, Nana Fatsima, tare da uwargidansa ya haife ta, watau Hadiza. Duk dai kuna tune da labarinta, tun farkon labarimmu na bayyanar musulunci.

Kuma ga wani babban abin tunawa, game da wannan 'ya ta Annabi, Nana Fatsima. Ita ce fa kuma ta haifi Alhasan da Husaini da Muhassin da waɗansu mata.

## Shirin Yaƙin Uhudu

To, yanzu bari mu koma ga labarin jihadi. Ban da yaƙin Badar da na Sawiƙi, babban yaƙi wanda ya bi shi, wanda ya kamata mu ba da labarinsa, cikin wannan taƙaitaccen littafi, shi ne yaƙin Uhudu. Mun gaya muku abin da ya gudana ga ayarin fataken Makka, masu dawowa daga ƙasar Sham, da yadda waɗanda Annabi ya sa dako, suka yifaɗa da su, da aka hana su ruwa, har Annabi ya yi fushi da mutanensa da suka aikata haka.

To, sabo da haka ne fa, ran da manyan Makka suka taru a ɗakinsu na shawara, sai suka ƙulla cewa duk ribar da ayarinsu

za ta samu, a kashe ta ga sayen kayan yaki na zuwa ɗauko fansa ! A cikin manyan da suka taru ƙulla wannan shawara ta ɗauko fansa, ga su Zubairu Ibn Muɗi'imu, ga su Safwana Ibn Umayyata, ga su Ikramatu Ibn Abi Jahali, ga su Harisu Ibn Hisham, ga su Huwaiɗabu Ibn Abdul Uzza. Kai, gaggan Makka duk ba wanda ya ke baya !

Manyan gari suna cikin wannan shawara, magana ta zo a kan kada dai a yarda mata su tafi wannan fagen fama kamar yadda suka ce suna so.

Da jin haka, sai Hindu, uwargidan Sarkin Makka Abu Sufuyana, wadda muka ba ku labari, ta ɗaga muryarta da faɗa ga masu shawarar a hana mata zuwa. Ga abin da ta ce, "Sa'ad da za a yaƙin Badar, mata sun shirya su bi mazansu, har fagen fama,-amma suna isa Juhufa, sai aka mai da su gida, tilas, wai kada su fita. To, duk ku sani, a wannan karo, ba mai hana mu zuwa fagen fama !"

Sabo da haka, tilas, a wannan yaƙi na Uhudu, kafiran Makka, har da matansu suka taho Madina su yaƙi Annabi. Sarkin Makka Abu Sufuyana, yana tsakiya, kewaye da shi ga runduna, irin wadda Larabawa suka rabu da ganin irinta.

Ban da mata dai, barade, mutum talata ke cikin rundunar, watau dubu uku ! Ga dawaki ingarmu guda metan ana jaye da su. Ga jakai talata, watau dubu uku su ma, suna ɗauke da kayan faɗa, da kayan abinci ! Barade na tafe suna kirarir suna, kiran sunan gumaka. Ban da wannan runduna ta maza, ga Hindu kuma a can tare da rundunar mata. Maza kuma ba damar nuna tsoro. Duk suka dirkaki Madina, wai za kashe Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi !

Ga su nan, ga su nan, ga su nan, har wani dutse da a ke kira Dutsen Uhudu, mil kamar biyar rabonsa da Birnin Madina. A nan Sarkin Makka Abu Sufuyana ya kafa mashinsa. Aka shiga shaya daga. A gefen dama suka kafa Halidu Ibn Walidi, a gefen hagu ga Ikramatu Ibn Abi Jahali. Wannan al'mari kun ga ya faru ne tun gabanin musuluncinsu.

### Rundunar Annabi

Kun ji abin da ya gudana game da labarin kafiran Makka. To, yaya labarin Annabi. Da ma da Annabi Muhammadu,

tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya sami labarin cewa ga kafiran Makka nan gaba ɗaya sun zo halaka sum sai ya tara jama'arsa ga shawara, kamar yadda ya saba. Duk aka yarda da a fita a tsare kai.

A ran da aka shirya fita, Annabi ya shiga gida, bayan sallar la'asar. Sayyidina Abubakar, da Sayyidina Umaru, suka bi shi suka tafi suka taimake shi yin ɗamara. Ya jawo kansakalinsa ya rataya a kafaɗa. Ya fito waje. Allahu Akbar, shawara ta ƙullu ke nan. Afialul Mursalina ya yiwo ɗamara ! Kowa ya je ya kama shiri.

Kun tuna a farkon hijirar Annabi zuwa Madina, mum baku labari cewa Annabi Muhammadu, ya iske a Madina da wani gwarzo wai shi Abdullahi Ibn Ubayyi Ibn Salul. A lokacin shi ne kamar sarkin Yahudawa na Madina. To, zuwan Annabi Muhammadu fa, tsira da aminci su tabbata a gare shi, shi ya dushe shi. Sabo da haka, sai ya zama ga shi kamar tare da Annabi, amma zaman munafinci.

Tsaya ku ji aikin munafinci. Sa'ad da Annabi Muhammadu ya yunƙuro zuwa taryar kafirai a Dutsen Uhudu, ya taso da runduna ta barade ne mutum dubu ɗaya tak. Da ita ya fito, zai taryi rundunar sarkin Makka ta barade mutum dubu uku. Shi wannan sarki na Yahudawa da mu ke ba da labari, Abdullahi Ibn Ubayyi Ibn Salul da jama'arsa, suna cikin rundunar Annabi kamar abin aminci, kamar masu cikawa ne ga alkawarin can nasu da muka gaya muku tun zamanin hijira. Allahu Akbar ! Ashe fitowar ta Yahudawan nan babban munafinci ne. Ana cikin tafiya, an tasam ma Uhudu, inda za a gamu da sarkin Makka, sai Abdullahi Ibn Ubayyi Ibn Salul ya ware shi da jama'arsa, barde ɗari uku, suka mazaya. Wannan shi ya nuna wa abokan gaba kamar rundunar Annabi ta fashe ne. Ka ji tataccen munafinci, ƙullalliya ! Ta haka, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, da da ya fito da mutum dubu, sai ya koma da ɗari bakwai kaɗai. Watau mutum ɗari bakwai ke nan, suka fuskanci talata.

Wannan al'amari duk bai girgiza Annabi ba. Sai suka ci gaba, aka shaya dagar gwabzo. A tare da wannan daga ta sarkin Makka, ga uwargidansa Hindu, a tsakiyar rundunar mata da muka ce. Su matan su ke yi wa mazansu kiɗan dundufa, suna yi musu waƙa, da harshensu na Larabci. Ga abin da su ke cewa :

Waihan Bani Abdad Dari
Waihan hamatal adbari
Larban bikallin battari !

A shiyyar dagar Musulmi kuwa, ga Annabi Muhammadu nan, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana kewaya mazajensa, yana yi musu huɗuba, yana gaya musu cewa nasara a gare su ta ke, amma fa da sharaɗi, sai in sun yi haƙuri, kuma sun bi umurni. Daga nan, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya zare kansakalinsa, ya ɗaga shi sama, ya ce, "Wa zai karɓi wannan kansakali nawa, ya kuwa riƙe shi da haƙƙoƙinsa ?" Daga nan sai wani barde na Musulmi, wai shi Abu Dujanata, ya zabura, ya ce wa Annabi, "Mene ne haƙƙoƙinsa, ya Annabin Allah ?" Annabi ya ce, "Ka yaƙi abokin gabanka da shi, har ya hanu !" Daga nan Abu Dujanata ya sa hannu da ladabi, ya karɓi kansakalin Gaya-Wa-Jini-Na-Wuce ! Ya shiga fagen fama da shi. Aka fara karo, daga nan na bar muku sani ! Wanda duk ya zaburo, sai ka ga kai ƙasa ! Sai dai ka ce kansakalin ke aiki da kansa, ba a hannun wani va ke ba.

**Allahu Akbar !**

Sayyidina Ali kuma, Zakin Allah mai rinjaye, Aliyu ɗan Abi Talib, yana can shi ma yana ta nasa aiki ! Fagen fama ya ruɗe ! Annabi kuwa, su abin na manya ba dama ! In abu ya ruɗe sai Annabi ya yi kabbara, "Allahu Akbar !" Musulmi na ji duk sai su karɓa masa, "Allahu Akbar !" Kafirai na ihu, Musulmi kuwa suna ta kabbara. Abokan gaba na kiran sunayen gumakansu, Musulmi kuwa na kiran suna Maɗaukaki Sarki Allah.

Abu Dujanata, mai kansakalin Annabi a hannun dama, ya yi ta keta mazaje. Duk inda ya mai da gaba, sai maza su ba shi hanya ! Yana cikin aiki, sai ya hangi wani kafiri na Makka, ya dage sai ɓarna ya ke yi wa Musulmi. Abu Dujanata ya zabura, ya yi kabbara zuwa gare shi, ya aika da shi lahira ! Ya duba bayan jarumin nan da ya kayar, sai ya ga Hindu, uwargidan sarkin Makka, wadda mu ke ba ku labari. Ashe da ma mai tsaronta ne ke yi musu ɓarna. Abu Dujanata ya ɗaga takobi, kamar ya cire mata kai, sai ya tuna ashe fa kansakalin Annabi ne ke hannunsa. Sabo da girmamawar kansakalin Annabi, kada ya bugi mace da shi, sai ya dakata. Allahu Akbar ! Ka ji ƙarfin imani !

A wani gefe kuma ga Hamza can, ɗan Abdulmuɗɗalibi. Takobin Allah. Yankau, sai wasa ya ke yi da kawunan maza ! Da ma wane ne bai san Hamza ba ? A yaƙin Badar, shi ya kashe Utbata uban Hindu, matar Sarkin Makka Abu Sufuyana. Shi ya kashe 'yanuwanta ! Sabo da jaruntakarsa har a ke yi masa kirari, "Takobin Allah, Yankau !" To, da ma tun a Makka, Hindu ta sa kuɗi jibge, ga wanda duk ya kashe mata Hamza. Sabo da haka, maza zaɓaɓɓu, suka taru a kansa. Allahu Akbar ! A wannan karo kafiran Makka sai da suka kashe Hamza ! A gindin wannan dutse na Uhudu Saifullahiya yi shahada ! Yanzu haka ko wane Alhaji ya je Madina sai ya tafi Dutsen Uhudu ya ga kabarin Sayyidina Hamza.

Ana wannan karo, sai wata mace, Musulma, wai ita Ummu Ummarata ta yi ta bin fagen fama tana ba maza Musulmi, ruwan sha. Ita kuwa mutumiyar Madina ce cikin waɗanda aka tarar, Ansar.

A wannan karo, kafiran Makka, sun zo da burin wai sai sun kashe Annabi Muhammadu ne, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Makamai ba irin wanda ba su zo da shi ba, don wannan niyya. Abu ya kai har da jifa da duwatsu. Cikin jifan ne, har wani wai shi Utbata Ibn Abi Waƙƙasi, dutsensa ya sami Annabi. Yaƙi ya murtuke ! Da Annabi ya ji dutse ya same shi haka, sai ya buɗe baki ya ce, "Ya Allah, ka gafarce su, ba su sani ba ne !" Ana cikin yaƙi, fagen fama duk ya ruɗe, sai kawai 'aka ga wata ƙaddara ta auku, rundunar kafiran Makka suka yi kamar wani abu ya firgita su. Kawai sai suka yi baya da gudu ! Musulmi suka bi. A cikin wannan ruɗu, waɗansu Musulmi su kuma, 'yam baka, suka yi kuskure. Da suka ga ga shi 'yan-uwansu sun sami kora, sai suka sha'afa, suka bar inda Annabi ya ce su tsare, kar su tashi kome suka gani. Sai suka tashi, suka bi kora. saɓanin umurnin Annabi.

Da Halid, ɗaya daga cikin sarakunan yaƙin kafiran Makka ya duba, ya ga masu bakan nan da da ke yi musu ɓarna, ga shi sun tashi, sai ya juyo da rundunar da ke gudu tare da shi, ta dawaki metan, ya auka wa Musulmi, ga su da ma 'yan kaɗan ! Ganin ya yi haka, dukan rundunar Makka kuma, wadda da ta ba da baya, sai ta juyo da kora.

Rundunar Musulmi ta zama tsaka, ga ta daɗa kamar kuma

ba wanda zai kai labari ! Duk an warwatse. Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sai mutum goma kaɗai ke tare da shi. Da Annabi ya ga haka, sai ya yi kabbara, "Allahu Akbar. Ku nufo nan ya bayin Allah. Ni ne Annabin Allah ke kiranku !" Jin kiran Annabi a haka fa, duk ko wane barde na Musulmi, sai ya ji wani sabon ƙarfi ya shigo masa. Ba girma, ba arziki, ko wane Musulmi ya keta wa kansa hanya ya nufi wurin da ya ji muryar Annabi ta yi kiransa. Shugabammu Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ! A cikin wannan ƙoƙari, Musulmi da dama suka yi shahada.

## Labarin Karya

Ana cikin wannan hali, maza na gwabzo, ƙura ta murtuke, maza sun ruɗe. Sai labari ya bazu cikin fagen fama, aka ce, "Ai an kashe Annabi !" Da jin wannan labari na cewa an kashe Annabi, Musulmi su ba su karai ba. Sai suka yi kabbara, wani cikinsu ya ce, "Sai mu ci gaba da yaƙi sabo da niyyan nan da Annabi ya mutu dominta !"

A wannan fage, ban da raunin jifa da aka yi wa Annabi, an yi masa raunuka da dama, sa'ad da aka bar shi shi kaɗai ɗin nan a fagen fama. Mutum guda karo da talata ! Da Annabi ya samu mutanensa auka sake taruwa, kewaye da shi, sai ya keta hanya a tsakanin mazaje, ya kai su raɓin tsaunin nan na Uhudu, suka yi ta harbin abokan gaba da kibau. Watau ta baya tsaunin nan ya zame musu tare mahara. A wannan lokaci duk kafiran Makka suna ta murna sun ji wai an kashe Annabi. Amma da suka duba ba su ga gawarsa ba, sai suka shiga shakka, kila dai ba a kashe shi ba.

Sabo da su tabbatar da haka, sai sarkin Makka, Abu Sufuyanu, ya yi kira, Muhammadu ! Abubakar ! Umaru ! Annabi ya ce, "Kada ku tanka!" Da sarkin Makka ya ji ya ji shiru, sai ya ce, "Kai duk mun halaka su !" Jin haka sai Sayyidina Umaru ya kasa daurewa, ya buɗa baki ya ce, "Karya ka ke yi, maƙiyin Allah, duk muna da rai. Allah kuwa zai ƙasƙanta ka cikin hannummu !"

Daga nan Abu Sufuynu ya ce, "Ya Umar, gaya mini gaskiya, Muhammadu yana da rai !" Umar ya ce, "Na'am, Annabin Allah yana da rai, in sha Allahu yana kuwa ma jin duk abin da

ka ke faɗa !" Daga nan Abu Sufuyanu ya ambaci sunan gunkinsu ya ce, "Hubbal mai girma !"

Jin haka fa, Annabi Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. ya umurci jama'arsa da karɓawa gaba ɗaya, suka ce, "Allah shi ne mafificin mai girma !" "Aɓu Sufuyanu ya ce, "Mun dogara ga gunkimmu na Uzza. Ku kuwa ba ku da gunki Uzza, balle ku dogara da shi!" Sahabban Annabi suka karɓa masa suka ce, "Allah shi ne makiyayimmu, ku kuwa kun taɓe ga barin wannan makiyayi."

Muna fata, a wannan wuri, kun lura da wani mamaki. Idan aka yi wa Annabi mugunyar magana shi kansa, to, ba ya kulawa, amma idan aka yi mgunyar magana game da Maɗaukakin Sarki Allah, nan kam Annabi ba ya ƙyalewa.

## Kura Ta Natsa

Duk dai kun fahinta da irin dabarar ɗa Annabi ya yi. Ya jingina rundunarsa a bayan Dutsen Uhudu. Da haka, ba a iya biyo su ta baya din dutse ya kare. Ta gaba kuwa, 'yam baka, Musulmi, ba su bari ko tsuntsu ya ratso. Ta haka wannan yaƙi na Uhudu ya yi wata irin ƙarewa. Musulmi dai ba su da damar barin raɓin wannan dutse inda Annabi ya raɓa su, balle su auka wa kafiran Makka. Kafiran Makka kuma duk yawan nan nasu, tun da aka yi gaba da gaba, ba su da ƙarfin halin yiwo ɗauki. Tilas sai aka rabu a haka, tangam!

Da ƙura ta natsa, yaƙi ya buwayi ci gaba, sai mazaje suka rabu. Hindu, matar sarkin Makka, tana cike da murnar an kashe mata Hamza, wanda ya kashe mata uba a yaƙin Badar. Sabo da fushin da ke tare da ita game da shi, ko da shi ke burinta dai ya cika, na mutuwarsa, duk ba su ishe ta ba. Sai ta tashi, ana biye da ita, tana kewaya gawawwakin da aka karkashe. Da ita, da sauran rundunarta suna yanke hancin Musulmin da aka kashe, da kunnuwansu, suna jefarwa. Da suka kawo ga gawar Hamza, sai ta sa wuƙa ta keta cikinsa, ta yanko antarsa, ta sa baki ta yi ta tattaunawa, wai tana ƙitad da baƙin cikinta. Da su kafiran Makka suka ƙare bizne matattunsu, sai suka bar na Musulmi nan, suka koma Makka. Suka riƙa cewa wai su suka ci nasara.

Amma Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, shi da jama'arsa su kuma sai suka shiga ƙage, suka shiga bizne nasu matattun. Suna kewayawa, sai suka kawo

a gawar Hamza. Annabi ya yi tsaye, yana duban yadda Hindu ta keta cikinsa, ta yanke hancinsa da kunnensa. Sai ya yi salati, ya ce, "Wallahi, ran da Allah ya ba mu rinjaye gare su, mu ma za mu aikata gare su abin da wani Balarabe bai taɓa aikatawa ba."

Da Annabi ya faɗi haka, nan da nan sai aya ta sauko daga Maɗaukakin Sarkin Allah. Aka sanad da Annabi cewa idan aka yi muku azaba, to, in za ku rama, ku rama daidai da wadda aka yi muku. In kuwa har kuka iya yin haƙuri, to, akwai alheri ga waɗanda suka yi haƙuri. In kana son ganin ayar sosai, ga ta nan a sura ta Nahali aya ta 126 da ta 127.

**Musulmi Saba'in Suka Yi Shahada A Uhudu**

Hasali dai Musulmi suka koma Madina cikin baƙin cikin wannan babban rashi da suka yi na 'yan'uwa. Musulmi suka tafi suka bar mutum saba'in gawa, waɗanda aka kashe ke nan nasu. Kun ga watau ushirinsu ke nan suka yi shahada a wannan karo.

Waɗannan Musulmi da suka yi shahada a wannan karo na Uhudu, har yanzu su ne Alhazai ke ziyara in sun je Madina. In ka ji Alhaji ya ce za mu ga Hamza, ko mun fito ga Hamza, to, wannan Hamza shi a ke nufi. Shi kuwa na san ba ku dai manta ba, baffa ya ke ga Annabi. Domin mun ce shi Hamza ɗan Abdul muɗɗalibi ne. Kuma shi Abdulmuɗɗalibi shi ne kakan Annabi, shi ne kuma kakan Sayyidina Ali.

Ana cikin dawowa sai labari ya riga isa Birnin Madina, aka ce wai a cikin rundunar Musulmi ba a iya sanin wanda ya tsira, sai dai an ga dawowarsu! Saboda jin wannan, sai wata Musulma wadda ke da miji, da uba, da ɗanuwa, cikin fagen yaƙin nan, ta taryi wani matafiyi, ta ce masa, "Yaya labarin Annabi a fagen fama?" Sai mutumin ya ce, "Ai mijinki ya yi shahada, ya mutu!" Matar ta ce, "A'a, tambayarka na yi; yaya labarin Annabi?" Matafiyi ya ce, "Ai tsohonki shi ma ya mutu a fagen famar!" Ta ce, "Ya mamaki!" Ni tambayarka na ke in ji labarin Annabin Allah. Ba labarin mijina ba, ko tsohona."

Matafiyi ya ce, "Dan'uwanki shi ma sai mu ce Allah ya ji ƙansa!" Matar ta ce, "Ya salam, ni abin da na ke so in ji kawa don Allah, shin ina labarin Annabin Allah?" Matafiyi ya ce, "Annabin Allah kam shi lafiya lau ya ke!"

Da jin haka, sai matan nan ta ruga, ta nufi inda mazajen nan

na Madina su ke da yawa zuwa gida, ta taryi Annabi da gudu, tana cike da murna ta ce, "In dai kai ka dawo, ya Annabin Allah, duk baƙin ciki kuma ya zama ƙarami!"

Wannan shi ne ƙarshen abin da za mu iya gaya muku a taƙaice a kan labarin wannan yaƙi na Uhudu. Ya Allah ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici!

## Bayan Yaƙin Uhudu

Wannan yaƙi na Uhudu, ya zama kamar sabon mabuɗi ne na fitinoni ga Annabi Muhammadu, tsira ɗa amincin Allah su tabbata a gare shi. Duk Larabawan ƙauye, waɗanda da ke shayin Musulmi, don firgitar da suka yi ga abin da ya faru a yaƙin Badar, yanzu sai suka hutsance. Kowa ya ɗauko ɗan yaƙinsa, sai ya nufo Madina. Musulmi su kore su su koma. Mutanen Makka suka gama baki da dukan kabilun Larabawa a kan kada a bari Annabi ya kai!

Da abu ya yi tsananí, sai Musulmi suka zama da ɗamara su ke kwana, da ɗamara su ke tashi. Ga hari suna fama da karo da shi, ga kuma yaudara ana yi musu. Hijira na da shekara huɗu sai wani munafiki ya zo, wai shi Abu Bara, kamar ya musulunta, ya sanya Annabi ya ba shi mutum saba'in daga cikin sahabbansa, wai zai ja su su je ga waɗansu kabilu can a Nejad, suna son bayanin musulunci. Sun rabu da Madina da kwana huɗu, duka aka halaka su! Aka kama su ɗai ɗai aka yayyanke su gaba gaba. Ita wannan ƙasa ta Nejad can ne fadar sarkin Makka na yanzu ta ke. A cikin wannan shekara kuma, wata kabila da a ke kira Banu Adhal suka aiko ga Annabi, wai ga su sun musulunta, a je a koya musu addini. Annabi ya aika da malamai, shugabansu Asim Ibn Sabit. Da zuwa sai barde metan suka hau musu na Banu Lihyan, suka halaka Musulmin nan duka. Yahudawa kuma da da aka yi alkawarin zaman aminci da su suka tayar. Kai, fitinu dai iri iri, har ba su lissaftuwa a wannan ɗan ƙurarren littafi.

Ana nan haka, hijira na shekara biyar, sai Kuraishawa na Makka, da kabilun Larabawan daji, da Yahudawa, duk suka gama ƙarfi suka yi rundunа wadda ta gigita kowa a ƙasar Larabawa. suka yunƙura gaba ɗaya kamar tashin duniya, suka nufi Madina kisan Musulmi!

Da Annabi ya ji su tafe a haka, sai ya tara Musulmi don aiy shawara, a ga abin da za a aikata na tsaron kai. Mutane suka yi ta kawo shawarwarinsu. Amma wadda aka tsaya kanta, ita ce ta wani sahabi da a ke kira Salmanul Farisi. Shi kuwa ba ma Balarabe ba ne, mutumin Farisa ne, can wata ƙasa dabam. Shi ya ce, a gina tsanya kewaye da Madina. A yi ta mai faɗi, da zurfi yadda doki kome nagartarsa ba zai iya tsallakewa ba, ƙalle mutum.

Da jin wannan shawara duk aka ce, "Na'am, na'am !" Kun ga al'amari abin lura. Da ma an ce, "Hikima kaya ne na ko wane mumini da ya ɓace masa. Sabo da haka in da ya gane shi, ko ga wa, sai ya kama abin biɗarsa".

Al'amarin shawara ba ƙarami ba ne. Kun ga ma har Alƙur'anin Allah Mai girma ya yabi sahabban Annabi da zamowar al'amarinsu duk na shawara ne. Sabo da haka, ba a tsaya ɓata wani lokaci ba, sai AnnabiMuhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ba da umurnin aka fara. Nan da nan aka gina ƙatuwar tsanya a bayan gari, don ta zama taremahara. Shi ne da larabci a ke kira handaƙ. Sa'ad da a ke ginin wannan tsanya, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, da kansa ya ke saran ƙasa. Labarin wannan hari ba ƙarami ba ne ! Sabo da girmansa har Maɗaukakin Sarki Allah ya yi maganarsa a Alƙur'aninsa Mai Girma, sura ta 33 aya ta 10 da 11 da ta 22.

A lokacin da Musulmi ke tsahiyar gina wannan rami, don ya zama tare mahara, sai aka iske dutse. Gina ya faskara gare su. Sai su sahabbai suka nuna wa Annabi. Da ya gani sai ya karɓi diga, ya ɗaga ya sara. Da ya sara sai aka ji ya ce, "Allahu Akbar !" Ya sake ɗaga hannu ya sara, sai aka ji ya sake cewa, "Allahu Akbar !" Ya sake cira hannu na uku, ya sara, sai aka ji ya sake cewa, "Allahu Akbar !"

Da sahabbai suka ji haka, sai suka tambayi Annabin abin da ya sa ya yi ta kabiri sau uku haka. Sai Annabi ya ce, "Sa'ad da na ke sarawa ne Ubangiji ya nuna mini ga shi am ba ni mabuɗin mulkin ƙasar Sham da ta Farisa da ta Yaman !" Kun ji abin mamaki ! Ana kicikicin yin tare mahara, ga abokan gaba ƙofa, ka ji Annabi kuma yana ba jama'arsa labarin waɗansu nasarori da Allah ya nuna masa ya ba shi. Shi ke nan, dutse ya koma kamar rairai, aka gama aiki.

To, da zuwa, wannan ƙatuwar runduna ta kewaye gari, amma suka kasa haye tare maharan nan da aka yi. Sabo da haka suka dakace gari ba shiga ba fita har mako uku. Wannan al'amari ya firgita Musulmi da dama. Sai su zo ga Annabi da tambayar abin da za su aikata. Shi kuwa sai ya ce musu su roƙi Allah, shi ne fiyayyen mai taimako.

Shi kuma Annabi, duk lokacin nan sai addu'a ya ke yi ga Maɗaukakin Sarki Allah, ya koram musu waɗannan abokan gaba. Yana cewa, "Ya Allah, mai yaye wahalce-wahalcen ma-wahalci, mai karɓar roƙon wanda aka zalunta, kau da baƙin cikin nan nawa, da rashin kwanciyar ran nan nawa. Ya Allah ka ga abin da ya auku gare ni da sahabbaina !"

**Rundunar Allah Ta Zo !**

Allahu Akbar, da Ubangiji ya tashi karɓa masa wannan roƙo, sai ya aiko da rundunarsa, ta guguwa, irin wadda ba a taɓa ganin irinta ba ! Ta zo ta tuttge tantunan da abokan gaba suka kafa, ta watsa ko wane shiri da aka yi. Kai, abu ya kai kuma abokan gaban nan na Annabi, sai ta kai su ke yi ba su ta kaya ! Wannan runduna ta Ubangiji ta ruwa da guguwa ita ta kori wannan ƙatuwar runduna ta sarkin Makka.

Wannan runduna ta Ubangiji, ta yi wa Kuraishawa da ɗib-gegiyar gayyanan tasu ɓarna irin wadda ta firgita duniya duka game da mu'ujizar Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi !

Labarin wannan al'amari ya zo a cikin Alƙur'a nin Allah Mai girma, sura ta 33 aya ta 9. A cikinta Ubangiji Allah ya yi kira ga waɗanda suka ba da gaskiya, ya ce su tuna da baiwar da ya yi musu sa'ad da rundunan nan mai kama da ɗango, ta zaike musu. Aka aiko da iska mai ƙarfi da runduna, wadda 'yan Adam ba su gani ba, ta kare su.

Ana nan haka, Musulmi kwana da ɗamara tashi da ɗamara, har hijira ta yi shekara shida. Watau, Annabi ya yi shekara shida a Madina. A cikin wannan shekara, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya taso da mutum dubu da arbaminya suka nufo Makka, ba da niyyar yaƙi ba. A'a, da niyyar su zo su yi ibada.

Da Kuraishawa suka ji labarinsu tafe, sai suka ce su ba su yarda ba su shigo Makka ko da wace niyya. Sai suka shiga wasa

kansakula da masu. Firatan suka hana su Annabi shiga gari, balle su yi hajji.

Da Annabi ya ji haka, sai ya raɓa gari, har ya isa wani wuri da a ke kira Hudaibiyya, nan bayan garin Makka, a hanyar Madina. Ya aika a gaya wa sarkin Makka cewa shi ba da nufin yaƙi ya zo ba. Ya zo ne da nufin yin ibada. Yana roƙo kuma a ƙulla aminci da su, a bar su su shiga.

Manya da yawa na Kuraishawa da suka ji Annabi ya ce yana so a ƙulla amana, sai suka yi tsalle waje guda, suka ce faufau, ba su yarda ba a ƙulla amana da Musulmi. Amma a cikinsu, aka sami waɗanda suka rarrashi saura suka yarda. Ba saboda suna son Musulmi ba, sai dai saboda sanin halin Annabi. Muhammadul Amin. Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana!

Wannan aminci da aka ƙulla ta shahara a cikin tarihin musulunci. Har malaman tarihi na duniya suna kiranta "Amincin Hudaibiyya." Ga manya daga sharuɗan wannan aminci :

(1) A dakata da yaƙi da juna daga nan zuwa shekara goma.
(2) Kabilun Larabawa a bar su, masu son aminci da Musulmi su yi, masu son yi da Kuraishawa su yi.
(3) A bana ba a yarda ba Musulmi su yi ibada a Makka sai dai su koma. Sai dai in suna so, to, baɗi su dawo. Amma ko baɗin in sun dawo, ba a yarda ba su zauna cikin Makka fiye da kwana uku.
(4) Kuma kada im Musulmi sun zo Makka, za su koma Madina su tafi da wani ɗanuwansu Musulmi wanda ke zaune a Makka.
(5) Idan wani mutumin Makka, Musulmi, ko ba Musulmi ba, ya tafi Madina, to, Musulmi su mayad da shi. Amma idan wani Musulmi na Madina ya zo Makka, kafirai su ba za su mai da shi ba.

Ka ji sharuɗan zalunci a fili! Wannan duk yana cikin mashahuran littattafan nan na Siyari, waɗanda a ke kira Ibn Sa'ad da Ibn Hisham.

Da aka shirya sharuɗɗan, Annabi ya ce a rubuta don kowa ya sami kofe. Sayyidina Ali shi aka sa ya rubuta. Da ya gama aka ce ya karanta a ji. Sai aka ji ya ce, "Wannan shi ne alkawari na aminci wanda ya gudana tsakanin Muhammadu Manzon Allah, da jama'ar Makka . . . . . . . ."

Kafin ya ci gaba da karanta sharuɗɗan sai jama'ar Makka

suka yi tsalle, suka ce, "Kai, soke wannan shedara, ba mu yarda da ita ba. Mu ba mu yarda shi manzon Allah ba ne. Mu dai mun yarda shi dan Abdullahi ne.

Sayyidina Aliyu ya ce, "Ni kam hannuna ba shi kankare wannan shedara." Sai Annabi Muhammadu, manya dan Abdullahi, ya ce a ba shi takardar. Shi da hannunsa ya soke wannan shedara. Aka rubuta yadda mutanen Makka ke so."

Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya dauki wadannan sharuda, ko da shi ke ba su ko kama hanyar adalci ba. Aka koma gida. Annabi ya dauke su domin shi da ma Annabin aminci ne. Duk kuwa abin da ya ga zai kawo aminci, kome zafinsa, nan ya ke nufa. Aka zauna hakanan.

Shi ke nan, Allah a cikin rahamarsa kuma, ya yi ta turo jama'a su da kansu suna ta shiga cikin Musulunci. A cikin haka ne, har Halid Ibn Walid da Amru Ibnal As wadanda ke cikin manyan sarakunan yakin Kuraishawa suka zo suka karbi Musulunci. Wannan al'amari ya zama babban nakasa ga Kuraishawa domin kuwa a da su wadannan suna cikin manyan makiyan Annabi!

## Zuwa Ga Sarkin Rum

Da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya sami wannan sukuni, sai ya fara aikawa da wasiku ga manyan sarakuna na duniya, wadanda ke kusa da su, yana kiransu ga shiga musulunci. Ya aika ga Hirkal, sarkin Rum, ya aika wa sarkin Farisa, da sarkin Habasha, da sarkin Masar.

A lokacin da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya aika wa Hirkal sarkin Rum, sai aka iske sarkin yana Darussalam. Abin kaddara kuma, a lokacin sarkin Makka, Abu Sufuyana, babban makiyin Annabi shi ma yana garin ya je hutawa. Abin kaddara kuma, da sarkin Rum ya karanta wasikar, sai ya sa aka kira masa Sarkin Makka Abu Sufuyana wai ya tambaye shi labarin wannan mutum Muhammadu.

Hirkal ya fara tambaya—"Daga wane tsatso Muhammadun nan ya fito."

Abu Sufuyana ya ce, "Ai ya fito daga cikin zuriya ce tsarkakka ta Larabawa."

Hirƙal ya ce, "Duk cikin zuriyarsu wani ya taɓa cewa shi Annabin Allah ne ?"

Abu Sufuyana ya ce, "A'a, ba wanda ya taɓa cewa haka, sai shi kaɗai

Hirƙal ya ce, "To, mabiyansa, ƙaruwa su ke yi ko raguwa ?

Abu Sufuyana ya ce, "Ƙaruwa su ke yi ƙwarai, kullum kuwa !"

Hirƙal ya ce, "Mafi yawan mabiyansa daga masu arziki su ke fitowa, ko daga matalauta ?"

Abu Sufuyanu ya ce, "Daga matalauta !"

Hirƙal ya ce, "Imaninsu ga sabon addinin nan mai ƙarfi ne, ko kuwa suna dai biye ne ?"

Abu Sufuyanu ya ce, "Imaninsu mai ƙarfi ne ƙwarai da gaske !"

Hirƙal ya ce, "Muhammadu ya taɓa faɗar wata magana ta ƙarya kafin ya kawo ga cewa shi Annabin Allah ne ?" Abu Sufuyanu ya ce, "Karya kam ba ta taɓa fita ba daga bakinsa !"

Hirƙal ya ce, "An taɓa ƙulla aminci da shi ya karya ?"

Abu Sufuyanu ya ce, "Har abada !"

Hirƙal ya ce, "Me ya ke koya wa jama'a ?"

Abu Sufuyanu ya ce, "Wai a bauta wa Allah shi kaɗai, a zauna zama nagari, kuma a taimaki maƙwabta da dangi !"

Wannan hira duk akwai ta rubuce a cikin mashahurin littafin nan na hadisi da a ke kira Buhari. Da fa wannan sarki ya ji wannan labari na Annabi Muhammadu, tsira da aminci su tabbata a gare shi, daga bakin babban maƙiyin Annabi, ba ma daga bakin masoyinsa ba, sai ya ce, abubuwan nan da Abu Sufuyana ya bayyana masa su ne manyan alamomin da suka nuna lalle Muhammadu, annabin Allah ne! Amma saboda tsoron mabiyansa, bai sami ƙarfin halin karɓar musulunci ba.

Kun ji labarin wannan takarda ta Annabi zuwa ga sarkin Rum.

**Zuwa Ga Sarkin Farisa**

To, ina labarin wadda ya aika zuwa ga sarkin Farisa ? Ita kuma ga nata. A farkon wasiƙar, ga abin da aka rubuta : "Na fara da sunan Allah, mai jin ƙan bayi a nan duniya, maganin jin ƙai gobe lahira. Daga Muhammadu ɗan Abdullahi, Annabin Allah, zuwa ga sarkin Farisa . . . . . . Da haka takardar ta fara.

Ashe wai an yi kuskure, ba haka a ke fara takarda ba ga al'adar Farisa. Ashe su sunan sarkin Farisa a ke fara sawa kafin

a sanya sunan Allah. Kun ga a wannan har sunan Annabi shi ya fara ƙafin a sanya na sarkin. Saboda haka da sarki ya karɓi takardar, sai ya ce, "Me! Wanda zan kira bawana, shi ne wai zai yi mini wasiƙa har ya fara sa sunansa, kafin nawa?" Sai ya kekketa takardar. Ya aika ga hakiminsa na Yaman, domin a lokacin tana ƙarƙashin daularsa ce, ya umurci shi sarkin Yaman wai ya sa a kamo mutumin nan Muhammadu, ya yanka shi!

Da hakimin Yaman ya sami wannan saƙo na sarki, sai ya ce, "An gama!" Nan da nan ya aika da mutum biyu, wai su je Madina su kamo Muhammadu, a zo a yanka shi. Da suka zo, Annabi ya ji abin da ke tafe da su, sai ya ce musu, "To, ai shi sarkin na Farisa wanda ya aiko da umurnin a kama ni a kai masa ya mutu a bayanku, ɗanda ya kashe shi!" Masinjoji suka dawo suka ba hakimin Yaman labarin abin da suka ji, da kuma abin da suka gano. Kuma da suka iske cewa sarkin na Farisa an kashe shi, suka ga labarin Annabi ya yi gaskiya, sai jikin hakimin ya yi sanyi, dalilin musuluntarsa ke nan.

## Zuwa Ga Sarkin Masar

Sarkin Masar shi kuwa, sai ya ƙarbi saƙon Annabi da girmamawa, har ya ba da hadaya a kai masa. Amma bai karɓi musulunci ba. Ka ji nasa.

Sarkin Habasha Najjashi, shi kuwa da ma kamar aboki ne. Kun san gare shi ne Annabi ya kai ajiyar jama'arsa. To, da ma da zuwan takarda, sai ta iske ya rigaya ya yi imani da Annabi. Saboda haka, ɓa wata jayayya sai ya karɓi musulunci. Wannan duk yana cikin mashahurin littafin nan na Siyari wanda a ke kira Tibri, shafi na 1569.

Bayan wannan, babban al'amari wanda ya biyo shi ne na yaƙin Haibara. Wannan gari shi ne kamar fadar Yadudawa na ƙasar Arebiya a lokacin. To, kun tuna da sarkin Yahudawa na Madina wanda muka ba ku labari Annabi ya iske,. Abdullahi Ibn Ubayyi Ibn Salul. Kun tuna su ne aka yi alkawarin zaman amana da su. Amma ina? Ba su riƙi wannan amana ba.

Saboda haka da su aka gama kai. Amma gama kai bai yi ba. Musulmi suka ƙurmushe su. Ta haka Haibara ta zama ƙarƙashin daular musulunci. Akwai magana mai yawa game da wannan yaƙi na Haibara. Sai dai mu taƙaita shi a haka. Ba

wannan kadai ba, duk labarin yakokin Annabi za mu rage su, har da su Yakin Tabuka ba za mu-shiga ba don gudun tsawaitawa. Annabi ya bar rikon Haibara a hannun Yahudawa masu ita. Iyaka dai aka yi alkawari da su su rika biyan haraji, su kuwa a tsare su daga wadansu abokan gaba da za su taso musu. Musulmi su ba ruwansu da su, muddin su ba su fara taka Musulmi ba. Domin haka addinin musulunci ya bayyana.

To, a yanzu, shekara ta cika. Watau a bisa ga amanar da Kuraishawa suka kulla da Musulmi a Hudaibiyya, bana Musulmi suna iya zuwa Makka hajji. Sabo da haka Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya taso da sahabbai mutum alfen, dubu biyu. Suka zo Makka cikin salama, domin hajji. A bisa ga alkawarin da aka yi, Kuraishawa suka kai da jiki don kada a gamu wani abu ya auku.

## Zuwa Ga Sarkin Basra

Da Musulmi suka gama, aka dawo gida lafiya, sai aka iske fitina kuma tana jira ! Akwai wani hakimi na wata kasa wai ita Basra. Shi kuwa a lokacin karkashin mulkin sarkin Rum ya ke. Yana kuma cikin wadanda Annabi ya aika da wasika ta kira zuwa ga musulunci. Da ya karbi takardar, ya karanta, sai ya ce a fara yanka manzon nan na Annabi. Aka yanka shi. Ya kuma nuna cewa shi ba wani abu tsakaninsa da Musulmi, sai yaki !

Sabo da haka, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya tara runduna, a karkashin wani bawa nasa, da ya 'yanta wai shi Zaidu, ya umurce shi da ya tafi ya ci, Basra.

Kafin mu nutsa cikin wannan labari na yakin Basra, ya kamata mu dakata kadan, mu gaya muku wani babban labari, na game da wannan sarkin yaki, Zaidu, wanda Annabi ya ba shugabancin wannan runduna ta yakin Basra. Labarin tun a baya ya kamata mu ba da shi, amma muka rasa wurin da za dace sai nan.

Shi Zaidu-a da kun ji mun ce bawa ne. Bawa ne na Hadiza, uwargidan Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Ita ta saye shi, ta kuma yarda wa Annabi ya 'yanta shi. Yana bararren bawa, Annabi ya dauki Zainabu, diyar ammiyarsa, ya ba shi aure.

Dangi suka sa hannu a ka, sun ga abin baƙin ciki. Ɗanuwanta. Abdullahi Ibn Jahashi ya ce, "Yaya za a ɗauki Baƙuraisha, Bahashima, a ba bararren bawa ?" Ga al'adar Larabawa ƙuwa, kafin bayyanar musulunci, wannan babban aibi ne, wannan ma ba a ko mafarkin zai yiwu.

Annabi Muhammadu kuwa, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, bai yi haka ba sai don ya nuna wa 'yan Adam da misali zahiri, cewa ba wani jini da ya fi wani fifiko. Larabawa ba su da wani fifiko bisa ga Tukururu. Fifiko kurum yana ga wanda ya fi wani taƙawa. Domin kuwa haka Maɗaukakin Sarki Allah ya faɗa a cikin Alƙur'amni mai girma.

Watau, wanda ya fi ka aikata abin da Allah ya ce a aikata. ya fi ka nisantar abin da Allah ya ce a nisanta, shi ne kawai ya fi ka daraja ga Allah. Ashe kun ga ba Balarabe ba ne ya fi kowa daraja ga Allah, ba ɗan sarki ba, ba ɗan attajiri ba. Kun ga Maɗaukakin Sarki Allah shi ya nuna mafifici a wurinsa. Sabo da haka ne Annabi ya gama wannan aure wanda ya sanya dukan Larabawa sanyi wajen al'adarsu, ta ganin kamar su suka fi kowa daraja.

### Kada A Kashe Malaman Kirista

To, mu koma ga labarin Sarkin Yaƙi Zaidu, wanda ya ba shugabancin yaƙin Basra. A cikin umurni da Annabi ya ba Sarkin Yaƙi Zaidu, ran da za su fita, ya gaya masa kada su kuskura su kashe mata, ko ƙananan yara, ko makafi, ko malaman ahlil kitabi, watau Kisita, ko malaman Yahudawa. Ya ce kada ma su taɓa gidaje, ko su sare itatuwan jama'a. Kun ji irin umurnin yaƙin musulunci. Suna is, da 'yar rundunarsu ƙarama, sai suka iske ashe hakimin nan na Basra shirin yaƙi ya yi sosai da sosai. Ya fito da runduna wadda ta riɓa ta Musulmi sau nawa !

Aka shaya daga a wani wuri da a ke kira Muta. Sarkin Yaƙi Zaidu, da Ja'afar, da Abdullahi Ibn Rawaka, dukansu ginshiƙai ne na musulunci. A wannan fage suka yi mutuwar shahada. Abu ya ruɗe, sai barde guda, Halid Ibn Walid, ya ɗauki gaban yaƙi da kyar, ya mai da jama'a gida, Madina, ba a halaka su duka ba. Rana ta ɓaci ! Kun ji inda wannan labari ya kwana. Duk abin da muka faɗa ɗin nan yana cikin

mashahurin littafin nan, na tarihin Annabi, na larabci, wanda a ke kira, Ibn Hisham.

A nan ya kamata mu dakata ga labaran yaƙoƙin da aka kawo wa Annabi a Madina, da waɗanda shi ya kai, domin tsaron kai. Mun tsaya a nan domin a namu tarihi dukansa, muna tafe da shi ne a taƙaice.

## Yaƙin Makka

Ya Allah ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryawa ga tafarki madaidaici.

Ba shakka, kome taƙaitawa da za a yi, ga labarin yaƙoƙin Annabi, wajibi ne, kuma tilas ne, a cika da labari na ƙarshe, watau labarin yadda Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya gaje Makka. Wannan shi a ke kira da larabci Fatahu Makkata.

Kun sani dai, a da da mutanen Makka, da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sun yi alkawarin barin yaƙi da juna har shekara goma.

To, a wannan lokaci na zaman aminci, abin ya yi kamar zai ɗore. Amma ina? Sai wata kabila, wai ita Banu Bakar, ta auka wa wata, wadda a ke kira Banu Huza'a. To, ita Banu Bakar, tana aminci da mutanen Makka ne, Banu Huza'a kuwa da na Madina, watau su Annabi.

Daga nan, barade arba'in daga cikin na kabilar Banu Huza'a, masu aminci da Musulmi, suka hawo raƙuma da gudu, suka kawo ƙara ga Annabi cewa ga shi fa Banu Bakar sun far musu da zalunci. Suka roƙi Annabi ya taimake su, kamar yadda suka ƙulla alkawari. Daga nan, Aflalul Mursalina, ya ce Makka ta daina taimakon Banu Bakar a kan Banu Huza'a, ko kuwa su fito fili su ce igiyar aminci da aka ƙulla a Hudaibiya ta tsinke.

Da Kuraishawa suka ji waɗannan sharuɗa, sai suka zaɓi a ce amincin Hudaibiyya ɗin ya tsinke! Shi ke nan, sai Muhammadul Amin, Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana, ya ɗaura runduna. Ta mutum nawa ku ke zato? Ta barade mutum dubu goma! Suka tinkaro Makka. Abin kirarinsu, takbiri da kalmar shahada! Babu sarki sai Allah, Allah mai girma!

To, ga al'adar Larabawa kuwa, kamar yadda muka gaya muku a baya. In runduna ta sauka, ana so a san yawanta. sai a ɓidi sanin raƙuma nawa su ke sokewa kullum, ko kuwa da dare a ga yawan wutacen da su ke hurawa. To, saboda sanin haka, da dare, daren da aka kusanci Makka, sai Musulmi kowa ya hura tasa wuta. Ta haka, jama'ar Makka suka ga karkara duk ta cika da wuta, suka firgita! Wannan hikima ce da Annabi ya bayar. Kun san shi burinsa a yi zaman amana ba zubad da jini. Kun ji wannan.

**Abbas Ya Kama Sarkin Makka**

Dare na yi, sarkin Makka, watau sarkin Kafiran Makka Abu Sufuyanu ya fito, da shi da Budaili Ibn Warƙata, suna raɓe raɓe kusa da rundunar Musulmi, don su samo asirin abin da su ke ciki. Ashe cikin daren kuma sarkin yaƙi guda na Musulmi, Abbas, ɗan Abdul Muddalibi, watau baffan Annabi, ya hawo alfadarar Annabi, fara, yana raɓawa kewayen sansaninsu, don kada mutanen Makka su yi musu farmaki cikin dare.

Abin da ya sa ya hawo alfadarar Annabi, gudu ya yi kada yana cikin kewaya da duhun dare, wani Musulmi ya zaci abokin gaba ne ya hau masa. Amma wannan alfadara ta Annabi, kowa ke bisanta, sai ya ratsa inda ya ga dama.

Yana cikin raɓe raɓe, sai ya zo kusa da sarkin Makka shi kuma ya fito raɓe raɓe. Cikin duhun dare, sai ya ji sarkin Makka na ce wa abokin tafiyarsa, "Kai, tun da na ke ban taɓa ganin wani sansani da ya hura wutace aka cika karkara haka ba!"

Duhun dare ya hana ganin juna, ashe Abbas yana kusa yana jinsu. Da ya gane muryar sarkin Makka, sai ya kira shi da sunansa na kakanni ya ce, "Kai Aba Hanzalata." Sarkin Makka ya waiwaya. Abbas ya ce, "Kaitonka ya Abu Sufuyana! wannan runduna ta manzon Allah ce, shi ke tafe da kansa. Idan kuwa kuka bari ya shiga Makka da ƙarfi, kaitonku!"

Sarkin Makka ya gane muryar Abbas, sai ya ce, "Abbas ne! To, ina dabara? Na gama ka da Allah." Sai Abbas ya ɗauke shi a kuturin alfadarar Annabi, ya nufi laimar Annabi da shi. Abokin tafiyarsa kuwa ya koma gida. Abbas ya ratsa rundunan nan ta mutum dubu goma!

Suna wucewa, sai suka raɓo wurin da Sayyidina Umaru Ibn

Haɗɗab ya ke. Da ganin Abu Sufuyana, sai ya yi zaton ko Abbas na son gudu da shi ne. Sai ya zabura, ya tafi ga tantin Annabi, ya biɗi izni ya sare kan Abu Sufuyana cikin dare.

Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ce, "A'a." Abbas ya ce yana roƙo a ba shi ceton Abu Sufuyana a wannan dare. Annabi ya ce ya ba shi, ya je da shi tantinsu sai da safe su zo.

## Sarkin Makka Ya Musulunta

Da gari ya waye aka zo da shi. Annabi ya tambaye shi, "Ya Abu Sufuyana, har yanzu watau kai ba ka ba da gaskiya ba, cewa babu sarki sai Allah ko ?" Ya Abu Sufuyana, har yanzu ba ka ba da gaskiya ni manzon Allah ne ba ko ?"

Abu Sufuyana ya karɓa ya ce shi kam a gaskiya zuciyarsa na ƙaiƙayi ga yin imani da haka. Aka ci gaba da ba shi bayani, ana kawo masa ayoyin Allah da misalai. Hasali dai bar wurin ba sai da ya karɓi musulunci.

Daga nan Abbas ya ce, "Ya Annabin Allah, Abu Sufuyana mutum ne mai son girma. To, a ba shi wani abu na girma da zai faranta masa rai." Annabi ya karɓa, ya ce, "Na'am, to, a yi shela a Makka, im mun shiga, a ce a cikin jama'ar gari, wanda duk ya faɗa gidan Abu Sufuyana ya nuna amana. Wanda ya rufe gidansa ya nuna amana. Wanda ya shiga masallaci ya nuna amana. Waɗanda suka yi haka duk ba za a taɓa su ba."

Malaman tarihi sun ce ranar goma ga watan Ramalan rundunan nan ta Annabi ta shiga Makka. A sa'an nan hijira na da shekara 8. Watau Annabi na da shekara takwas ke nan da komowarsa Madina. Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya raba rundunarsa, suka shiga Makka ta jihohi dabam dabam. Ya ce su shiga da aminci ba da yaƙi ba.

Mutanen Makka kuwa, ganin abin ba dama, duka ba su daga kai ba. A cikin sarakan yaƙin Annabi, da aka ba jan waɗansu jama'a shiga Makka, akwai wani sarkin yaƙi, da a ke kira Sa'ad Ibn Ubada. Da ya ke jan jama'arsa, sai ya riƙa waƙa da larabci, yana bayyana cewa, "Yau rana ce ta karon maza da mazaje. A yau, Ka'aba ba ta tsira!" Da Annabi ya ji wannan waƙa, sai ransa bai so ba. Ya karɓa ya ce, "A'a,

yau rana ce ta ɗaukaka darajar Ka'aɓa!" Sai ya karɓe tutar shugabancin yaƙi daga hannunsa, ya ba ɗansa, shi wanda aka fitar ɗin, ya ce ɗan ya ja. Sunan ɗan Kaisir. Shi Allah ya sa yana da sanyin hali.

Duk cikin ƙungiyoyin nan da suka shiga Makka, ta ƙofa dabam dabam, ba wadda ta gamu da wata runduna ta Makka da ta tare mata gaba, sai ƙungiyar da Sarkin Yaƙi Halid ke ja, ita kaɗai. Da Annabi ya ji kansakula na wasa a wannan ƙofa, sai ransa bai so ba. Da ya tambayi yadda aka fara, sai aka ce masa abokan gaba su suka fara hau wa Musulmi. Sa'an nan hankalin Annabi ya kwanta, ya ce, "To, in haka ne kam ba laifi, don sun bi umurnin Allah ke nan!"

## Tsarkake 'Dakin Ka'aba

Daga nan Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya tasam ma 'Dakin Ka'aba. Gumakan nan 360 da da kafiran Makka ke bauta wa duk ya karairaya su. Har surorin da da su ke bauta wa, duk ya lalata su. Yana karya su yana cewa, "Gaskiya ta bayyana, ƙarya kuma sai ta tafi!"

Da ya gama tsarkake 'Dakin Allah, daga dauɗar tsafi, sai ya sa Bila babban bawa, ya yi kiran salla a 'Dakin Ka'aba. Aka shiga aka yi salla. Allahu Akbar! 'Dakin da da a ke taruwa a yi tsafi, ana bauta wa gumakka 360, yau ga shi ya koma ɗakin bauta wa Maɗaukakin Sarki Allah, shi kaɗai, wanda ba shi da abokin tarayya!

Allahu Akbar! Shekara takwas ke nan da suka wuce, kafiran Makka suka kori Annabi daga wannan birni na iyayensa da kakanni. Yau ga shi ya dawo ya shugabanci talikkai duka! Annabi ya hau mumbari, ya kama huɗuba, yana cewa :

"Gaskiya ta bayyana, ƙarya kuma sai ta tafi! ....... Ba abin bauta wa da gaskiya sai Allah. Allah ya cika alkawarinsa, ya taimaki bawansa. Allah, shi ne da ƙarfin zatinsa ya rinjayi abokan gaba. Ya ku Kuraishawa, yau Allah ya ɗauke muku girman kan nan naku na jahiliyya, da girman kan nan naku na alfahari da asali. Ku sani, duk jama'a 'yan Adam ne, Adam kuwa da turɓaya aka halicce shi. Ba shakka a cikinku wanda ya fi saura daraja, shi ne kawai wanda ya fi saura taƙawa kamar yadda Allah ya ce."

Daga nan. Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya sake duban jama'ar Kuraishawa da suka taru ya ce musu, "Ya ku jama'ar Kuraishu yaya ku ke zato yau, zan saka muku !" Kuraishawa suka karɓa gaba ɗaya, "Da jin ƙai, domin kuwa kai ɗanuwa ne mai jin ƙai, kuma ɗan ɗanuwa mai jin ƙai !"

Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya karɓa musu da zuciya mai gafartawa, da hawaye cike da fuskarsa, yana-cewa, "Ya Allah, ka karɓe su. Allah, kai ne fiyayyen mai jin ƙai !"

Da aka natsa, mutanen Makka suka yi ta kawo caffa, suna musulunta domin kansu. Sarauniya Hindu, uwargidan Sarkin Makka Abu Sufuyana, ta zo gaba ga Annabi, ta biɗi gafara a gare shi. Kun sani, ita ce fa, don ƙin musulunci har ta cinye hartar Hamza a fagen yaƙin Uhudu. Kun dai tuna da ita. Annabi Muhammadu, tisra da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya gafarta mata. Allahu Akbar ! Muhammadu Aminu, Muhammadu Annabin rahama !

Daga nan Annabi ya sa aka yi yekuwa, cewa, "Ya jama'ar Makka, a cikinku wanda ya yi imani da Sarki Allah, da ranar kiyama, to, kar ya bar gunki gidansa, ya karairaya shi".

## Sayyidina Abubakar Da Tsohonsa

Ana cikin ture-turen zuwa ga Annabi, sai ga Sayyidina Abubakar ya taitayo mahaifinsa, ya zo da shi gaban Annabi. Da Annabi ya gan shi sai ya ce, "Ya Abubakar, me ya sa ba ka bar shi can wajen da ya ke zaune ba, in je gare shi ?" Sayyidina Abubakar ya ce, "Ya Annabin Allah, shi ya kamata ya zo gare ka, ba kai ka je gare shi ba".

Annabi ya zaunad da shi kusa da shi, ya rungume shi ya ce, "Ko ka yarda za ka musulunta ?" Tsoho ya ce, "Ai ni na yi imani babu sarki sai Allah, kai kuwa manzonsa ne !" Allahu Akbar ! Hasali dai malaman tarihi sun ce kwanan Annabi 15 yana ta musuluntad da jama'a a Makka.

Da aka natsa, sai mutanen Madina suka yi zaton Annabi ya dawo gida ke nan Makka, ya rabu da su. Da Annabi yajihaka, sai ya ce musu, "Ni bawan Allah ne, Annabin Allah kuma. Shi ya umurce ni da in yi hijira bisa ga umurninsa zuwa gare ku.

Inda kuka zauna duka, ni ma nan zan zauna. a nan kuma zam mutu !"

Abin sha'awa, ko a wannan lokaci fa, ba dukan mutanen Makka suka karɓi musulunci ba. A'a, akwai da yawa waɗanda suka yi caffa ga Annabi, amma ba su yarda da su musulunta ba. Watau su dai sun yi masa alkawarin ba za su cuci Musulmi ba ke nan, kuma ba za a gama kai da su a cuci Musulmi ba. Sabo da haka suka yi masa caffa. Amma a lokacin su ba su yarda ba Allah ɗaya ba ne. Ba su kuma yarda ba shi Annabin Allah ne. Aka kuwa zauna da su a haka. Daga baya da suka gane wautarsu, suka gaskata Annabi.

Abin mamaki ma shi ne wannan. Da Musulmin Makka za su yaƙin Hunaimi, sai ga har waɗanda ba su musulunta ba, daga mutanen Makka, sun shiga cikin rundunar Musulmi, sun tafi taimako. In lokacin faɗa da abokan gaba ya zo su yi kafaɗa da Musulmi suna taimakonsu. Idan lokacin salla, ya yi, su zauna gefe ɗaya suna kallon Musulmi har su gama abinsu. Wannan al'amari ya isa ya kori zancen masu ƙaryar cewa wai da tilas Annabi ya baza addinin musulunci.

Masu cewa wai a zamanin Annabi, mutane da yawa sun shiga musulunci domin tsoron kada a kashe su ne, ba domin sun gaskata Annabi Muhammadu ba, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Wannan zance ne na jahilai. Wata sa'a kuwa na masu hassadar musulunci.

To, Annabi ya dakata a Makka, yana shirya zaman jama'a bisa hanyar musulunci. Sai da ya ga abu ya gyaru sosai, aminci ya samu, sa'an nan Annabi ya koma Madina, da jama'arsa waɗanda suka zo. Ya bar wa Abu Sufuyana, sarkin Makka wanda kuka sani ya ci gaba da mulkin garinsa. Kun ga abu ya fito fili, Annabi ba yaƙin biɗar mulki ya ke yi ba, kamar yadda masu yi wa musulunci hassada su ke cewa.

## An Hai Ibrahim

Ba shakka, ba ni zato akwai wani malamin tarihi da zai iya wuce wannan hijira, ta takwas ga tarihin Annabi, ba da ya faɗi labarin haihuwar Ibrahim ba, da labarin rasuwarsa a wannan shekara. Shekara ta takwas bayan hijira, Mariya, matar Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ta haifi Ibrahim. Da ya wuce shekara guda kaɗan, sai ya rasu.

Abin ƙaddara, ran da ya rasu sai aka yi husufi, watau wata ya kama rana. Ba rana ya kama wata ba. Ganin haka sai waɗansu Musulmi, suka fara cewa lalle saboda baƙin cikin rasuwar Ibrahim ne rana ta dushe haka.

Da wannan zance ya kai ga kunnen Annabi, sai nan da nan ya tara sahabbansa, ya bayyana musu cewa, "Husufin rana da husufin wata ayoyi ne na Ubangiji. Rana da wata ba mai yin husufi don haihuwar wani, ko don mutuwarsa!"

To, mu koma ga labarimmu. Hasali dai, tun daga nasarar Makka, duk ƙasar Arabiya, sai kabilu suka yi ta kawo caffa, su da kansu suna musulunta. Watau nasarar Makka ta zama babban mabuɗi ke nan na bazuwar musulunci.

Allahu Akbar! Muhammadu Aminu, Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana! Ya Allah ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici! A haka, kwana tashi, kwana tashi, kwana tashi, duk ƙasar Larabawa ta zama cikin aminci. A ƙarshen shekara ta goma, bayan hijira, sai Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya taso daga Madina, a cikin jama'a masu ɗimbin yawan gasken gaske, ya nufo Makka domin hajji. A wannan shekara, malaman tarihi sun ce, mutum dubu dubu har gida ɗari da ashirin da huɗu suka taru a Makka, domin hajji daga ko wace jiha ta ƙasar Larabawa. Cikinsu duk ba ɗaya wanda ke tsafi! Gaskiya ta bayyana, ƙarya kuma ta tafi!

Garin da Annabi ya bari da guɗu, yau shekara goma kaɗai, ana binsa za a kashe, ba don wani laifi ba, sai kawai don ya ce Allah shi kaɗai ya ke, ba ya da abokin tarayya, yau ga shi Allah ya maido shi, a kan duk ƙasar ba Makka kawai ba, shi a ke saurare. Muhammadul Aminu, Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana!

A wannan karo ne, a wannan rana, ranar tara ga watan Zulhajji, ranar Hawan Arafa, aya ta sauko ga Annabi, daga Maɗaukakin Sarki Allah. Dubi Alƙur'aninka sura ta 15 aya ta 3. Ta bayyana cewa a ran nan Ubangiji ya cika wa Musulmi addininsu dominsu, ya cika ni'imominsa a gare su, ya zaɓa musu musulunci ya zama addininsu.

Saukar wannan aya, a wannan rana, ta bayyana a fili ga Annabi, cewa ƙaurarsa ta kusa. Domin kuwa, an aiko shi ne

da saƙo, na addinin musulunci don ya bayyana wa duniya. To, ga wanda ya aiko shi ya ce yau saƙo ya cika. Ba sai manzo ya koma ga wanda ya aiko shi ba?

**Huɗubar Annabi Ta Ban Kwana**

Da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya karɓi wannan saƙo daga Ubangijinsa, na cewa abin da Allah ya yi nufi ya aiko shi ya kawo ga duniya a yau ya cika, ba sauran wani abu kuma da za a aiko masa ya bayyana, sai ya gane cewa ashe kuwa lokacin barinsa da duniya ya zo ke nan.

Jin haka, sai kuma shi, shugabammu Muhammadu, ya shirya ya yi ban kwana da jama'a, domin lokacin komawarsa ga Sarkin da ya aiko shi ya zo. Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya fara da godiya ga Ubangiji, da yabo kuma a gare shi. Sa'an nan ya ci gaba da cewa, "Ya ku mutane, ku saurari zancena. Domin kuwa ban sani ba kila har abada ba zan sake gamuwa da ku ba daga wannan shekara, a wannan wuri.

"Ya ku mutane, haramun ne gare ku jinin junanku, da dukiyoyinsu, har ran da kuka sadu da Ubangijinku." . . . . . . Ya ku mutane, ku sani za ku gamu da Ubangijinku, zai kuwa tambaye ku ga ayyukanku, ni kam na ida saƙo.

"A cikinku wanda amanar wani ke ga hannunsa, to, ya mayar wa wanda ya ba shi riƙon amanan nan. Kada ku yi zalunci, ku kuma kada ku bari a zalunce ku.

"Bayan haka, ya ku jama'a, ku sani cewa Shaiɗan ya taɓe, ba za a sake bauta masa ba a wannan wuri naku har abada!

"Bayan haka, ya ku jama'a, akwai hakki a gare ku zuwa ga matanku, su kuma mata akwai hakki a gare su zuwa gare ku.

"Ya ku mutane, ku ji zancena, ku lura da shi. Ku sani ko wane Musulmi ɗanuwa ne na Musulmi. Kuma su Musulmi dukansu 'yan'uwan juna ne. Bai halatta ba wani mutum ya karɓi wani abu daga wani ba da ya ba shi da yardarsa ba. Kada ku zalunci kawunanku.

"Ya ku mutane, ku sa hankali ga zancena. Ku sani ni kam na i da saƙo. Na bar muku abin da ba za ku ɓata ba in kuka riƙe su. Wannan al'amari ne bayyane—su ne Littafin Allah, watau Alƙur'ani, da Sunnar Manzo." (Sunna ita ce abin da shi Annabi ya faɗa da bakinsa da abin da ya aikata da kansa cikin zamansa na duniya).

To, da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kai ƙarshen huɗuban nan tasa ta ban kwana da duniya, sai ya ce, "Ya Ubangiji yalla na i da saƙo ?"

Sai jama'a duka mutanen nan dubu ɗari, da dubu ashirin, da dubu huɗu, da ya ke yi wa zance suka karɓa, "Na'am." Sai Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ce, "Ya Allah, ka shaide ni!"

**Annabi Ya Koma Madina**

Da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya kawo ƙarshen wannan huɗuba tasa, sai ya sauka daga kan taguwarsa, ya yi wa jama'a salla. Da ya ƙare, aka sake hawa zuwa wani wuri Saharatu. A can ne Annabi ya sanad da jama'a ayan nan, ta Alƙur'ani, da muka ce ta saukai masa a farkon wannan magana. Da Sayyidina Abubakar ya ji saukar wannan aya, daga Maɗaukakin Sarki Allah, ya ji ga shi Sarki Allah ya ce Annabi ya i da saƙon da a ke so ya kawo ga 'yan Adam, sai a ransa ya ce, "To, lalle lokacin barin Annabi duniya ya matso. Lokaci ya matso da zai bar duniya, ya koma ga Sarkinsa." Sai ya fashe da kuka. Aka tambaye shi dalilin kuka, ya ce, "Ina kuka ne don na ga tun daga yau addini ya fara raguwa ke nan." Aka ce ta yaya ?" Ya ce, "Idan an ce al'amari ya cika, to, sai ka saurari raguwarsa."

Shi ke nan, aka ƙare hajji. Annabi ya dawo Madina. Larabawa kowa ya koma gida a ruɗe, saboda tunanin huɗuban nan ta Annabi, ta ban kwana. Ana nan, ba a cika wata uku ba, sai Annabi ya kama rashin lafiya. Da shi ke ya san wannan rashin lafiya na ƙaura ne, duk wasicin da zai yi wa jama'a sai ya yi ta yi. Ya yi kamar kwana 12 yana rashin lafiyar. Tun yana iya fita, ya yi wa jama'a salla, har ta kai sai ya ƙaddama Sayyidina Abubakar, shi ya shugabanci jama'a a yi salla.

Ran nan yana kwance, sai 'yarsa Fatsima ta zo kusa da shi.— Sai ya yi mata magana a hankali, ya ce mata, "Ba zan tashi ba ga wannan ciwo!" Sai ta ɓarke da kuka. Daga nan sai ya ce mata, "Bari kuka, duk cikin 'ya'yan da ke da rai, ke za ki fara iske ni." Sai ta fashe da dariya. Daga baya, da A'ishatu ta tambaye ta dalilin kuka da dariya duka gaba ɗaya, sai ta ba ta labari. Haka kuwa aka yi!

Ran da Annabi zai cika, yana shahada, a hannun A'isha, tana karɓawa, sai ta ji kawai ya yi shiru. kamar ya shiga barci,

Ashe ƙaurar ke nan! Can, sai Sayyidina Umar ya shigo, aka ce Annabi ya rasu. Waɗansu na cewa, "A'a, Annabi bai rasu ba Annabi ba ya rasuwa!" Ta jin haka Sayyidina Umar ya ruɗe, ya zaro takobi, ya fito waje, yana cewa, "In na ƙara jin wanda ya ce Annabi ya mutu, yanzu in sare shi!" Allahu Akbar! Dubi tsananin imanin Sayyidina Umar, amma ka ga yadda rasuwar Annabi ta ruɗa shi!

### Annabi Ya Kaura

Ana cikin wannan hali, sai ga Sayyidina Abubakar, ya faɗa cikin gida, ya dubi Annabi a kwance, ya haƙiƙance ya rasu. Sai ya fito waje cikin taro. Da kyar jama'a suka buɗa masa wuri, ya tsaya, ya fara da godiya ga Allah, sa'an nan ya ce, "Ya ku mutane, wanda ya ke shi da ma Muhammadu ya ke bauta wa, to, ya sani Muhammadu kam ya mutu. Amma wanda ya ke shi da ma Sarki Allah ya ke bauta wa, to, ya sani Allah shi ne Rayayye wanda ba ya mutuwa."

Jama'a ta yi tsit. A sa'an nan Sayyidina Abubakar ya karanta aya ta 144 a cikin sura ta Ali Imrana, inda Maɗaukakin Sarki Allah ya bayyana a fili cewa Muhammadu Manzon Allah ne. Manzannin Allah kuwa da yawa sun gushe kafinsa. Saboda haka idan shi Muhammadu ya mutu, ko aka kashe shi, shi ke nan sai Musulmi su daina addinin musulunci?

A ciki dai ne Allah ya bayyana cewa jama'a su sani wanda ya juya, ya bar addinin musulunci, to, juyawarsa ba za ta cuci Ubangiji da kome ba. Ubangiji dai zai saka wa masu godiya a gare shi. Mai son jin ainihin abin da Sarki Allah ya ce, ya duba ayar.

Jin haka jama'a duk sai ta natsa. Ga ayar Allah tuni a hannunsu, ruɗewar bege ga Annabi ta sa sun manta da ita.

Allahu Akbar!

Muhammadu ya bar mu hijira ta goma,
Ya koma ga Sarkinsa Mai Kaddarawa.

Da za ya cika sai da yay yi jawabi,
Yana ta su'ali ga Mai ɗaukakawa.

Ya ce, "Ya Ilahi, ina tambaya,
Kar ka sa kabarina abin bautatawa!"

Sa'an nan ya jingina hannunta A'isha.
Yana ta shahada tana taimakawa.

A can A'isha ta ji ya bar kalami,
Ta dafa shi sannu tana girgizawa.

Tana ce da shi, "Sayyadi kar ka ƙyale,
Ka dube ni ya shugaban Annabawa !"

Muhammadu, me za ni ce ma in dace,
In ce maka tauraruwar Annabawa.

Af, ai fa tauraruwa na dushewa,
Tsaya di in ce ma watan annabawa.

Amma wata ma ya kan yi husufi,
Kwatancinka rana cikin annabawa.

Rana da kanta hazo kan rufe ta,
Kwatancin Muhammadu ya zarce kowa.

Muhammadu ku ad da yau gobe taku,
Ka dube mu ranar da ke tsawatawa.

Ka san ni gabanka, Muhammadu Na Dija,
Inai ma kirari ina taƙamawa.

A ran nan a san ni gare ka na dogara,
Mai son ka kau bai ganin taɓukewa,

Ka shaida Muhammadu mun yi shahada,
Ka shaide mu ranar da ke tambayawa.

Haƙiƙatu mun shaida Allah guda ne,
Muhammadu kai ko cikon annabawa !

### Annabi Mutum Ne !

Wannan bayani da muka yi a wannan juzu'i na uku, zaiƙara wa kowa sanin cewa Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, mutum dai ne,.sai kuma nyayyen mutane. Mashahuran littattafan Siyari, in suna ba da labarin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata

a gare shi, su kan ce shi Annabi mutum ne, matsakaici ga tsawo. Yana bayyana a gare ka, sai ka ga mashahurin kwarjinin nan, da Allah ya halicce shi da shi, ya daki zuciyarka. Ko mutum ya ƙulla wata mummunar niyya game da Annabi, suna yin arba, sai ya ga kwarjinin nan nasa ya cika masa ido, ya ji zuciyarsa ita kuma ta cika da ƙauna gare shi. Sai ya sake niyya.

A cikin manyan littattafan hadisi na larabci, Buhari da Muslimu, duk an ruwaita kalamin da wani sahabin Annabi ya yi ga bayaninsa. Ya ce, "Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, shi ne mafi kyaun duk wanda ka taɓa sani, ko ka taɓa jin labarinsa. Annabi shi ne mafi jaruntakar duk wanda ka taɓa sani ko ka taɓa jin labarinsa. Annabi shi ne mafi alherin duk wanda ka taɓa sani, ko ka taɓa jin labarinsa. In ka yi arba da Annabi, sai ka zaci kamar a bisa ga fuskarsa ne hasken rana ke hauhawa".

Idan Annabi zai buɗa baki ya yi magana, ba ya sauri. In ya faɗi abu ma, sau da dama, sai ka ji ya maimaita, don ya tabbata abin da ya ce ɗin nan ya shiga zuciyar waɗanda ya ke yi wa maganar. In Annabi yana magana, ko wace kalma tasa sai ka ji ta fito da lafazi wanda zai sanyaya maka rai, saɓanin yadda za ka ji ta a bakin sauran 'yan Adam.

Wani Sahabi, na Annabi ya ce shi ma bai taɓa ganin uwa ɗa Annabi ba, sai yana murmushi. Wannan bayani me zai hana ya zama haka ? Shi Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, da kansa ya kan ce, "Ka tarɓi ɗan'uwanka da fuska sakakkiya, yin haka shi ma sadaka ne".

Idan Annabi na tafiya, kuna bayansa, sai ku ga sai kun yi da gaske, kamar za ku riƙa sassaka, sa'an nan za ku iya ɓinsa. A cikin ko wane hali kuka gamu da Annabi, za ka gan shi a cikin halin tawali'u. Tufafinsa kamar na kowa, sai dai fa sun fi na kowa tsari da ɗahara. Wurin kwanciyarsa kuwa wata sa'a bisa ƙirgi ne. Abincin da ya ke ci kuwa kamar na kowa.

Allahu Akbar ! Kun ga watau mutanen duk da ya zauna ba wanki, -ba wanka, ba tsabta. To, ƙarya ya ke yi, in ya ce maka wai wannan shi ne tsoron Allah, ko ya ce maka wai daudan nan da ya bari Annabi ya ke kwaikwayo. Musulunci ba addini ba ne na ƙazanta. Musulunci addini ne na tsarki, sharaɗa wanki—da wanka—da aski—da ƙanshi.

Al'ada guda kuma ta Annabi Muhammadu, tsira da amin-

cin Allah su tabbata a gare shi, wadda kowa ke tunawa, ita ce wannan. Sau da yawa, aiki idan ba mabuwayi ba ne shi ya fi so ya yi abinsa da kansa. Shi ke ɗinke tufafinsa da kansa. Shi ke taryo bisashensa da kansa. Shi ke ɗinke takalmansa da kansa. Hasali ma idan aikin gida ya yi wa matansa yawa sai ya taimake su yin wadansu, watau irin su wanke ƙore.

## Annabi Yana Ba Kowa Mamaki A Duniya

Irin halin Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, abu ne wanda ya ke ba kowa mamaki a duniya. Har waɗanda ba Musulmi ba, a wadansu wurare, irin halin Annabi ya kan ba su mamaki. Akwai kafirai masu cewa su abin da ke ba su mamaki, shi ne yadda aka kasa ganin ɗigon alfahari a gare shi, sa'ad da ya yi ta samun nasarar yaƙoƙi. Suka ce lalle da sabo da son zuciya ce ya ke yaƙi, da ba shakka zuciyarsa ta ɗagauta ga nasarar da ya yi ta samu. A lokacin da Annabi ya maƙare ƙasar Larabawa duka, halinsa bai sake ba, daga yadda ya ke a sa'ad da a ke ta ba shi azaba. Hasali ma, a lokacin nasararsa, ko zaure ya shiga ya ga wadanda ya tarar a ciki, za su nuna masa wata alama ta girmamawa, fiye ga ta al'ada, sai ka ga ransa bai so ba.

Mu ƙara maimaitawa, Annabi mutum ne, wanda ya ke kula da tsabta ainun! Wanda duk ka ga ya bar tufarsa da dauɗa, ko ya bar jikinsa da dauɗa, ko ya bar gidansa da dauɗa, ko ya bar kansa da gizo, ko ya bar haƙoransa ba guga, to, kada ya ce maka yana kwaikwayon Annabi ne. A'i, haƙoran Annabi, kullum zai sa asawaki ya goge su. Ga shi da son turare. Abu duk mai dauɗa, mara ɗahara ko mai mugun wari, Annabi baya so a kusanci masallaci da shi, kada wadansu su cutu. Ka ga misali ma wanda ya ci albasa, ko ya shafa tafarnuwa, an hana su zuwa masallaci, domin warinsu ba daɗi. Hasali ma dai, a cikin Musulmi, a kam maganar ɗahara, tsarki, akwai inda aka ruwaito jawabin Annabi, da ya nuna cewa ɗahara, tsarki, watau tsabta, yanki ne na imani. Watau mutumin da ya zauna da ƙazanta ya rasa wannan yanki na imani. Jahilai su ke ce wa tsabta barikanci.

Ladabi, kunya da alheri, wadannan suna cikin jijiyoyin halayen Annabi. In har Annabi bai so jin wata magana ba da aka yi, ko bai so ganin wani abu ba da aka aikaga, to, rashin son nan naza, ga fuska sahabbansa za su iya ganewa, amma ba

dara kalmar da za ta fito bakinsa ba.

Bari ta manya ko 'yan yara ƙanana, kullum Annabi rausasawa ya ke yi a gare su. In zai yi musu magana, sai ka ji ya yi masu mai daɗi irin wadda a fuskar yaron ma za ka gane ya ji daɗinsa. In ya gamu da 'yan yara kuma a hanya, shi za ka ji ya fara gaishesu, "Salamu alaikum !" Su kuma su karɓa masa. "Alaikas salamu ya Rasulullahi !" Wanda kuwa duk Annabi ya sami labarin ba shi lafiya, to, sai ya taka tinkis tinkis ya tafi har gidansa ya gaishe shi. Ba kuwa zaɓe ya ke yi ba, da babba da yaro, da mai arziki da matalauci duk ɗaya ne a gare shi. Wanda kuma duk ya kira shi gidansa ya je ya ci abinci, zai tafi da murna.

In kuwa mutum ya baƙunci Annabi, sai da ga shi Annabi ya koma kamar bara a garę ka, kai ka koma ubangida. A wajen wannan liyafa tasa ga baƙi, ba wani bambanci ko kai ma arziki ne, ko mara arziki, ko aboki ne, ko abokin gaba. Ko ka ba da gaskiya ga Annabi, ko ba ka ba da gaskiya da shi ba, in dai ka baƙunce shi, to, duk ɗaya ne.

Matarsa Nana A'isha ta ce tun da ta ke tare da Annabi, ba ta taɓa gani ba, ko ji ya rama muguntar da aka yi masa. Abin da kawai ba shi iya ƙyalewa shi ne abin da ya soki darajar Maɗaukakin Sarki Allah. Anas, wanda ya shekara kamar goma yana yi wa Annabi hidima, ya ce tun da shi ke bai taɓa jin zagi ya fito bakin Annabi ba.

Ban da wannan kuma, al'amari duk na son jiki, Annabi ba ya tare da shi. Akwai lokacin da zai hau doki, ko raƙumi, ya yi sukuwa, don ya motsa jikinsa. Hasali dai, har a cikin hadisi, akwai wanda ya ruwaito wani jawabi na Abu Jahali game da Annabi. Kowa kuwa a cikinku, wanda ya karanta wannan littafi da na bayansa, ya ga an sa ɗam misali, na irin ƙiyayyar da Abu Jahali ke gwada wa ga Annabi. To, har shi da kansa Abu Jahali wata rana ya ce wa Annabi, "Ya Muhammadu, mu fa ka sani ba kai ba mu ke ƙaryatawa, a'a, abin da ka kawo shi muka ƙaryata." Ka ji wannan, wai fa ita ce shaidar babban maƙiyi. Muhammadu Aminu, Muhammadu mai gaskiya da riƙon amana !

Ya Allah ka daɗa tsira ga shugabammu Muhammadu, mabuɗin abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya sa gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici.

NNPC